[10/14, 20:00] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*Intelligent Writer's Asso.*

*DEDICATED TO: My Mommah Hajja Hadiza muhammed Ba"are I so much luv u my mommah*

*Wannan littafin ba Sabon Novel bane Tsohon Novel dina ne na Dawo dashi,saboda zan sake gyarashi,na fadadashi domin masoyana wadanda basu karanta ba Dama wadanda suka karanta...Ina godiya sosai domin kun nuna min One love💝kuna ma kan nunamin SON SO FISABILILLAH..*

*Typing 1 january 2019*

*Chapter 1*

*Kaduna*

⭐Da gudu wata mota 320 kirar toyota,ta shiga cikin wani private hospital mai suna *S&S SAFANA SPECIALIST HOSPITAL*

Cikin Hanzari matar tabude motar tafito tayi cikin asibitin da gudu tana fadin"ku taimakamin kada y'ata ta mutu ku taimaka min.." Nurses suka biyota aguje da gadon daukan marasa lafiya,wata matashiyar budurwa ce aka fito da ita daga cikin motan tareda wata dattijuwan mata,tsirtsetsen cikin keta wutsul wutsul alamar yana gab da Fitowa Ihu take zabgawa iya karfinta tareda wasu maganganu marasa ma'ana Da Hanzari suka gungurata sai labour room,Hajiya karima takalli Momma tace"To ai sai kira d'anki shafaffe da mai ya taho ya girbi abunda ya shuka" tafada dawani irin izgilanci,Momma tayi murmishi irin nata kan tace"Ayyah Hajiya zai zo ba"a gabanki namai waya ba kan mufito,insha yanxu zai zo kila wani abun ne ya tsaidashi"Tafada tana duban Hajiyar yamutsa fuska tayi zatayi magana kenan Kamshin turaren azzaro visit yafara musu maraba ko ba'a fada musu ba sunsan mamallakin kamshin.

Momma takara fadada fara'arta daidai lokacin da suka kariso maza biyu ne cikin shigar suit Black and ash,rigar likitancine saye acikin su,Daya daga cikinsu ya Karisa yana Fadin"Momma

Har kun iso?

Cikin fara"a tace"mun iso Babana kashiga sun shiga da ita ciki"mtswssss tsakin daya katsesu kenan suka juya atare suna kallon Hajiya kari datake zabgamusu Harara,tace cikin kallon raini"Kaga mallam ba mgana zaka tsaya yi ba yata nakeson nasan Halin data ke cike,tundazu anshiga da ita bawani labari"Tsam dukkansu sukayi da rai kafin momma tayi karfin halin zame Hannunta tana Fadin"Babana Hanzarta kashiga ga Halin da *SAKINATU* take ciki.

cikin takaici da bakin ciki ya juyo wow!! abunda na Furta kenan dogon bufullatani mai cikar zati da kamala,yanada tsawon da dan kibam murjewa,dogon Hanci ya mallaka tareda madaidaitan dan bakinsa pick kamar yana shafa janbaki idanunsa,bakin gashin kansa yakwanta ye luf dashi,zagayayyen sajensa yakaramasa kwarjini Fari ne tas mai jaja din nan abun burgewa goshinsa dauke da tabon salla wanda yake kara masa kima a idon mutane,wani siririn gilashine mai karama Fuskarsa kyau sanye a idanunsa,kallo daya zakamai ka fahimci tsayayyan Namiji ne mai cikar zati da Haiba

*DR SAFWAN SALE SAFANA* kenan likitan daya kware gurin kula daduk abunda yashafi mata wato gynea Doctor wanda ke tare dashi *DR TAHIR* ne  Abokine kuma Amini garesa kuma abokin aikinsa dasuke aiki akarkashin asibitin shi Dr safwan din.

Sai da ya isa kusa da ita yadan ramkwafa yace cikin dakakkiyar murya"Barka da zuwa Haji......."

"wai shi na tambayeka"ta katseshi "yata nake bukatar jin Halin datake ciki anshiga da ita tundazu naji shuru'"

takareshe fada tana wani jijjiga kamar wata yar daba,yadade tsugunne kafin yamike cikin sanyin jiki,ya Nufi kofar labour room din yasa Hannu a handle din kenan Wata murya cikin karaji da azaba yaji tana fadin

"Allah ya isa tsakani na dakai safwan,kayi min ciki kabarni da wahala,kacemin Haihuwa babu wuya...Gashi....Gashi kabarni da wahala  kai babu abunda kasani sai ci🙈kamar tuwo wlh bazan sake yadda dakai ba" cikin bakin ciki da Nadama yasaki Hannun kofar ya juya ya Fara Tafiya duk suka bishi da kallo Hajiya kari tace cikin daga murya"Kai safwan ina zaka ko bakajin ihun da sakina takeyi ne....".Ina ko waiwayowa baiyiba saima kara sauri dayayi har yabace daga gurin.

Cikin Takaici Hajiya kari tadaga Hannu sama tana Fadin"wayyo ni karima nashga uku"kan ta isa kusa Da momma tana Fadin"ke wata irin uwace kinaganin wulakancin da d'anki yayi ma y'ata ammh kin gagara mai magana,saboda yagama cin moriyar ganga ya dirkamata ciki ko"?

Takareshe Fada Tana zaremata ido,Momma tayi mirimishi daya zaman mata jiki kam tayi magana Dr Tahir yarigata dacewa"Am....Hajiya kiyi Hakuri i promise u sakina Zata Haihu lafy"yana gama fadar  haka ya bude Kofar Labour Room din ya Shiga.

Dakyar Dr safwan ya karisa office dinshi cikin kunan rai,toilet yafada yasakarma kansa shower ko kayan jikinsa bai cireba Haka ruwan keta kwararamai yafi minti talati ahaka so yake yarage radadin dake addabansa,Haka ya Fito ruwa na diga ta ko'ina ajikinsa kan kujrerar dake office din yafada yana maida Numfashi.

Har abada baisan yaushe zai zama mutum a idanun sakina da mahaifiyarta ba,baisan yaushe sakina da Mahaifiyarta zasu daina cimai mutumci  ba shida mahaifiyarsa ba,baisan sai yaushene zata darajasa ta kallesa amtsayin miji ba bai sani ba,bai sani ba,yafada da karfi idanuwansa sun canza launi.

Yafi minti Hudu acikin wannan yanayin kafin ya sake Bude idanuwansa,gabadaya Zuciyarsa ta gama cika da wani kunci kansa na sarawa lokaci daya jijiyoyin kansa suka Dago,kansa ya Dafe lokaci daya yana Share Ruwan Dake Diga daga saman kansa,kafin ya sake komawa ya jingina da jikin kujeran yana maida Numfashi a jere kamar wanda yayi gudun tsere.

Runte idanunsa yayi yana ajiyar zuciya Lokaci daya yana Saukar Da Numfashi Daga ganin yadda yake yi zaka fahimci yanayin Dayake ciki na bacin rai da dacin Zuciya,idanuwansa ya bude yana bin Kofar shigowa da kallo lokaci Daya Abubuwan da suka Faru abaya suka fara dawowamai daki daki kamar alokacin Abun ke Faruwa tamkar yana kallo cikin magijin talabijin.

*Domin samun kasancewa cikin masu karanta Sanyaya biyu na Mr Bello da Matar Naseer kan 350 duka biyun Single 1 kuma 200 vips kuma 400 ne Duka biyu kuma 600 ne Muna maraba daku masoyanmu Sai kunzo*

Commets,share,like and vote....

*Anitha..*
[10/14, 20:00] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO:My mommah Hajja Hadiza muhammed Ba"are*

*02*

*SHEKARUN BAYA*

" *DR SALE HABULE SAFANA* shine cikakken sunan Mahaifin Dr Safwan wanda d'ane ga marigayi Justice Habule safana kafin Allah yamai Rasuwa,yayi gwagwarmaya agwannati har kawo mutuwarsa

Dr sale habule safana Haifaffan garin safana ne dake jihar katsina,yana da shekara bakwai aduniya Allah yadauki ran mahaifinsa,Mahaifiyarsa Hajiya Maryam wacce suke kirada Hajiya mama ita tadinga kula da danta har yagirma,Yayi sakandiri sch dinsa a barewa college dake zaria anan kuma yahadu da Aminsa kabir kankia ganin sun fito daga jaha daya yasanya abotarsu tafi tafiya daidai.

Bayan sun kamallah makaranta suka Fada ABU ZARIA a inda Sale ke karantan medicine shikuma kabir political science,ammh duk da haka suna Haduwa in basuda lectures,Haka rayuwa tacigada da tafiya Har kabir ya kammala digirin dinsa ya dora masters dinshi shikuma alokacin sale yatafi Bautar kasa.

Sale a garin adamawa yatafi bautar kasa kuma achan Allah yahadasa da mahaifiyar Safwan Hadiza,Hadiza mahaifaffiyar Adamawa ce bafullatanan asali, marainiya bata uwa ba uba sai kanin mahaifinta wanda yariketa mai suna Baffa Sani Hadiz bata zurfafa lilimi ba iyakarta sakandiri ammh masaniya littafan Addinin muslunci tana da ilimi fiye da tunanin mai karatu bai kammala bautar kasa ba Allah ya kulla aurensu tareda jajircewan Hajiya mama.

Lokacin da'akayi bikin kabir kankia na kasar spain yaje yin phd dinsa,sai da yadawo yaji amininsa yayi aure hakika ya tayasa murna kwarai matuka samun mace irin Hadiza,Macece kyakyawa dogowa mai dogon Hanci da gashi,Bayan kammala bautar kasarsa yafara aiki da Aminu kano,Yaso ya dauki iyalansa sukoma kano da zama Hajiya mama taki amincewa dole yasa yabarsu nan safana yana zuwa musu weeked

Bayan kammala karatun kabir kankia yafada siyasa kadangadan akuma lokacin iyayensa suka masa aure da yar uwarsa Karimatu,karimatu tun tana karimar shegiyar makirace,gata bawani kyau ba bakace mummuna ga gajarta,tun tana yarinyanta take bala'in son auren mai kudi bata shiri da takala,gata da kyashi da hassada ga bariki kala kala dan dai babu yadda zai yine yasa yahakura ya amshi karima.

Yafara rike mukamin sakataren gwannatin janar katsina akuma lokacin Hadiza ta haifi Safwan Hakika tunganin Farko da karima tama Hadiza taji ta tsaneta saboda tafita kyau uwa uba hankali Natsuwa da tarbiya kai akomai tadarata shiyasa lokaci guda kyashi ya shigeta,batawani sakarmata sai kiga tawani yamutse yamutse kamar taga kashi shiyasa Hajiya mama ganin Farko tace"Kabiru ina karoro wannnan ruwan yan Duniyan"kai tsaye agabanta mirmishi kawai yayi itakuma karima tadago tana karema Hajiya kallo ta kasan ido.

safwan yazo cikin gata,badewa mahaifinsa ya tafi london karo karatu sai da ya shekara uku kana yadawo lokacin yazama consultand,Safwan nada shekara biyar iyayensa suka kaisa Nigeria turkish.tunda Hadiza ta haifi safwan bata kara Haihuwa.

Haka dai Rayuwan ta cigada juyawa cikin nasara da kwanciyar Hankali lokacin da Safwan ya kammala secondry sch dinsa lokacin Da Allah ya karbi ran Mahafinsa hatsari yayi ahanyarsa tadawowa daga kano hakika matuwar Dr sale Habu safasa ta girgiza yan'uwa da abokan arzika,Alhaji kabir yaji mutuwar Amininsa matuka sai dai Hakuri

Hajiya da Hadiza wacce Safwan kekira da Momma suka dau dangana suka maida Hankalinsu wurin kula da safwan,Lafawar abun yasa yadage kasar malesia zuwa karatun medicine sai da ya shafe shekara sha kana yadawo lokacin yazama cikakken likitan mata.

Shima din da Aminun kanon ya fara aikin kan chukun chukun bude asibitinsa ya kammala da taimakon Dady Alhaji Kabir kanki wanda yake matsayin kwashinan ilimi ta jahar katsina.

Koda bude asibitin ya kammala baida na aiki da Aminu kano ba Saida ya tattaro Su Hajiya suka dawo garin kaduna kana ya maida Hankalinsa kan asibintinsa,Dr tahir Aminsane wanda suka Hadu a malesia course daya suka karanta,kuma yan kasa daya shiyasa abotarsu tayi karfo Shiyasa bayan ya kammala asibitin ya Nemosa don Atafi tare

Alhaji kabir bai yada iyalan Dr sale ba yana kokarin ziyartarsu in yasamu dama,duk abunda suke bukatu tunkan suyi mgana yake kawo musu Hakika shi mutumin kirkine sai dai Karima tanajin bakincikin abunda yake musu dan dai bayya zatayi duk da yanxu ta mallakeshi sai abunda tace yakeyi

*WACECE SAKINATU*

SAKINAT KABIR KANKIA shine cikakken sunanta yace ga kwamishina Alhaji Kabir kankia da Hajiya karima wacce ake kira Hajiya kari,yayansu hudu salmace babba tana aure a portharcort wani controller ne sai laila dake auren wani dan kasuwa a kano,sai Sakina daga ita sai Ummi.

Gabadaya ya"yan Hajiya kari laila da sakina,sune suka dauko halayyanta wanda ma harsun gyasheta Salma ce da Ummi kadai suka fita dabam,dukkansu suna da degree sakina business admistration takaranta Tana son taga tazama yar kasuwa tana juya kudi ahannunta shiyasa tana dawo daga london bayan ta kammala masters dinta Mahaifinta ya tallafamata,tafara odar kaya daga dubai zuwa Nigeria irinsu dogayen riguna da takalma da jaka,kayan maza kai duk abunda yadanganci sawa da kwalliya,cikin lokaci Allah yasa abun albarka cikin shekara biyu sakina ta bunkasa tayi kudi tuni takeda dankara dankara shaguna a kano,kaduna,katsina,zamfara,da gombe,Sakina boutique and costimetics,sakinat shoes,etc.

Gabadaya Hajiy Kari bata kula da tarbiyan yaran ba kwamishina baya zama so komai na Hannunta,shiyasa sakina tataso tun tana karama bata kunya ga raina na gaba da ita bata da kunya ko kadan bata iya girmama nagabada da ita ba.

Sakina bawata kyakyawa bace ta azo agani bakace gajera ammh saboda shafen nan na yaran zamani yasa takoma Fara,Wani gajeran hanci gareta tana da dan tudun baki,kan nan kamar Hammatar dan iska kullum cikin gashin doki take,tanason mu'amala da abun mai kyau duk da ita din bamai kyau bace,Sakina bata kaunar talaka ko kadan shiyasa danginsu na kanki kowa yasanta da rainin arziki shiyasa kaf suka fita harkansu sboda Hajiya kari inrin matan nan ne masu kyashi arziki daga ita sai mjinta da yayanta.

Sakina yar gayuce ta karshe kullum cikin shigar alfarma zaka ganta,to tazo kaduna duba shop dinta taji zazzabi ya rufeta tana Hanya shine tafada asibitin Dr safwan ganin farko tamai yasace zuciyarta wanda dagashi har ita basusan juna ba saboda kowa ba kasar nan yayi karatunsa ba,Ada ta dauka wasane sai da takoma gida kana ta tabbatar da takamu da son Dr safwan,tayi kokarin tayakiceshi ammh hakan ya faskara,abinciken da'aka matane tagano dane gun Aminin Abbanta.

Da tama hajiya kari magnar kin bada goyan baya acewarta baida qualities din auren yarta,ammh sakinat taki hakura,taci gaba da shisshigemai da kissa da kisisina,Da hajiya taga yarta taki hakura yasa tashiga tafita har soyayyah mai zafi ta kullu atsakaninsu,Lokacin da kwamishina yaji labari yayi matukar farinciki dasamun suriki irin Dr safwan,kuma yakara zumunci tsakaninsa da amininsa duk da baya raye.

Da Hajiya mama taji Ibr tadaga tsalle tace bata yarda ba saboda sanin mugun halin Hajiya kari ammh Dr safwan ya tubure dole tasa ta amince ita daman momma batada matsala cikin lokaci kankanin komai ya kammallah Amarya tatare a gidanshi dake kaduna,mai dauke da shashi biyu daya na momma da Hajiya daya shine mallakin sakina

Sunkwashi amarci na tsawon wata guda kafin halayyan,Sakina sufara bayyana.

Commet
And
Share
[10/14, 20:00] Sis Janafty: Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/HYISeJb3pcr33n3fhabu5h

*NA TAFKA KUSKURE...!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*03*

------Hallaya ta farko data fara bayyana shine kazanta da lalaci,kafin Hajiyarta tasamo mata masu aiki Sai dai shi Safwan inyagaji da ganin kazanta ranar karshen mako yazage ya tsaftace gidan tun yana mgana har ya zuramata ido.

Girki kuwa baida darajar da sakina zata girkamai abinci to tama iyane banda indomie bata iya dafa komai ba,kullum sai dai masu aiki su jagwagwala su ijeye sai da kullum yana aikin rab'awa sashin Mommah yanacin abinci, gashi batason zaman gidan kullum tana Hanyar katsina ko kano,Ko yamata mgana baji takeyi ba shiyasa ya zuramata ido.

Raininta har Mommah bata kyaleka ba yimata take dayake Mommah macece mai Hakuri da kawaichi Mommah irin matannan ne masu mugun Hakuri ko zagin ta kayi sai dai tama mirmishi,ashekaru bata wuce48 ba,shiyasa sakina tayi bala'in rainata tadinga daka mata tsawa,Hajiya mama ce take shakka domin itace big problem dinta agidan Safwan.

...Hajiya mama Dattijuwa ce yar kimanin shekara saba"in aduniya,Bata daukan raini ko kadan irin tsofaffun nan ne wanda komai ke ransu gameda kai saisun fada maka sai dai kamutu tanada faran faran da jama'a dason mutane tun tana safana macece takowa makotanta kuwa kamar yan'uwanta Haka ta daukesu,tanada fada in aka tabota gata wani lokacin da ashisshigi

koba"ayi da"ita ba,saita tsoma kanta,shiyasa Sakina ta tsaneta saboda tana mata katsalandan a al"amarinta game da Mijinta Safwan.

Wani lokacin Hajiya ke tarema mommah tacima sakinar mutumci intaga tana mata Rashin kunya,inkuwa dukkansu suka bata haushi tasharesu saboda Takaichin yadda Mommah ke zama Sakina namata yadda Taga dama kuma tana matar Danta ,Safwan yarasa yadda zaiyi da sakina daya tashi daukan mataki mommah tahanasa.

Ranshi bai kara baci da Sakina ba saida tayi Rashin lafiya tafara, zubar jinin,Dubar farko ya fahimci taje anrufemata bakin mahaifa dayake Allah ba'a mai dabara sai ga ciki ya bulla agefen mahaifan bai mata mgana ba, sai da yayimata operation yamaida cikin,cikin mahaifa ya sallamota suka koma gida,Sakina taga bacin ran Safwan wanda bata taba gani ba mgana har kunnin kwamishina shima yacimata mutumci ba'a son ran sakina ba tacigaba da renon cikin jikinta domin ita atsarinta babu Haihuwa Allah shi kyauta,Shawaran Hajiyarta da laila ne sunfada mata karta yarda yamaida ita akuya tadinga zazzagamai ya"ya karshen tadurkushe ta zama Tsohuwa shikuma ya auro wata.

SAFWAN yaci sunan mahaifin momma ne shiyasa bata iya fadar sunansa sai dai da babana, Mutum ne mai Hakuri saboda Nonon Momma ya tsotsa,shekararsa ta haihuwa 30 yanada kawaichi da dattako mutum ne mai Nagarta kallo daya zakamai kakirasa ustaz ammh social ne yana da zurfafan bincike a bangaren ilimin addini duk da matsayinsa na likita yahaddacce Qur'ani tun yana shekara sha hudu aduniya saboda jajircewan mommah agaresa, da sauran littafai irinsu,muwadda malik,sahihul bukhari,iziya,sira,fiqhu,dadai sauransu,yana da tsantsane da addinsa matuka mutum ne mai yalwar fara"a,yana bala"in kaunar mommansa saboda itace ginshikinsa da kakarsa Hajiya mama.

Abangaren kaya yafison manyan kaya atsarinsa yafison yasanya shadda gezner da yadi mai stantsi ammh saboda yanayin aikinsa yasanya yake surkawa da suite ammh duk Ranar jumma"a kowa yasani shigar manyan kayan ne atsararinsa.Yana da zuciya da fushi wanda yakan dade kafin yayi irinsa fushin kuma in yayi fushi da abu na har abada yakeyi,bangaren abinci yafison abincin gargajiya,irinsu dambu,fate,fankasau,tuwo miya kubewa da dai sauransu.

Aurensa da sakina babu abunda yakaru dashi sai ci baya tunbayan aurensu matsaloli suka dunga kunno kai saboda sanyinsa yasa ta rainasa bai isa yamata mgana taji ba shikuma baisan hayaniya da kwakwazo dat why yake yakyaleta uwa uba yana ganin mutumci mahaifinta,A yan"uwanta kaf bamai darajashi sai salma da ummi Hajiya kuwa da laila dama sune aminan sakina duk abunda sukace shi takeyi,ko bangaren auratayyah bazai iya dora komai ba domin sai inyarasa yadda zaiyi ne yake neman sakina,saboda baya samun gamsuwa bata iya komai na fanni bama miji kulawa ba,gashi bata rabo dama kanta pixsing kullum suka gama saduwa da juna sai yakoma yana jinyar kansa saboda tsabar yakusan dayake sha,ita bata damu danashi bukatan ba nata kawai tadamu dashi tayimai sharf kamar kayan wanki yaci yatashi bawani salo

balle kukan kissa,ita ba abunda tasani sai ci ta kwanta sai gayun kawai awaje ammh aciki sai takaichi.

Ko Rainan cikin sai abunda yagani sai yayi sati bai nemata ba ammh duk ranar daya nemata bada son ranta ba sai yakusa kuka saboda takaichi itadai sakina ba abunda tasani sai harkan kasuwanci ko dan kayan gyaran jiki bata damu data sha ba dan tagyara kanta ba a"a ita abunda tasama gaba shine agabanta,shiyasa bai rabo da azumin litini da alhamis Domin kare kansa daga halaka.

Kullum ta kalli cikin jikinta sai ta zageshi aranta,Haka tacigaba da renon cikin,cikin bakinciki da danasani saboda mahaifinta yace wlh yaji Ibrin wani abu yasamun ciki kashinta ya bushe,ga bakincikin tadaina fita ko'ina tunda cikin ya tsufa,kullum cikin zuwa Hajiya take tana duba yarta acewarta,babu mai kula da ita,gashi ta ranma mommah saboda sunganta bamai karamniya bace.

Ranar da Sakina tafara naguda tun Safe Dr safwan yatafi asibiti,kuma da safe ya bartaa tana barci,itakuwa Hajiya daman sunyi waya,da ita tafadamata batajin dadin jikinta shiyasa tun safe,tasa dereba ya daukota suka kamo  Hanya koda ta iso ta iske sakina tafara jigata,shiyasa da Hanzari tafito da ita zasu wuce asibiti,Itakuma momma tafito tazo taduba sakinar sai taci karo dasu,cikin azama ta isa tana tambayan lafiya"harara kawai Hajiya kari ke zabgama mommah takasa bata amsa,da sauri Momma tace Hajiya bari  in dauko mayafi insanar da hajiya muje"Ko kallonta batayi ba koda ta isa,shashensu ta iske Hajiya mamq cikin daki take fada mata"Tabe baki hajiya tayi kan tace"Allah raba Ify nikin gama barci nakeji in kinfita kirufemin kofar"

daga haka tashige ta barta nan mommah takira Dr safwan take fadamai gasunan zuwa da sakina zata Haihu,yashiga rudu yace su hanzarta,Koda tafito Hajiya na kokarin sanyata cikin mota tataimakamata suka sanya suka nufi asibitin tanaji Hajiya kari takira yarta laila tanafadamata abunda ke faruwa tana zagin Mommah din da danta wai sun bar Sakina agida zata mutu sai da ita tazo Daga katsina,mommah kuwa sai dai kawai tayi mirmishi ta kauda kai.

Shine dalilin kawota asibitin da abunda yafaru.

WANNAN KENAN

Commet
And
Share
Vote.
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*04*

-----Tura kofar office din akayi tareda shigowa,Dr tahir ya kariso yana mai karewa Dr safwan kallo wanda ke kwance ruwa nadiga ajikinsa duk ya jika kujera kwaya dayan datake cikin katob office din,cikin azama Dr Tahir ya isa garesa yana Fadin"Dr Safana wht wrong with u"?

yafada yana mai dafasa,ajiyar zuciya Dr safwan ya sauke yana mai sauke gwaron numfashi bayan tsawon lokacin daya dauka yana tuna iya tsawon lokacin daya dauka yana kunsan bakincikin sakina da uwarta.

Ya dago idanunsa jajir kamar garwashi yana bin Dr Tahir da kallo,kallo daya Dr Tahir yama safwan yaji mugun tsausayinsa ya tsirgamasa hannu yasanya yana jijjiga kafadarsa yana fadin"Dr Safwan Dan Allah Dan Annabi kayi.....!"

"Nagaji Nagaji Tahir wlh Nagaji"ya katsesa cikin kunar rai da kosawa"koda yaushe kaida momma kalmarku daya inyi hakuri shin bakuda wani abunda zaku iya gayamin sai kalmar Hakuri eye"?

yafada yanawani zaremai ido idanunsa sun tara kwallah,cikin sanyin jiki Tahir ya karisa kusa dashi yana riko hannunsa,yana fadin"Babu...Babu safwan babu wata kalma data dace dakai bayan Hakuri,nasanka kacigabada da hakurin daka saba Allah nasane dakai"shuru Dr safwan yamai yana kallonsa kamar yana karantan wani abu atareda shi,kara damke hannunsa yayi yana jijjigawa alamar lallashi cikin kasala ya zare hannunsa ya isa ga wata durowa dake cikin

office din akafe ya bude sai ga wasu jeren kayan sun bayyana kai tsaye ya ciro su yakama Hanyan toilet Dr Tahir yayi zuru yana kallonsa sai dayaga yana shirin shiga toilet don kana yace

"ta sauka lafiya an sami DR SALE SAFWAN SAFANA  Da sauri ya juyo yana kallonsa kan mirmishi ya subuce masa zaiyi mgana kenan Dr Tahir ya rigasa dacewa"Both momma and bby are in good Health yanzu ma zan basu sallama su koma gida" gyada kai yayi kafin yace"thanks so much Dr....."!

"Zan maidasu gida"Abunda tahir ya katsesa dacewa kenan kafin yafice mirmishi kawai Dr safwan yayi kafin ya girgiza kai yafada toilet.

***

Dr Tahir ya tura kai Dakin da"a ka kawo sakina bayan angyarata,ita da bbyn nata,Momma ta amsa sallaman tana Fadin"Attahiru sannu da kokari "

"Yauwa mommanmu Barkanmu fa"Yafada shima yana mirmishi karisawa yayi yana mai kara kallon babyn wanda kamar Dr yayi kaki,momma tadago tana Fadin"kaga danku ko,kungirma yanZu inashi baban nawa yazo yaga dansa mana"Tahir yace zaizo yanzu momma bari nadubata in babu matsala inmai daku gida"

Momma tace"Alhamdulillah..."Gurin sakina ya karisa wacce ka zaune kan gado tana shan ruwan shayi yayinda Hajiya kari ke gefenta tana faman buge bugen waya"cikin mirmishi yace"Sannu madam munfa gode"Kallon raini ta watsama Tahir kan tace"Dole kace kungode kun hadani da aiki kun gudu"Yasan da wanda take shiyasa yace mata"is ur duty ai madam kema kinsani Haihuwa na matane ba maza ba kuma meye ribar auren soyayyah,A Haifi ya'yan soyayyah"yakareshe  Fada yana dariya kasa kasa tunda yafara mgana Hajiya kari dake waya take zafgmai Harara yana kallonta ta kasan ido aransa yace'oho dai bazan dakuba dai" kasa bashi amsa sakina tayi saboda tasan waye Tahir gurin maida magana kamar dan Hausa bakwai.

..Ya rubuta mata maganin karin jini kafin yabata sallama saboda ta haihu lafy ko kari ba'a mata tana haihuwa kaji kwakwazo tsit tamike ras kamar ba ita ba yana tsokananta yasan ya kunnota shiyasa yaketa dariya,ita kuwa Hajiya kari jitake kamar ta shakeshi yacika iyayi ga tsinannan tadi kamar wani aku,momma tana ta zunduma ma Tahir Albarka har suka fito,har mota yarakasu momma dai ita ke rike da jikanta,har sunshiga mota Hajiya kari ta lego tace"Shi wanchan fa koda dan shege aka Haifa mai ai yazo yaganshi balle dan Sunnah ne kuma shi yadigasa"Tafada kanta tsaye Dr Tahir yagyara tsayuwa sanin matan bata da kunya ko kadan yasa kai tsaye yace mata"Wlh aikine yarikesa ammh kema kinsa bakasha wahalar diga abu da kanka ba,kuma ka banzarta dashi ba"Yafada yana kallonta ido cikin ido kasa bashi amsa tayi har dereba yajasu suka bar asibitin yana kallon motan yana killer smile kafin yace'kunyan mara

kunya asara.

***

Hajiya mama dake zaune a farfajiyar flat dinsu tana tsinkan zogalanta datazo dashi daga safana radio tane agefenta takure kara tana jin gidan radion freedom ansa wakar sangaya ta daddage, tana bin abinta Mallam Ilaya mai bawa fulawa ruwane agidan,shine aikinsa shike zaune kusa da Hajiya tana zubamai labarin zamanta a safana sukaji hon din motan Mallan Habu mai gadi yayi gaggawan zuwa ya wangale get motar tasu tasawo kai zuwa parking space Momma ce tafara fitowa rike da baby a hannunta kafin Hajiya da sakina wacce tafito tana wani hura hanci kamar wata sakarya,Hajiya mama tai galala tana kallonsu Tunda Hajiya kari tafito taga Hajiya mama tawani hade rai,momma cikin farinciki ta nufi Hajiya mama tana fadin"Hajiya kiyi barka kinyi sabon maigida"Tsuramata ido Hajiya tayi tana kallonta sama da kasa kafin tace"Au....Wai tasauka ne na"aza bazata iya Haihuwa da kanta ba?

tafada tana bin sakinar dawani kallon raini jikin Momma yayi sanyi kafin tayi mgana Hajiya mama taci gaba da cewa" 'au ke kika koma mai renon kuma saboda sunmaidake wata sha katafi ko"?

tafada ranta abace Momma tadago zatayi magana taga mallam iliyasu ya tsuramusu ido da sauri tace"Mallam ilaya kunyi d'a fa "yana washe baki yazo ya amasheshi yana sa masa albarka shima mallam Habu yakariso yana sa albarka.

Hajiya mama tamike tawuce tana fadin"bari naje naji ubanwa zai mata renon dan.."tana fada tawuce fuu sashen sakina wacce tun fitowarsu suka shige ciki,koda ta isa basu afalo cikin bedroom ta samesu sakina kwance share share Akan gado Hajiya kari nagefen suna mgana Hajiya mama tafado dakin,sororo suke binta da kallon Hajiya kari tayi karfin halin cewa"Haba hajiya da girmanki kina shigowa guri babu sallama"tafada tawani cin mgani Hajiya mama ta kallesu a wulakance kan tace"Ana sallama inda akasan darajan sallamane ba inda ba'asan darajarta ba"Cikin kunan rai sakina tace"gaskiya hajiya wlh kija girmanki,kan mene gaskia kija girmanki tunkan na tunkudesa"takareshe fada da rashin kunya Hajiya mama tace"Kin ma uwarki bani ba wlh da ita kikeyi don banace kinma ubanki ba don Kabiru yaron arziki ne,  nikam nafi karfinki fitsararriya kawai,kuma wlh kinemi mai miki reno hadizar baiwar  uwarkice  dazaki barmata rikon jika tareni d'a kuma ta reni jika bazai yuyuba tunda kika iya bin miji kikai ciki to kin ko san yadda ake reno"Tana gama fadar haka ta buga musu tsaki tafice.

Hajiya kari takalli sakinar tana fadin"wai wannan tsohuwar anya kanta daya"Sakina tace"lafiyarta kalau  Hajiya tsabar iskanci ne wlh,kuma shi safwan  din ke dauremata gindi"Cikin takaichi Hajiya kari tace"shegiyar tsohuwa mai shisshigin bala'i"Sakina ta karbe da cewa"ta karshe wlh Hajiya tshohuwarnan tana shigan hanci wlh"Tafada tana bayyana takaichinta.

Hajiya tace"barta mugama da jikanta tukunnah ita karamar alhakice.

Koda Hajiya takoma ta iske momma na tsaye tana jiranta kallonta tayi tana rumgume da baby kan tace"sai ki wuce ki kaimusu dan'su saura kizauna kina musu bauta tunda nasan ki zuciyarki kamar ruwan sanyi take"tana fadar haka ta tattara shimfidanta ta shige ciki,koda momma takai shi itace tamasa wanka tasama sakina nata,ko wankanma saboda lalacewa dakanta tashiga hajiya na kallonta ko ajikinta momma taga abun mamaki ammh sanin halinsu yasa taja bakinta ta tsuke.

*Anitha..*

.Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO: My Mommah Hajja Hadiza Muhammed Ba"are*

*05*

-----Karfe goma da wani abu Safwan yabaro asibitin sa dake anguwan rimi kaduna daura da iyali hospital kai tsaye anguwan sarki yana nufa cikin motarsa kirar benz baka,cikin slow yake

tafe har ya kariso get din gidan nasa hon ya Zuba da hanzari mallam habu ya wangalemasa get yana masa barka da dawowa tareda masa barkan karuwan da'aka samu.

Kai tsaye part din momma yadosa cikin takun isa sanye cikin suit masu ruwan toka rigar likitancinsa sabe a kafadarsa wayarsa ke rike ahannunsa daya kuma yana sanye cikin aljihu,da sallama yashiga falon momma kadaice,afalon zaune kan darduma alamar sallah tagama tana lazimi cikin fara'a ta amsa sallanma tana cigaba da laziminta takalminsa sawu ciki na fatar damusa ya cire kafin ya kariso gabanta ya zauna yana fadin"Momma......"Tadago tana kallonsa cikin Annuri da farinciki,kansa yadora kan cinyanta data tankwashe yagyara kwanciyarsa,itakuma tasanya hannu tana shafa kansa lumshe ido yahau yi yanajin wani farinciki na ratsashi cikin kasala da gajiya yace"momma...Yunwa nakeji"mirmishi tayi kan tashafa addu"an shima yashafa yana fadin "Allah ya karba mommanmu"Allah ya maka albarka babana yajagoranci lamarinka yasama zuru"arka albarka"Atare suka Amsa gabadayansu da Amin harda hajiya mama data fito daga daki tana kallonsu.

Kichen tashiga tadaukomasa dambun zogalan datayimai saboda tasani masoyinshine,ruwa ta hadomai dashi sai furan data damamai don shinema basa rabo da furar'gabansa ta ijeyi tana fadin"kin cikasa da tadi....Maza ci abinci sufiyanu nasan kana jin yunwa"Mikewa yayi yana fadin"kai i so much luvs u Hajiyata kinaji dani"yafada yanajan kulan gabansa fara'arsa takarune dayaci karo da abunda ke ciki yadago cikin Annuri yana kallon momma da Hajiya dasuke kallonsa cike da so da kauna yana fadin"thanks so much hajiyata Allah biyaki da Aljannah"Amin...SufiyanuAllah yayi maka albarka"bata rai yayi yace"kinga hajiya wlh zamu bata basunana sufiyanu ba am Safwan sale safana by name"

Hajiya tace"kai kasan wani Safawa, nibansanshi ba sufiyanu nasani Ato"Tafada  harda da jaddawa kara bata rai yayi yamata banza yayi bismillah yafara cin abincinsa,har ya kammala bai sake mgana ba sai daya wanke hannunwansa kana yamike zai kwashe kwanukan momma tayi saurin amsa tana fadin"A'a barshi babana,kaje kahuta kuma kaga masu jego da safe ma hadu"Tafada tana amsa farantin ajiyar zuciyar ya sauke yana juyawa yace"Sai Allah ya kaimu momma"ta amsa da"Allah ya tashemu lafy"Hajiya tamike tayi hanyar dakinta tana fadin"muda ba'a son mukwana lafiyan sai mun tashi da izinin Allah ehe"tafada harda buga kafa dariya takusa subucema momma da Safwan sukayi saurin shanyewa saboda sunsan Halin Hajiya yanzunan takara harzuka.

Mirmishi kwance afuskar sa ya isa part dinsu koda ya shiga falon yadau shuru ga wata katuwar plasma tana yi ita kadai,kashewa Yayi kafin ya nufa bedroom din daya zama mallakinsa kan

doruwar gadon ya ijeye wayoyinsa guda biyu kirar i phone8+ da lapcoat dinsa ya fada toile wanka yayi kafin ya dauro alwala,daure da tawul ya fito a kugunsa daya kuma yana goge jikinsa kan dressing mirror dake shake da kyan kwalliya kamar za'a bude shago ya isa kan yahau goga jikinsa  da man detol,turaren avon yahau fesawa jikinsa sai da ya feshe ko'ina kana ya zura jallabiya ash colour yashimfida sallaya yadata sallah raka'a hudu yayi kafin yayi sallama yadade yana kwararo kirari ga sarki Allah daya bashi wannan kyauta haihuwa tareda addu'an Allah yakarasa masa juriya da hakurin akan sakina.

Kai tsaye bedroom din sakina  ya isa ya tura da yar siririyar sallamarsa sakina na kishingide akan gado wayace ahannunta tana latsawa yasani baiwuce chart  takeyi da kawayenta ba Hajiya kari na gefe ta baje sai kwasan barci take harda munshari dariya takusa kubcemai ya waske,kai tsaye ya isa ga jaririn dake kan dan gadonsa yaduka yasa hannu yadaukesa yana mai kare masa kallon cikin kauna,tsantsan kamar da yaron yake dashi yake kallo,hatta da yatsunsu iri dayace,sonsa da kaunarsa mai zurfi,yakamashi lokaci daya,rumgumesa yayi cikin shauki,da soyayyah ta har abada

Sakina dake kwance ta tsuramai ido tana kallon kyakyawan mijinta dogon dan safana tasani har abada bazata daina,son mijinta ba, tana sonshi har gobe kuma tana kishinsa batasan sanda tatashi ta isa kusa dashi inda yake tsaye tadafa kafadarsa ahankali ya waiwayo kwallah tataru a idanunwansa da azama yahada ta da yaron ya rumgume yana fadin"Thank u Sakina....thanks so much sakina"yafada yanajin kamar kwalla zata zubo mai.

Jikin sakina yadan yi sanyi shiyasa tayi huging dinsa back,na tsawon lokaci suna rumgume da juna kafin su saki juna suna bin juna da kallo cikin ido itace tayi saurin sadda kanta kasa saboda kar ya sata cikin wani yanayi.

Hannunta kawai yaja kiii.....Tana biye dashi har bedroom dinshi kana ya saketa ya haura gadon ya ijiye yaron yana kallon sakina cikin ido kan yace"Kinga kyautar da Allah yamana ko"?

kallonsa kawai tayi batace komai ba,yacigada da cewa"Sai wanda Allah yaso  da rabon yake basa ammh kinaso kimana wasa da damar da Allah ya bamu"yakareshe fada yana sa idonsa anata,Hamma tayi kan tahaye gadon blanket taja tarufe jikinta tana fadin"Kabarni na huta Dr haihuwa fa nayi ko barci bansamu ba"tafada tana runtse ido alaman bata son damu.

Girgiza kai kawai yayi yacigada da kallon dansa har barci ya daukesa yana kan kirjinsa,koda yatashi daddare yana tsala kuka yatashi sakina tabashi nono tsaki ta buga tana fadin"Don Allah kabarni nayi barci mana"tana gama fadar haka takara jan bargo dama tunda yazo duniya bata bashi nono ba,sai ruwa da aka bashi,shi yayi ta girgizasa asaman kafada har yayi barci saman kujerar dake bedroom din yakwanta yadorasa bisa cikinsa hannunsa zagaye dashi har gari ya waye.

Gari na waye momma ta iso part din nasu,ta iske basu tashi ba kichen tashiga tasa ruwa a kittle tazo tazauna tana jiran tashinsu,Dr Safwan ya fito sabe da yaron yana lallashinsa yatashi sai yaga momma da sauri takarisa ta amsheshi tana fadin"Yaya kuma,kuka yakeyi ne"?Sakarmata shi yayi yana fadin"Wlh momma tun jiya yake rigima"momma tace"to yasha mama kuwa"tsuru yayi mata kan yace"indai ba'a asibiti ta bashi ba ba to bata bashi ba momma"ajiyar zuciya ta sauke kan tasabaashi tana aikin jijjiga har yayi shuru.

Yana zaune momma tamasa wanka tashiryasa cikin kayan sanyin masu kyau yafito ras dashi momma tamika ma safwan tana cewa"nono yake bukata ka roketa ta duba wannan yaron karta dau alhakinsa"cikin mutuwar jiki da kunan zuciya ya amsheshi ya rumgumesa yanajin tsausayinsu har cikin ransa itama momma shi take kallo cikin tsausaya aranta tana fadin"insha allahu HASKE yakusa shigowa rayuwarka Safwan".

Huduba yayi mai kan ya mikama momma yana fadin"Sunan dady nasa masa momma"yafada da raunin murya washe baki tayi tana fadin"kai masha allahu da zuwan sabon megida Allah yaraya ka SALISU"..

WHAT....""

Sakina ta furta da karfi wacce fitowarta kenan daga bedroom cikin rigar barci kai a hargitse,.

Taci gaba da cewa cikin karaji"me kace sunan dan sali wa"? Tafada da renin wayau galala

momma tayi tana kallonta yayinda mamaki da al'ajabi ya daskarar da Dr safwan,ashe iskancin Sakina ya wuce inda yake tsammani.

Rike kugu tayi kan ta kariso falon tana cewa"tabdijam da sake an ba mai kaza kai,dan kunga nayi banza bawai ina nufin banason abunda na haifa bane balle awani roro sunan yan da na tsoffi a sama y.......SAKINA....!!! Safwan yakatseta da tsawa wanda ya firgitata har momma dake rike da jinjiri balle shi yaron daya yanka ihu tsawar ita ta data Hajiya kari, wacce take sharar barci cikin tashin hankali ta fito falo, dai dai lokacin da Safwan yace cikin bacin rai"na rantse har ga Allah  inkika karisa abunda zaki fada sakina sai na baki mamaki inkin musa kuma"yafada yana kadamata hannu

Tadan tsorata ammh tsabar rashin kunya yasa tace"me zaka iya eye "? tafada tanamasa wani kalon sama da kasa juyawa yayi zai koma daki tabishi tana fadin" Wlh ba wanda ya isa yasama d'ana wani rubabban suna wai sal...."jika ke tas!tas! ya wanketa da mari sai da ta kifa yace cikin bacin rai "wlh tallahi babu wanda ya isa ya sauyama yarona suna nine ubansa kuma nace sunan dana SALISU  inga uban da isa yachanza masa suna shashasha kawai wacce batason darajan mijinta ba"yana fadar haka ya shige daki harda bango kofa jikake bam!!!!

Kasa Sakina ta zube tana kuka tana fadin"wlh Allah ya isa,kuma zakasan waka mara sai kayi nadama kuma suna baka isa ba kasama dana wannan sunan ba"tafada tana gunjin kuka,momma tadake rike da jariri ta isa kusa da Sakina zata rikota "tayi saurin dagowa tana ballamata Harara kafin ta mike ta shige daki da gudu tana cigaba da kuka,Hajiya kari tabi bayanta.

...Momma ta koma ta zauna asanyaye Hajiya mama dake bakin kofa tace tana tafa hannuwa"yayi daidai....abun yayimin dadai wlh dahaka yakema shegiya da tashiga taitayinta"momma tayi shuru tana kallon Hajiya dake ta fada tana habaice habaice amsan dan tayi tana jijjigasa tana fadin"wai shin anbashi nono kuwa,momma tace"ina fa taki bashi...."kutumar ubancan yau ga yar iska"ba'a bada nono uwarta ta bata"tafada ahasale kan ta mika mata dan tana ficewa da sauri.

Kai tsaye dakinta takoma ta dauko wayarta kirar Nokia da Safwan ya siyamata to dayake

badamuwa tayi da wayan ba shiyasa bata cika amfani da ita ba,kai tsaye gun Habu mai gadi ta nufa tana fadin"mai sunan megida dan Allah duba ko zaka ga ansa kabiru,ya amsa yana duba mata yace"eh Hajiya gashi...Tace yauwa bugamai "tafada tana bubbuga kafa kamar wacce zatayi dambe

Bugu uku kwamishina ya dauka don yana da Nombar Hajiya maman da sallama yadauka yana gaisheta ta katsesa cikin masifa"kabiru kazo kaci ma yar iskan yarka da tsohuwar kilakin matarka mutumci"cikin al'ajabi kwashima ya mike yace cikin rawar murya"wani....Wani abun ne yafaru Haji....?"kwarai zata kashe min jika kuma ta kashe dan data haifa dan taki bashi nono"tafada kit wayar ta mutu ba chaji Hajiya mama tayi kayfci tace"kazo ayi ta kare ko ta gyara ko tabika kutafi tare ina dalili"mallam Habu dake kallonta yace"Hajiya lafiya mai yafaru"?Harara ta zabgamai kan tace"idon matambayi "Tafada tana wani harararsa afusace ta wuce takoma part din sakina.

*Shakira...*

Commet
And
Share
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE...!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza Muhammed Ba"are*

*06*

-----Aikuwa hankalin kwamishina ya tashi dama meeting suke dashi da gwamnah,suna kammallawa,direba ya wuce dashi,kaduna koda ya isa sashen Hajiya mama yafara isa,aikuwa ta lissafamai kaf abunda sakina tayi,Hajiya mama takareshe da cewa"kaduba kabiru duk tsufana bai isa sakina ta ragamin ba,to wlh tsaf take zageni balle Hadiza ai marainiyarta ce.

Hohoho Sakina taga ta kanta don marika biyu kwamishina ya saukemata sai da momma taita bashi hakuri,yayi mata gargadi da kakkausan murya kan tashiga taitayinta inba haka ba wlh tallahi sai yasa da kanshi safwan ya sauwakemata tadawo gidan,kuma taci ubanta,yasa ta dole taba yaron nono agabanshi yakuma ce inta isa ta sauyama yaron suna,Hajiya kari ba yadda zaiyi da ita illar sata agaba suka wuce katsina,har ya tafi basu hadu da Safwan ba domin kiran gaggawa yasamesa daga asibiti.

Washegari sai ga,laila tazo daga lagos ai kwamishina yace tayi maza takoma don ya haramta mata zuwa gidan sakina tunda yagane itace shedan din itada uwarsu,dole laila takoma da tarin takaichinta,salma ce kawai da ummi suka je sunnan Salisu wanda akama alkunya da Adil,sai kawayenta da yan uwa da abokan arziki,Sakina tashaka matuka shiyasa tayi alkwarin gasama Safwan aya Ahannunsa,badai haihuwa ba to ta haifa masa sai ya rena kayansa kuma haihuwa wlh har abada😳😳domin tuni tasa an juyamata mahaifa ita da haihuwa sai sadda tayi ra"ayi,anya Sakina baki *TAFKA DA KUSKURE BA*?

Kwamishina da kanshi ya dauko mai zama da Sakina goggo Ramatu daga kankia tazo tana kula da Sakina da Adil hakika goggo Ramatu taga duniya agidan sakina rashin arziki kiri kiri yimata takeyi da rashin kunya duk dan tana kokarin gyarata shiyasa datagama abunda zatayi take komawa shashin Hajiya mama su barke da Hira dama zamuce ta tarar da mujemu.

Su sakina nayin arba'in goggo Ramatu,takoma tareda shatara na arzikin da Dr Safwan ya hadamata hakika tayi kewar mutanen kirki hajiya mama da momma tatabbatar da Sakina tana kokarin Tafka kuskure matukar tabari suka sallamata.

kamar jira take tayi arba'in tacigaba daga inda ta tsaya washegarin ranar tatafi kano wai anyo mata odar kaya,haka take kullum cikin yawo,kuma Adil agida take barinshi sai dai kaganshi bayan Hajiya mama ko bayan Momma suna aikin jijjiga in dare yayi Safwan ya amshesu wlh har kwallah sukemai aboye saboda tsausayin Dr safwan bai huta asibiti ba kuma agida ba Hutu,shidai kawai yabarma Allah komai ya yarda cewa wannan itace KADDARARSA.

**************************

*Zamfara*
Zurmi...

Tafe suke su biyu sanye da dogayen hijabai marun colour har kasa da nikabi kafafunsu sanye cikin safa baka ganin komai sai tafin hannunsu,littafaine a hannunsu sun rumgume alamar daga mkrantan islamia suke.

Aisha ce takauda shirun dacewa'Nikuwa *SAFEENA* ina so in tambayeki"?

wacce aka kira da Safina tajuyo tana kallonta ta cikin nikabin ta tace cikin siririyar muryanta"Nasani daman zaki tambayeni....Nasan mganan bata wuce ta mallam yahuza ko"?

Aisha tace"oh ashe ma kinsani....Ni wai meke tsakaninku anya ba sonki yake yi ba"?

Dariya Safeena tayi mai ban sha'awa kan tace"Nima ban sani ba Aisha....Kawai dai inajin wani iri in ina tare dashi"
Duka Aisha tadakamata kan tace"Yar iska ashe dama kina sonsa"

mirmishi kawai tayi batayi mgana ba har suka iso kofar gidan su Safina,Safinar ce taja ta tsaya tana kara rumgume littafanta tace"To sai gobe Aisha ki gaida mama"

"ALLAH yakaimu nima kigaidamin da Ummi yammah tayi shiyasa bazan shigo ba.."

Mikewa Aisha tayi,ita kuma Safina tashiga wani dan madaidaichin gidan bulo,da sallama tashiga,Ummi dake kichen ta fito tana amsawa,

Safina tace "Sannu da aiki Ummi" amsawa tayi cikin farinciki yauwa"Safinatu baiwar Allah andawo" tace"eh Ummi ina Abbah,tace"Yanzu ya fita zuwa massallachi shida Usman.

Shiga daki tayi ta kware hijabin jikinta da Safa da nikabin,sanye take da riga sikat na atamfa sunmata das da ita fitowa tayi tazari buta tashiga ta kama ruwa kan tafito tayi al"wala tashiga ta gabatar da sallar mangariba tadade tana azkar kafin ta mike ta fice ta iske Ummi na kwashe tuwo ta taimakamata suka kwashe suna Hira.

Ta idar da isha'i kenan taji sallaman Abbanta da shi da Usman kaninta,da sauri ta fito sanye da hijabi tana fadin"Sannu dadawowa ABBAH"

Yadago cikin annuri yace"Yauwa HAFIZA SAFINA brkan ki da gida"

Mirmishi tayi kan ta sunkuyar da kanta tana dariya saboda haka Abbanta ke kiranta saboda zamowarta Hafiza abangaren Alqur'ani mai girma.

da sauri takoma daki ta dauko tabarma ta shimfidamai tare da kawomai abincinsa da roban wanke hannu lokaci Daya tana  zauna a gefen tana fadin"Abbah yau aka fada mana amkranta zamu jigawa gasan alqur"ani kuma dani aciki"

"Masha Allahu....Allah Yasa albarka Allah ya albarkaci Rayuwarki" ta amsa da Amin ta na mai jin farinciki bismillah yayi kafin yafaraci shida usman ya kalleta yace"Sako hannunki Safina muci tare ko masamu albarkan ci cikin taro"cike da zumudi ta wanke Hannu ta tsoma suna ci suna Hira sama sama.

Ummi Data sallame sallah ta fito tazo tazauna tana fadin"Au abun na ya"ya ne kenan "kai tsaye yace mata"eh na ya"yane iyaye sai su koma baya"

..Safina tace"La Ummi kema fa kinsan tare muke ci da Abbah kema kinso kiyi mgana ne"

"Allah miki albarka,tasani jan magana  ne kawai"

Ummi tayi mirmishi tace tana zama"Ni ne maijan mgana..? yace"to waye,?rigimarki nada yawa Zainabu ko safina bazatayi abunda kikeyi ba"

Kai tsaye tace'Me nakeyi..? tafada tana kallonsa shima kallonta yakeyi kafin yace"Kinfini sani"saurin sunkuyar dakai tayi tana dariya Safina tayi dariya Ummi ta dungureta mata kai tana fadin"Baki da kunya ko"

Yace"kyalemin yata itama tasan gaskiya.Haka suka kammallah cin tuwonsu cikin farinciki da annushuwa.

*Shakira..*

Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba"are*

*07*

WACECE SAFINA

*SAFINA ALIYU ZURMI* shine cikakken sunanta,mahaifinta mallam Aliyu zurmi dan asalin garin zurmi ce dake jahar zamfara malami ne wanda ya shahara abangaren ilimin addinin islama,yana da matar aura guda daya wacce ta kasance diyar malaminsane dayayi karatu awurinsa agarin jalingo bafullatanan chan ce,to dayake yakasance na hannu daman mallam alokacin shiyasa ya dauki yarsa zainabu abu ya aura masa batareda yayi duba da shidin marayane wanda baida komai,da kowa ba,hakika zainab tacika ya tama mahaifinta biyayyah,su biyu iyayansu suka haifa ita da yayarta iyami,tare akayi bikinsu da iyamin wacce ta auri wani dan kasuwa a safana ita kuma Aliyu yadaukota suka dawo zurmi da zama.sana'ar saida hatsi yake a kasuwa Allah yasama abun albarka sunada rufin asirinsu.

Aurensu da wata biyu suka samu,Ibrin rasuwar mahaifansu,sakamakon gobara takamasu cikin dare hakika anyi matukar rashi,rashi ma mai girma daga baya suka fauwalama Allah komai suka rumgume mazajensu.

sai da Zainab ta shekara,uku kana ta haifi yarta mace wacce aka samata Safina hakika safina tazo dawani al"amari domin soyayyata tuni tayi katutu azuciyar iyayanta,tun tasowarta

yarinyace mai hankali da Natsuwa,ga hazaka mahaifinta yazage gurin koyamata ilimin addini tana shekara,goma sha biyu aduniya ta sauke alqur"ani,tana bitan sauran littafai.alokacin ne kuma ta sake haihuwan Usman daganan haihuwa ta tsayamata.

Tana da shekara sha biyar da aduniya ta kammallah sakandiri sch dinta sakamakon yarinyace da duk,garin zurmi ansan da ,da baiwanr da Allah ya bata,tana aji biyu a sakandiri akamata jumping taje ss1,Safina tahaddace sahihul bukhari da muwadda malik tana da sanin kan hadisi sosai gasan alqur"ani kuwa na gari gari ba inda bata zuwa kuma tayi na daya,hatta mkrantansu suna alfahari da ita tuni ta kammallah aji shida yanzu suna ajin manyane.

Iyami wacce suke kira inna bata taba haihuwa ba har Allah ya karbi ran mijinsu to dayake kishiyarta nada ya'ya tare da ita suke rike dasu har kwanan gobe,Safina tana bala"in son innanta iyami saboda har hutu take zuwan mata,da kuma Aminyarta Hajiyar safana wacce wanchan zuwan datayi inna iyami ke fadamata,jikanta yadauketa sun koma kaduna duk da bataji dadi ba shiyasa safanar tafita aranta.

Samari dadama suna kawoma safina kai ammh bata basu dama ba saboda burin mahaifinta na zamowarta wacce al"ummah zasuyi alfahari da ita tareda kasarta Nageria,tana son iyayenta saboda suna da kyakyawan alaqa atare dasu inkagansu suna raHa da ya'yansu kace kannensune.

Safina yanzu tana da shekara goma sha bakwai ne aduniya yarinyace doguwa,bakace domin mahaifinta ta dauko sak doguwar fuska gareta tareda dogon hanci tana bakinta dan daidai matsakaitan idanuwa gareta Safina bawata kyakyawan azo aka gani bane ammh kyanta mai tattare da baiwane,tana da dogon gashi har baya baki silik wanda saboda yawansa yasa take kitso biyu ta rabu dashi.

Dirinta mai tsayawa arai ne domin daga kasanta a tsuke take samanta shima atsuke ba kallo daya zakamata kafahimci ta mallaki baiwa mai tarin yawa ba  sai ka zauna da ita,miskilace ta karshe bamai wayan haniya ba tanada zurfafa bincike kullum agida in bata komai to zaka ganta cikin Nazari ne shiyasa iyayanta ke alfahari da ita matuka.

Bata jin wani namiji ya burgeta ba saboda kaf masu cewa suna sonta bbu wanda yadace da tsarinta,tana son Namiji yakasance mai aji ne kuma yakansance yanada fukafukai guda biyu wato ilimin addini dana zamani yakuma kasance yafi zurfafa ana addini,sosai yakuma zamonto mai alkunya,kawaichi,da dattako,kuma bamai yawan kwaranniya ba kuma wanda yaba duniya baya wanda yafi fuskantan lahirarsa yakuma kasance mahaifiyarsa na raye saboda tasamu makwafin Umminta,Nikuwa nace tab anya Safina zaki samu kuwa🤔

Mallam yahuza ne yakusa hada wannan abubuwan duk da baigama hadawa duka ba ammh taji ta natsu dashi duk da bai furta yana sonta ba ammh alamu sun nuna haka,mallam yahuza malaminsu ne amkrantan dasuke karatu wanda kowa yasan matashine jajirtattace mai ilimi da hangen nesa,shiyasa dashi kadai zakaga Safina na mgana harda mirmishi.

WANNAN KENAN

*********************

KADUNA

----Yau din ma Sakina kano ta kama Hanya tatafi tabarma shazeey Adil shazeey wata kedarace mara sallah Sakina ta dauko a mtsayin Nanny wacce zata reni Adil sai da takwana biyu da zuwa kana Dr safwan ya ganta bakinciki kamar yakasheshi yanzu ace arasa wacce zata renin mai d'a sai,kafura mara sallah kuma ace har yakoyi wasu abubuwa atareda da'ita,dawannan bakinciki ya isa shashen momma Adil na sabe akafadarsa wanda yanzu kimanin watansu uku yayi bulbul dashi sai wutsul wutsul yakeyi ahannunsa.

Momma na zaune cikin dakin Hajiya tana shafamata man zafi akafa saboda tace yau kafan ta matsamata,chan kasan makoshi yayi sallaman wanda momma ce kawai taji shi,kai tsaye ya shigo ya zauna kan stool din gadon yana rumgume da Adil momma takallesa tsausayinshi na tsirgamata.

Hajiya mama taja tsaki"mtwssss...Kai wai da girmanka kashigo ma mutane daki babu sallama" banza ya mata bai tankataba takara harzuka tace"Kai tashi kafita tunda ba dakinka bane haba ina dalili kazo kama mutane zaune kamar kabasu ajiya"
A Harzuke yace"Haba Hajiya kewai baki gane yanayin da mutum ke ciki ne eye"?yafada dadan karfi galala tayi tana kallonsa kan ta kwace kafarta tagyara zama tace"To Habule gani dakeni kaji tunda wuyanka ya isa yanka"tsaki yaja kawai ya mike yana gaida momma kan ya mikamata Adil yana fadin"momma ki rikesa agurinki zan tafi asibiti," tasa hannu ta amsheshi kan tace"Adawo lafy Allah yabada sa"a" ya amsa da Amin

Hajiya mama tafara salallami tana fadin"yau anyi tsinanna yau din ma ficewa tayi tabar d'an oh ni maryama naga takaina"tafada harda dora hannu akai,Dr Safwan ya isa bakin kofar yana fadin"Momma ko anzo karbarsa kar kibada shi.. Wai sakina arniya ta dauko wai ita zata renanmim d'a,dan Allah momma ki rike adil agurinki nasan bazaki gazaba"Ai da sauri Hajiya ta sauko daga kan gado tana fadin"Ar....Me lalle sakina yar tasha ce yanxu haka ta raina mutane to wlh billahil azim sai tabar gidannan bazan zauna da kedara ba agidannan ba wlh"Tana fadar haka tabi bayan Dr safwan tafice fuu.

Yana kokarin shiga mota yaga ta shige sashensa,kada kai kawai yayi ya shige mota yabata wuta don ahalin dayake ciki baida lokacin hajiya mama.

Shazeey taga bala"i domin hajiya mama tadunga mata watsii da kaya bayan tagama tasa yan aikin Sakina sujata sufitar da ita dagan gidan,fadi take"kuja shegiya kafurar banza agidan nan wlh baki isa kizauna ki koyamana kafurci ba kuja shegiya nace🤣🤣🤣sukuwa suna janta tana kuka tana rokon hajiya mama tana fadin"Madam plz help me....Srrry ho..."sorin uwarki inkika kara kirana madam sai kinci ubanki"waje suka watsata sai da kanta yabugu da kasa da sauri tace"jesus ai da wani gudu Hajiya tabita tana fadin"mun shiga uku zata konamu jejesas din babanki😂 agidannan,Ai da gudu shazeey ta rarimi kayanta megadi yabude mata get tayi waje,Hajiya tace"tsinanniya kawai da ki tsaya dasaina na fasa katon kanki kamar na kwakwa🤣🤣🤣🤣kowa na kunshe dariyarsa sabida in Hajiya taganka wlh sai kasani.

Momma tana gani ammh batayi mgana ba saboda sanin halin hajiya yanzunan ta dawo kanta Ranar hajiya wuni tayi tsinema sakina da uwarta daga karshe akace"ai ba shegen d'a irin sufiyanu sai da na hanasa daukoma yarinyannan saboda nasan arina ko ganin uwarta kamar wata tsohuwar kilaki amma dayake kunnen
kashi gareshi ya kwasomana bala'i har gida,daga baya kuma aka hau share hawaye tana fadin"Allah ya jikanka salisu dakana nan a raye dabai auromana tsinanniyan yar"nan ba🤣🤣🤣🤣Haka hajiya ta wuni ashar.

*Hoho sakina kinga ta kanki tunda Hajiya mama ta tsaneki*😂😂😂

*Anitha...*

Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

_Ina mata yan kwalisa masu Bukatar su Fito su kere Sa"a cikin Sa"anni ko matan abokai ko cikin kawaye..? Ina Mata wadanda ke Bukatar Gwangwajen ya"yansu cikin kayan alfarma domin kere sa"a da Fitowa cikin Alfarma cikin Sa"aninsu,Toh duk kusha Kuruminku ina tafe muku da Wani Karin Albishir ko kuna da Labarin DIJA COLLECTION,wanda ya Hada komai na kayan kawan Mata da maza domin fitowa Tsab,da Sanya mata suna Dagawa..?Ki hanzarta ko kuma mu hanzarta wajen samun daman zama mace yar Kwalisa muna saida komai na kayan adon mata da maza da yara,Irinsu Atamfa,leshi,Material,Takalman mata dana maza na yara dana manya,akwai dan kunnaye masu kyau da Tsari,kina bukatar mayafai na nuna Tsara..? Toh duk zaki samesu a Dija Collection ,kina bukatar Abaya.. ?shima karki damu duk zaki samu a Dija Collection kayanmu suna da Ingancin Domin ingancinmu ne yasa muka Cigaba,Zaku iya Tuntubarmu ta wannan Nombobin wayar kamar haka 07045112780,ko kuma 09036617473,Sai kunzo...karku Manta Siyan Nagari mai da Kudi Gida.._

*08*

------Koda Sakina tadawo ta iske hajiya mama ta kora mata shazeey Ranta yabaci tadinga yada mganganun acikin gida,takira hajiya kari tafadamata,suka taru suka dunga tsinema Hajiya mama ita kuwa Anty laila cewa tayi"Fine and good sai kibarmusu dansu su rena tunda sun raina kokarinmu don dai bazaki zauna ki ijeye kasuwancinki kina masa rainan d'a ba"

Sakina ta shaka game da Hajiya mama Shiyasa ta kudiri niyyar yi musu abunda bazasu manta da ita ba,ammh duk maganganun data keyi,iya shashen ta ne,don tasan wacece hajiya mama,in Taji ta jita bazata ji da dadi ba.

*Zurmi...*

Usman ne ya sheko da gudu cikin gida,yana haki Ummi dake bakin rariya tana wanke wanke,tasaki aikin tana fadin"Usman...Lafiyarka kuwa?"yana haki yace"Ummi yaya Safina ce nagansu yanzu suka dawo"

Ummi tasaki mirmishi tace"ikon Allah...Allah yadawo dasu kenan"?

"eh...."yabata amsa kan yakara shekawa da gudu,yakara ficewa.

Ummi ta rausayar dakai tace,"oh Usmanu ba dama,ta cigaba da wanke wankenta cikin farin ciki na dawowar yarta daga jigawa gasar karatun qur"ani ta jaha na Fidda gwani kwanansu biyu.

Ta kammallah kenan taji sallaman yar' tata cikin farunciki tareda rakiyar kawarta Aisha,da gudu tarumgume Ummi tana Fadin'oyoyo Ummi nayi kewarku wlh"

Ummi tana dariya tace"Oh Safinatu na barka da dawowa "Safina tace"yauwa Ummi nasameku lafiya"?

Aisha tace"la Ummi shine dan kinga Safina kika manta dani,Ummi tayi mirmishi tana fadin"haba ai har abada Aisha kema diyatace kamar yadda Safina take diyata"Mirmishi sukayi tare Usman kuwa yana jidan kyaututtukanta yana shiga daki dashi

Aisha tace"Ummi ku tayamu murna Safina taci lambar yabo ta daya  a jahar mu ta zamfara"guda Ummi tasaki tana nuna Farincikinta.

Abba daya sawo kai cikin gidan yake fadin"Ash....Ash...Zainabu guda kuma"?

ta amsa da cewa "Nuna farinciki ne Abbah diyarmu tasamu nasarar cin gasan zuwa gasan a kasa  gabadaya zata wakilci jahar zamfara.

Yana kawata fuskarsa da fara'a yana fadin"Masha Allah yakamata ki furta zainabu ba guda ba ko so kike hancinki awuta"yafada da tsigar zolaya gabadaya aka sa dariya.

Safina ta isa kusa dashi ta durkusa tana fadin"sannu dadawo wa Abba"ta fada tana amsan ledar dake hannunsa cikin Annushuwa ya mikata mata yana fadin"Masha Allahu Hafiza safinatu natayaki murna da sauran al"umnah gabadaya Allah yasa abunda kikasa gaba ya amfaneki da sauran al'ummah gabadaya"

Atare suka amsa da Amin Abbah,Aisha ta gaisheshi ya amsa yana samusu albarka kafin Ummi ta zuba masa ruwa  a buta ya gabatar da al'awala shida Usman suka wuce massallachi.

Sai da taraka Aisha gida kana tadawo tayi sallah suka shimfida tabarma suna Hira da Umminta tana bata Ibrin abunda ya faru achan gurin gasar fidda gwanin,Abbah ya yo sallama suka shigo Safina ta kawomasa Abincinsa da roban wanke Hannu,sai da ya kammallah,ya wanke Hannu kana yace"Safina..."Ta amsa da Na'am tajuyo tana kallonsa tana basa hankalinta.

Yafara da" Alhamdulillahi daya nuna min wannan Rana Hakika Allah ne abun godiya,Allah nake roko yasa abunda kikasa gaba ya amfaneki agaba dake da ya'yanki da al'ummah baki daya"Suka amsa da Amin....

Yaja fasali kan yakara kiran sunanta"Safinatu.... Ta amsa kanta na kasa yacigaba da cewa"kafin tafiyarki Malaminku yazo yasameni game da yana neman izini awurina nabashi da dama yanemi auranki"Arazane tadago tana kallon Abban Nata.

Ummi tace"ikon Allah,Safina taji kirjinta na lugude tasaci kallon ummi,Ummi takalli Abbah tace"to kai baka fadama diyar taka ko wanene ba?"Dan murmusa yayi kafin yace"ah nazata tafini saninshi"Da sauri tace"Wlh Abbah ban sani ba"Sai kuma da tafada kana ta Sunne kai a kafadar Ummi tana dariya,Ummi ta dungureta tace"yar nema kawai" Abbah yace"kyalemin uwata,nasan bata sani bane,bakowa bane sai mallam yahuza"tagefen ido ta kalli Abbah kana ta kalli Ummi,Ummi tace"Masha Allah yaro ko mai Hankali Allah yasa albarka"Tafada tana kallon Safinar dake sunne kai tace"to kina sonshi..."?

Abbah yace"Ash...Zainabu kincika azarbabi wlh"Safina tatashi da gudu tashige daki tana dariya,Abbah yabi bayanta da kallo yana Fadin"kin korarmin mamata ko baki kyauta ba,Ummi tace"daga abun arziki yabata amsa da cewa"ba'a son taimakon ki barmu mana"Usman kuwa murna yakeyi wai yaya zatayi aure su Ummi suka bisa da kallo suna dariyar yarintansa.

Safina kan gado tafada tana dariya filo tajawo ta sanya akirjinta,tana lumshe ido tabbas mallam yahuza koda batasan so ba tanajin wani yanayi atare dashi,ta tuna sanda suka dawo yake jifanta da wani shu"umin kallo na wanda ya mutu kan sonka,ita kunya yasata ta kauda kanta,tadade kwance tana saka tana warwara kafin barci yakwasheta.

*Kaduna...*

Yau din Dr Safwan yakasa controlling din kansa tun a asibiti yakejin yanayinsa na chanzawa tabbas yamayi kokari baisan yaushe rabon sa da Sakina ba.

Adaddafe ya isa gida ko sassan momma bai isa ba, ya nufi sashen sa kai tsaye dakin Sakina

yama tsinke tana kwance kan gado tayi daidai tana waya ya shigo ta wutsiyar ido ta kallesa taga yazuba mata ido,yana mata wani kallo idanuwansa sun kankace,kallo daya tamai tagane halin dayake ciki,shiyasa tayi mirmishi tagefen baki ta watsar dashi ta cigaba da danna wayarta.

Yaga bata da alamar sauraransa,yasa ya Nufeta ya fizge wayar yana kallonta da idanuwansa wanda bakomai aciki sai zallar desire tace'Mallam lafiya?

"tafada tana wani binsa da ido cikin zafin Nama ya isa gareta ya fizgota suka kara fadawa kan gadon rumgumeta yayi yana shinshinan wuyanta yace cikin wata murya kamar ta mashaya"No sakina...Karkimin haka kema kinsani....I need u on bed"fizge jikinta tayi kan tace"ahayye....Dama nasan zaka zo ai tunda yanzu ina da amfani to wlh kajima na rantse bazan baka kaina ba ai daman nace nida kai ne acikin gidan nan"

Tsuru yamata da ido yana kallonta jikinsa duk yayi sanyi kasala hadi dawata sha"awa mai karfi ya taru ya dannesa dakyar yayi karfin halin mikewa Ya karisa gareta zai rumgumeta ta dakatar dashi dacewa

"tsaya tsaya karma  kamatso don wlh bazaka samu ba kaje wa'inda suka fini daraja su baka"tafada tana wani gatsina zubewa yayi agabanta yana fadi Cikin kasalallaciyar murya"plz.....Sakina ki mun rai ki tuna rabona dake tun kan ki Haifi Adil...Plz in kika hanani bansan ina zani ba bansan wani hali zan shigaba ko so kike inje inyi zina"?

yafada yana tsareta da ido tsaki ta doka kan tace"to kaje kayi zinar mana ruwan wa?"tafada tana zakuda kafada wayarta ta dauka tafice daga dakin ta bamko kofa jikake bam...!

Sororo yabi bayanta da kallo kafin ya sulale kasa yana dafe da mararsa,ya runtse ido cikin kuna da takaichi ransa na masa kuna yana ji aransa cewa mutuwa zaiyi matukar bai fitar da abunda ke damunsa ba gashi tunda yake bai taba kusantan zina ba.

Yadade zaune kan yararrafa ya mike yana tangadi ya fice daga dakin kai tsaye sashen su momma ya isa yasamesu zaune afalo Hajiya na kan kujera tana kwakulan goranta ita kuwa momma tana bawa Adil madarararsa,yana shigowa yafada kan kujera yaraf yana dafe da mararsa cikin kunan rai da azaba.

Momma tace"Subuhanallah....Hajiya ta mike tana salallami tana fadin"Kai lafiyar ka kuwa

mutuwa aka yi Hala.?

*Shakira...*

Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO: My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*09*

-------Kusa dashi haj.Mama takarisa tana Fadin"Kai sufiyanu wai lafiyarka kuwa? ko baka da lafiya ne?

shuru yayi mata yana dafe mararsa cikin azaba,saboda bazai iya bude baki yabata amsa ba cos muryan nasa bazama ta fito ba.

Haj.Mama fusata tayi tace"Kada Allah yasa ka fadamin,Mara mutumci kanaji ana mgana kama mutane banza,chan da tsiyarka.."

Momma dake gefe rike da Adil ta zurama danta ido tsausayinshi na ratsata kwallah tatarun mata cikin kwarmim ido tayi saurin sharewa ta mike ta isa kusa dashi tadafa sa tana cewa"Ayya babana meke damunka? baka ji Hajiya na mgana bane..?

Haj.Mama ta amshe da cewa"yana ji wulakancin sane ya tashi to wlh yafi kowa sanin gidanta ya tarar"..tafada harda buga cinya momma tayi shuru tana kallonsa yana kara dukunkunewa cikin kujera Haj mama tayi tsaki tace"mtwssss....Kawai kazo saboda bakin hali katasamu kana mukurkusu kamar wani mai Nakuda,kaji dashi dai"

Momma dai tayi shuru ba'a bin tayi mgana ba Haj.Mama ta hada da ita,yana jinta yayi banza iska da ita sai da yaji yadan samu dama kana ya mike ya nufi kichen yana tangadi haj.Mama tace'"oh ni maryamu dama yunwa ce tasaka wannan aikin yau ga dan iskan yaro shine kana ji ana mgana kayi mana banza"ko waigowa baiyi ba yakarisa kichen din yafara bude buden durowa haj.Mama tayi firit tabishi tana fadin"wai kai kabamu ajiyane"?

Tsaye ta ganshi yana Neme neme tsayawa tayi sororo tana kallonsa wata durowa yajawo sai ga lemon tsami da sauri ya dauka yadauko kofi ya yanka da wuka yana matse ruwan yakafa kai zai sha Haj.Mama ta rike tana kallonsa ido cikin ido.

Fuska ya daure kan yace"mene....Sakarmin"yafada muryansa ta shake Haj.Mama tace"Anki a saki wlh bazaka shaba ba ka  kashe kanka ba"kara hade rai yayi kan yace"ki rabu dani nace"yafada da tsawa Sakin mai tayi shikuwa ya kafa kai yashanye yana dafe mara,nan kichen din ya sulale yana dafe mararsa data kulle wuri daya.Haj.Mama tayi tsam tana kallonsa ita ba yarinya bace tafahimci halin da jikanta ke ciki tsausayinshi ya rufeta domin tasan gado yayi gun kakansa shima ba dama🙈kaji haj.Mama🤣

Cikin zafin Nama da bacin rai ta fito daga kichen din ta wuce momma dake zaune tana sharan kwallan tsausayin d'anta  kwara daya tal data mallaka aduniya ake neman zauta mata mishi tadaga Hannu sama tace"Ya Allah kana ji kuma kana gani...Ka kawoma wannan bawa naka mafita"takareshe fada hawaye na zuba bisa kuncinta har shima Adil kamar yasani yasa kuka,jin kukansa yasa Dr Safwan fitowa bayan abun ya lafamai kan kujeran ya koma ya zauna yadafe kai,momma ta kallesa tace"kadinga maimata innalillahi wa"inna ilaihirraju"un zaka samu sassauci aikuwa cikin kankanin lokaci yaji komai na sauka kamar ana sacce taya🤣

Sakina Na kan kujera remot ne ahannunta tana sarrafa tashoshin talabijin Haj.Mama ta fado falon bako sallama Sakina tadago tana kallonta da mamakin ganinta tace"lafiya....Uwarki nace"Haj.Mama tabata amsa tana nuna ta da yatsa Sakina tayi tsam tana kallonta kan ta maimaita da sigan tambaya"Uwata fa kikace? eh ita ko zaki rama ne"Sakina tayi mirmishin gefen baki kawai ta maida hankalinta a kallon talabijin din Haj.Mama ta harzuka tace"Uban me kika mai gashi chan ya kwantamana magashiyatan"?shekeke ta kalleta kan tace"Au bai fada muku ba?" Haj.Mama tace"daya fadamana zaki ganni nazo tambayarki rasa kunya meran tanka"shewa sakina ta saki kan ta mike tayi taku zuwa gaban hajiya tace"Naji dadin zuwanki domin dama ke yadace in bama sakon....Kinsan me yake damunsa?

Taci gaba da cewa" kaina yace in basa na hanasa,ko zaki iya bashi naki ne kinga sai ki wuce mai takaichin..."🙆🏽‍♀️ tafada tana wani ware hannu alamun ko ajikinta,haj.Mama ta daskare tsaye tana binta da kallo Hawaye yana zuraro mata a idanuwanta.

Sakina tashiga tafa hannu tana fadin"good.....Indai zaki iya bismillah...Bake uwar shisshigi ba ke komai da ruwanki ba,to kinji mtsalar jikanki inkina da maganin mtsalarsa to bismillah"haj.Mama ta share hawayen ta tace"lalle kin cika tabbatacciya sai yau nagane Sufiyanu bai yi dacen mata ba,naji bazanmai maganin mtsalarsa ba ammh ina so kisani zan kawo wacce zata iya mganin mtsalar tasa ke kuma zaki gane *KIN TAFKA KUSKURE*"

Daga haka ta fice tana sharan Hawaye da Haban zaninta,haka ta iske su momma zaune Tatasa Dr Safwan gaba yana cin abinci Adil na goye a bayanta,kallonsu Hajiya mama tayi taji mugun tsausayinsu ya mamayeta ta kasa mgana kawai ta fashe da kuka ta shige daki.

Cikin tashin Hankali momma ta kalli Dr Safwan shima ya kalleta,kan yayi saurin tsame hannunsa cikin abinci ya mike yana Fadin"momma....Me zaisa hajiya kuka"?itama mikewar tayi bata samu zarafin mgana ba tafada dakin Hajiya suna zuwa su isketa tana shirya kayanta cikin bakkonta🤣Allah sarki Hajiya,tana sharan hawaye.

Momma ta durkusa gabanta tana fadin"Hajiya...Lafiya kike kuka ko an miki wani abu ne?"shuru Haj.Mama ta musu tacigaba da hada kayanta Ajiyar zuciya Dr Safwan ya sauke kan ya isa kusa da Hajiya ya riko Hannunta yana Fadin"Hajiyata...."yafada da tsausasawa tadago tana kallonsa idanunta jajir ya cigaba dacewa"Hajiyata mene ya Faru,Rayuwa bazatayi mana dadi ba matukar baki fadamana meke damunki ba"yafada yana kara damke Hannunta,

Rike Hannun nasa tayi kan tace"Babu komai jikana....gobe in Allah ya kaimu zan tafi Safana,da sauri ya kalleta zai yi mgana tace"A"a kar kace komai kwana biyu zan yi in dawo"Ajiyar zuciya ya sauke kan yace"Har naji sanyi hajiya ta nazata zaki barmu ne"Ya kareshe fada da wata raunanniyar murya.

Girgiza kai tayi tace"Inje ina sufiyanu...Har ABADA kune ahalina bayan ku banda kowa"Tafada tana kallon Hadiza rumgumeta yayi yana Fadin"Nima Hajiya bazan iya rayuwa baki cikinta ba,koda fadan damukeyi mudunga yi wlh ina matukar jin dadi"Dunguremasa kai tayi kan tace"Dan Nema wato da gangan kake jana ko"Kansa ya aza kan kafadarta yana fadin"thank u

hajiya thanks momma for keeping me Happy"

Hajiya mama ta kalli momma tace"wai meyace Ne naji yana kirana ne Allah yasa bazagina yayi ba wlh inci ubanshi"🤣gabadayansu suka sheke dadariya har Hajiyan.

*Turkashi....Kowani mataki haj.Mama zata dauka sai kun biyoni a shafi na gaba ammh karku manta*

*Commet Share and Vote Domin kwarin gwiwata*

*Anitha...*
[10/14, 20:01] Sis Janafty: _Ina mata yan kwalisa masu Bukatar su Fito su kere Sa"a cikin Sa"anni ko matan abokai ko cikin kawaye..? Ina Mata wadanda ke Bukatar Gwangwajen ya"yansu cikin kayan alfarma domin kere sa"a da Fitowa cikin Alfarma cikin Sa"aninsu,Toh duk kusha Kuruminku ina tafe muku da Wani Karin Albishir ko kuna da Labarin DIJA COLLECTION,wanda ya Hada komai na kayan kawan Mata da maza domin fitowa Tsab,da Sanya mata suna Dagawa..?Ki hanzarta ko kuma mu hanzarta wajen samun daman zama mace yar Kwalisa muna saida komai na kayan adon mata da maza da yara,Irinsu Atamfa,leshi,Material,Takalman mata dana maza na yara dana manya,akwai dan kunnaye masu kyau da Tsari,kina bukatar mayafai na nuna Tsara..? Toh duk zaki samesu a Dija Collection ,kina bukatar Abaya.. ?shima karki damu duk zaki samu a Dija Collection  suna da Ingancin Domin ingancinmu ne yasa muka Cigaba,Zaku iya Tuntubarmu ta wannan Nombobin wayar kamar haka 07045112780,ko kuma 09036617473,Sai kunzo...karku Manta Siyan Nagari mai da Kudi Gida.._
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

_Ina mata yan kwalisa masu Bukatar su Fito su kere Sa"a cikin Sa"anni ko matan abokai ko cikin kawaye..? Ina Mata wadanda ke Bukatar Gwangwajen ya"yansu cikin kayan alfarma domin kere sa"a da Fitowa cikin Alfarma cikin Sa"aninsu,Toh duk kusha Kuruminku ina tafe muku da Wani Karin Albishir ko kuna da Labarin DIJA COLLECTION,wanda ya Hada komai na kayan kawan Mata da maza domin fitowa Tsab,da Sanya mata suna Dagawa..?Ki hanzarta ko kuma mu hanzarta wajen samun daman zama mace yar Kwalisa muna saida komai na kayan

adon mata da maza da yara,Irinsu Atamfa,leshi,Material,Takalman mata dana maza na yara dana manya,akwai dan kunnaye masu kyau da Tsari,kina bukatar mayafai na nuna Tsara..? Toh duk zaki samesu a Dija Collection ,kina bukatar Abaya.. ?shima karki damu duk zaki samu a Dija Collection  suna da Ingancin Domin ingancinmu ne yasa muka Cigaba,Zaku iya Tuntubarmu ta wannan Nombobin wayar kamar haka 07045112780,ko kuma 09036617473,Sai kunzo...karku Manta Siyan Nagari mai da Kudi Gida.._

*10*

-----washegari kuwa da duku duku Haj.Mama tace zata tafi,direba Dr safwan yahada ta dashi haj.Mama ta hau fada kan mene wai ita ake mata haka ne yanzu batada ikon tafiya sai an wani hadata dawani gard,to hala bacewa zatayi ne,dakyar ya lallabata ta shiga motan direba yaja suka lula hanya Momma takoma cikin gida cikin kewar Hajiya.

Sakina kuwa Dr Safwan na ficewa ta kece dadariya tafada kan gado tana fadin"yaro...Yaro ne inba yarintaba kagama wulakantani sannan kadawo kace in baka ai kayi kadan,Badai haihuwa ba gashi chan na haifa na ijiyema..Sai ka raina d'an nikam nida haihu ho ba yanzu ba"duk ita kadai take magunganunta,takira haj.Kari tana fada mata sai cewa tayi"kinyi daidai yata gwara kinuna masa kincika yar halas".

Hajiya na wucewa ya shirya cikin suit ash and black ya daure wuyansa da tektie kafarsa cikin sawu ciki bakake na fatar damisa,rigar likitocin sane sabe a kafadarsa,hannunsa dake daure da agogon fata na kamfanin Rado ke cikin aljihu daya kuma yana latsa waya yana fitowa sakina dake kwance kan kujera tashaki kamshin turarensa Azzaro visit.

Ta gabanta yabi ya wuce ko kallonta baiyi ba yasakai yafice kwance take ammh sai da ta mike kishi ya turniketa naganin yadda mijinta yahade ammh ya sakai ya fice ko kallonta baiyi ba,tsaki tayi kan tace"chan ta matse maka,takoma ta kwanta tana hammah kan nan kamar anyi wasan kura dashi..Allah ya kyauta.

Sashen momma ya shiga ya karya yama Adil wasa kana yafice zuwa asibiti ta bishi da Allah ya kiyaye.

Ko a Asibitin Dr Tahir ya fahimci Dr Safwan na cikin damuwa ya tambayesa yace babu komai,bai matsamasa ba, ya rabu dashi iyakata dai yasan bata wuce matsalar Sakina kullum addu"an shi shine Allah yadubi abokinsa ya kawo mai mafita ta alheri na alheri.

*********************

*Safana..*

Misalin karfe 11 na safe Direba ya isa Safana da Haj.Mama bayan ya Sauketa ne yatambayeta yaushe zata koma yazo yadauketa ballamai harara tayi kan tace

"to Habule randa kace"ta kareshe fada harda murgudamasa baki kama baki yayi yana Fadin Allah yabaki Hakuri Hajiya adawo lpy,ko kallonsa batayi ba tawucewarta,kada kai yayi ya kara gaba.

Ba tsohon gidansu da Dr Safwan ya gyara tafara isa ba,da yake nan suke sauka in sunzo,ba chan tayi ba wai bazata iya zama ita kadai ba,direct gidan kawu Bala ta nufa kani yake agurinta sai dai Uwani matarsa taga hajiya kwatsam,nan ta tarbeta cikin farinciki da jin dadi kawu balan bai nan ya tafi kasuwa bai dawo ba sai dare yazo ya tadda Hajiya yayi murna ganinta bayan ya natsane uwani tashiga ciki ta basu wuri,Ya kalli Haj.Mama yace"Hajiya lafiya irin wannan zuwa..? Ina Fatan wajen Ita Hadizan da Safiyanun duk lafiya suke..?

"Haj.Mama najin haka ta Fashe da kuka tana Fadin"wlh kawu Bala (dayake itama haka take kiranshi) in baku sa hannu arayuwar dan marayan Allah ba Wlh zata kasheshi da bakinciki.." cikin tashin Hankali yace"meya ke Faruwane dashi safiyanun dinne, Hajiya maryam..?

Hajiya mama bata yi jinkiri ba,ta warwaremasa duk abunda ke Faruwa ta karashe da cewa"so nake na nuna yarinyarnan da uwarta sun Tafka kuskure domin sai nasa sunyi kuka da idanunsu"

Kawu bala yayi ajiyar zuciyar yace"Lalle Safiyanu bai yi sa'an mata da suruka ba wlh sam,Haj.Mama tace"wa...?.Tsinannan kenan ai wannan uwar tasu mai kama da ruwan yan duniya itace kesata komai takeyi"

Kawu bala yace"to shi kwamishina yasan abunda ke Faruwa"?Haj.Mama ta tabe baki tace"wannan aie tagama dashi tun yaushe ake fadamai yakasa daukan mataki,mudai da mukasan zafin da'nmu mu zamu nemasa mafita...."Kawu bala yace"to mecece mafita Hajiya Maryam..?

Kai tsaye tace"Mafita ita ce AURE ZAN MASA"....kawu Bala ya kalleta lokaci Daya yana Fadin"Aure kuma Hajiya..?tabashi amsa

" Da kwarai da gaske aure zan nemamasa da wacce tadace da al"adansa da addininsa"kawu Bala yace"To yanzu ina za"asamu yarinyar daa zata dace dashi"?shuru Hajiya mama tayi kan

chan tace"bakomai Allah zai kawo wacce ta dace dashi...Daga haka suka cigaba da tattaunawa.

Gari na wayewa Haj.Mama ta shirya tayi ma gidan Aminiyarta tsinke iyami tayi matukar murna da ganin hajiya mama suka kule adaki suna hirar yaushe gamo acikin hirar ne Haj.Mama take tambayan Safina iyami tace"Safina tazo kun koma kaduna da sati daya,taji haushi inaga shiyasa taki dawowa,Haj.Mama tace"Allah sarki diyata Safina tana chan dai ta kammallah karatun ne?"Iyami tace" eh ta kammallah sai dai kisan diyar taki Hafiza ce bana ita zata wakilci zamfara agasan alqur"ani ta kasa.."Haj.Mama tace"masha Allahu Allah yasa albarka iyami ta Amsa da Amin.

Wuni sukayi tare suna hiransu cikin hirar ne iyami ke tambayan Safwan da iyalansa nan Hajiya ta zayyanemata komai da dalilin zuwanta garin ta kareshe da cewa"wlh iyami yarinyarnan in aka barta da yaron zata iya kasheshi da bakincikinta"iyami tayi shuru tana kallon Aminyarta tana sharen hawaye kan ta jinjina kai tarike hannun Hajiya tace"maryama kidaina kuka kin kawo kuka a inda za'a share miki hawayenki.."

haj.Mama ta saurara tana kallon iyami kai ta gyada mata kan tace"kwarai share hawayen ki muyi mgana"ta share hawayenta tagyara zama tana Fuskartanta.

iyami tayi ajiyar zuciya tace"nidai bani dawata y'a balle in dauketa in bawa Safwan domin sharemai hawaye ko? tafada da sigar tambaya haj.Mama tace"Nasani iyami...Meyasa kikace haka.." iyami taci gaba da fadin"Saboda ina so na kore miki damuwar dana gani a idanunwanki,mezai hana mu Nemamasa SAFINA"

Da sauri Haj.Mama tamaimaita"SAFINA..."iyami tace"kwarai Hajiya ita kadai ce zan iya sharemiki hawaye da ita duk da bani na haifeta ba Nasan mahaifinta bazai ki ba"shuru haj.Mama tayi tana bin iyami da kallo iyami tace"maryama ko..."".da sauri Haj.Mama tace"kar kice komai iyami nakasa mgana ne kingama min komai na rasa dawata kalma zan gode miki lalle Safina itace Hasken dana dade ina gani agidan Sufiyanu Allah na godemaka,iyami tace"babu komai ai yadda safina take awurina haka Safwan yake awajena yaron nan duk sanda sakonsa zai iso Safana dani aciki musamman zai zo ya gaisheni to meye ake nema gun Namiji wanda yawuce wannan Allah dai yasa alheri zamu kullah

Cikin farin ciki Haj.Mama ta amsa,da Amin Amin

*Topha ya kuke hango abun yayi,?zai bada kala?kudai ku biyoni dan kuga yadda badakalar zata kaya*

*Commet and share domin shine abincinmu da gwarin gwiwanmu*

*Janafty..*
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*13*

----Basu samu zama ba sai zuwa dare,dawowar Dr Safwan kenan daga Asibiti yasamu kiran gaggawa,Shiyasa ya Tafi batare da ya Tsaya jin dame Hajiya mama ta dawo ba

Wajen karfe 9:30pm na Dare ya Shigo Gidan Habu mai gadi na barka da dawowa ya amsa cikinn Sakin Fuska kafin ya Nufi Shashen Mommah Saboda Sanin Bakin Hajiya mama akwai mgana

Zaune ya iske su suna mgana yayi sallama suka amsa ya cire takalmi ya kariso ciki Kafadansa Sabe da Lapcoat dinsa kusa da Momma ya zauna yana gaisheta ta amsa tana mika masa Adil

Haj.Mama dake kan kujera zaune tayi gyaran murya tace"Mgnar dana ce zamuyi mganace data shafemu dukkanmu shiyasa naga yakamata na taraku mu tattauna

"kai Sufiyanu mganar duk akankane..."yadago yana kallonta bai yi ba mgana tacigaba da cewa"kwarai da gaske ni wacece agareka? tafada tana kallonsa Da sigar tambaya cikin daure kai yace"ke kakatace wacce ta haifi mahaifina ammh hajiya mai yakawo wannan m....."?Daga masa hannu tayi kan tace tana kallon momma"Na isa in zartar da hukunci a gidan nan Ko Ban isa ba..?

Momma tace"haba hajiya ai dani da babana a karkashin ikon ki muke...Kifadi bukatarki umarni kawai zaki bada insha Allahu zaki samemu masu biyayyah".

Haj.Mama ta rausayar dakai cikin farinciki tace"Masha Allahu naji dadi dama nasanki Hadiza bazan samu mtsala dake ba,zuwana Safana dalinlinkane Sufiyanu"Ta fada tana kallonshi shima dagowa yayi yana kallonta kan yayi mgana ta rigasa dacewa"Matarka tafadamun mganar daya zaburar dani na farka daga barcin daya kwasheni,na tabbata in sakina tafi karfin iyayenta da mijinta to mu d'anmu bai fi karfin mu ba"

tayi shuru kan taci gaba da cewa"Naje da Niyyar Neman Safiyanu Aure ne....""Arazane Dr Safwan yadago yana fadin"Neman aure kuma hajiya"?

yafada da sigar maimaitawa da Tambaya Haj.Mama tamike tsaye tace"Kwarai kuwa.. kuma sai kayi sa'a gidan dattako,ne daga Neman aure kuma aka Dauro Aure"Ras gaban Dr Safwan ya buga momma tace cikin mamaki"aure...Kina Nufin yanzu Babana mata biyu garesa kenan"Haj.Mama tace"ya wuce wai Hadiza ina fatan wannan aure shi zai kawo chanji arayuwar yaron nan" Nan tashiga labarta musu daga farko har karshen abunda ya Faru takareshe da cewa"Ka shirya ranar sati Attahiru ya raka ka kaje ku ga juna ina so ayi ayi tatare ne cikin lokaci"tafada da bada umarni.

Ajiyar zuciya momma ta sauke tana kallon Dr Safwan dayake kallon Hajiya cikin al"ajabi na abunda take Fada cikin sanyin murya yace"Hajiya wannan tatsuniyace ko kuwa dai wasan da kika sabane"?

Harara ta zabgamai kan tace"kai ashe shashashane ban sani ba ana nema maka mafita da yanci ammh kana sakarci ko?to babu wasa matarka SAFINA ta na chan tana jiranka"zai sake mgana Momma ta girgiza masa kai tayi saurin cewa"Alhamdulillah...Hajiya Allah ubangiji ya sa alkhairi aka kullah....Nasan Safina yarinyar kirkice kwarai matuka"

Haj.Mama tawashe baki tace"kwarai da gaske Safina itace daidai da tsarin Rayuwarka,ayanzu haka tana chan ibadan ita ta wakilci jahar su ta zamfara a gasar alqur'ani ta kasa gabadaya"Momma ta washe baki tace"Kai hajiya alkhairi ya shigomana gida wlh....Allah yasa mu amfana da ilimin nata"hajiya ta amsa da Amin

Dr Safwan mutuwar zaune yayi yashiga rudu gani yake kamar amafarki wai ya sake auren wata bayan Sakina abunda bai taba zato ba ko a mafarki baida sha'awar auren mace fiye da daya to dayanma ya yakare da ita balle har yayi Tunanin kari,Haj.Mama ta katsemai Tunani dacewa"baka ce komai ba,ko bakayi murna da alheri dana maka bane"?cikin sanyin murya yace"na isa Hajiya...Allah yasaka da alheri"ta amsa cikin Farinciki dacewa"ko kaifa dan Albarka,Allah yama rayuwarka Albarka ya Sanya Safina abokiyar zamankace"momma ta amsa da Amin mika maka mata Adil yayi kan ya mike ya musu sai da Safe.

Asanyaye ya isa shashensu kai tsaye bedroom din shi ya shiga kan royal bed din dayaji kayataccen zanin gado,yafada zubewa yayi yana sauke Numfashi yakurama saman dakin ido yana tunanin makomar Rayuwarsa baisan dawani ido zai kalli wata mace amatsayin matarshi ba,bawai don yana matukar son sakina ba a"a sai dan gasamasa aya Ahannu da Sakina tayi shiyasa ya cire kowacce mace a lissafi bai ko tunanin kallo wata mace da sunan kallo sha'awa duk halinsu daya yake gani yadade kwance kan ya yunkura yafada toilet,yayo wanka ya dauro al"awala yazo yagabatar da Nafila yadade yana addu',oi kafin ya koma ya kwanta wanda har barci ya kwasheshi bai tantance wani hali yake ciki ba shi dai ba haushi yake ji ba kuma ba murna yakeyi ba

Asuba tagari Dr S S Safana

_*TEAM SAFINA_😍

_*TEAM SAKINA💞_

*Anitha...*

commet
share
And
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

_*Hohoho ur Durling Safeena Aliyu zurmi tace karkuji komai,kawai ku bata lokaci tayi alkwarin chanza Rayuwar Dr S S Safana....iz juz d begining guyzs*_

*14*

----Koda garin Allah ya waye har saida Dr Safwan ya makara kafin ya tashi shima Dr Tahir ne ya ishesa da kiran kan ankawo musu emergency ,yayi mamakin barcin daya sha wanda rabonsa da irinshi wlh bazai iya tuna waba( lalle Safeena ke haskece arayuwar Dr S S Safana)cikin gaggawa yayi wanka ya shirya cikin suit masu rowan toka samfarin DKNY agurguje ya shiga shashen su momma ya musu sallama suka rakasa da sa albarka.

Wata matace aka kawo zata haifi yan uku to biyu sun danne daya kuma suna kokarin turo kai atare gashi karfin uwar yafara karewa zuwan Dr Safwan cikin kwarewa da taimakon Allah ta haifi yaranta cikin salama da kwanciyar Hankali yan"uwan matan sun matukar jinjinama Dr Safwan ganin yadda tun dazu likitoci ke kara kaina akanta bata haihu ba ammh yana zuwa cikin mintin da bai gaza goma ba ta haihu hakika sun yaba da jajircewa irinta Dr Safwan Sale Safana

wanda har sai da suka Furtamai.

Aranar Dr Safwan ya wuni aiki a asibiti operation uku yayi duk agajiye yake komawarsa office kenan ya bude karamin fridge din dake office din ya ciro ruwan faro ya kafa kai sai daya sha fiye da Rabi kana ya ijiye kan kujeran office din yafada yana maida Numfashi.

Dr Tahir ne ya turo kofar office din ya shigo ya kariso yana kallon Dr Safwan dake kwance idanunsa a lumshe duk da yasan ba barci yake yi ba file din daya shigo dashi ya ijiye kan yace"Dr Safana wai meke Faruwa ne yaudin nan naganka kana wani annushuwane"?Dr Safwan yanajinsa yayi masa shuru sai chan yace"Kai fa mugun dan sa"ido ne wlh Tahir"Yafada still bai bude ido ba.

Dr Tahir ya kyalkyace da dariya kan yace"My man...ai indai kaine to momma ce kawai zata Fini saninka common gist me "Mirmishi Dr Safwan yayi kan ya Mike Zaune yana Fadin"Zan yi gisting dinka ammh ba yanzu ba but it only i know yau ina jin yanayi na yana canzawa i dont know may be wani abu something zai Faru dani ne"Dr Tahir yayi galala yana kallonsa cikin farinciki kafin yace"Ko dana ji Dr Safana Dan Allah shafamin nasan komiye yasakaka Annuri yau iz sometin special".

Mikewa Dr Safwan yayi kan ya isa kan teburin dayama office din kwanya yana Fadin"Tsiyana dakai wutar ciki,ba ni nace ba"yafada yana kallonsa tare da dagemai gira guda daya Dr Tahir yace"Sure my Dr nakosa ne"Dr Safwan ya zari wani fayal yana wucewa yace"Nafasa kasan ban san damu"Da sauri yace"Srry..Nadaina damunka but karkajamin rai"Tsaki Dr Safwan yaja kan yace"in kafito ka rufemin office din Aku"Dariya Dr Tahir yayi kan yace"Bakomai indai za"a bani Ibr,daga haka ya fada toilet din office din shikuma Dr Safwan ya Fice.

Hmmm Su Dr Safwan tun yanzu tunma baku hadu da Safinar ba kafara zakewa

*******

*Zurmi...*

---Masha Allahu kwanansu Safeena hudu suka dawo jaharsu ayayin da jahar Zamfara tazo na

biyu,Hakika Safeena ta godema Allah dayasa iyayenta suka tsaya akanta tasamu limi yau dalilin ilimi tasamu kujerar makka harda motar hawa golf da zunzuruntun kudi har dubu dari biyar tayi kuka,kukan Farinciki da zamowarta wurin dabakowa ke takowa ba sai wanda Allah yabama limi da basira,haka suka dawo cikin Farin ciki kudi dai mkrantansu ta mallakamawa kujerar makka kuma Abbanta ayayinda motar tace Abbanta yabada adinga mishi haya,Hakika Ummi taga Ranar Haihuwa domin makota da yan"uwa da abokan arzika sai shigowa suke tayasu murna,suna cikin amsan baki shyasa Abbah bai samu kebewa da Safeena ba sai da tadawo da kwana uku kana.

Cikin dakinshi yakirata bayan ya yi godiya ga Allah subuhanahu wata'ala daya azurtasa da samun ya irinta,yayi mata Nasiha mai kashe jiki har sai da ta Fitar da kwallah kan ya gangaro kan zence yace'Safeena kinsan dai bazan cutar dake bako?"Yafada yana kallonta gyada kai tayi kawai jikinta yagama Sanyi fatanta Allah yasa bawani abu yafaru ba bayan batanan ba.

Yacigaba da cewa"to duk abunda zan Fada miki ki daukesa matsayin kaddara..Kina gabda tafiya gasar nan na daura miki aure"Dam!dam!gabam Safina ya buga tadago da sauri cikin Rawar murya tace'Aure kuma Abbah'...?kai tsaye yace'Kwarai Safina...Na daura miki aure sati biyu da suka wuce da jikan Hajiyar Safana"yafada yana ciro sadakinta ya kama Hannunta ya Damkamata,Safina taji hawaye ya wanke mata Fuska tana so tayi mgana ammh kuka yaci karfinta mallam Aliyu ya kalleta yaji tsausayinta ya tsirgamasa yace cikin taushin murya"karki ce komai yata Allah yayi miki albarka Safina Ubangiji ya jibanci lamarinki yakuma zaunar dake lafiya agidan aurenki"yafada yana kauda kai kwallah tataru a idanunsa,Safina tayi karfin halin cewa"Hakika Abbah kai yafi chanchanta daka zabamin mijin daya dace dani,na karbi auren nan hannu bibbiyu sai dai ina rokonka dan Allah Abbah kutayani da addu'a Allah ya bani juriya da hakuri"takareshe fada tana kara tsananta kukanta Abbah yace"tashi kije yar albarka da izinin lahi bazaki tabe ba Safina"cikin sanyi ta mike rike da kudin tace" Abbah karike kudin"girgiza kai yayi kan yace"A'a Safeena Hakkinki ne ki mikama Ummanki ta adana miki kan muji daga mijin naki.Kada kai tayi kan tafice tana sharan hawaye.Runtse ido Abbah yayi yanaji har aransa kamar bai kyauta ma Safina ba Sam.

*Shakira..*

Commet
Share
And
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*15*

----Tana isa daki tafada jikin Ummi dake zaune gefen gado,tafashe da kuka Ummi tariketa tana fadin"Ya isa Safina kidaina kuka haka Allah ya kaddara kinsan bawa bai isa ya gujema kaddararsa ba"

Safina tadago tana kallon fuskar Ummi da dan hasken makarfin daya dan haske dakin fuskarta shabe shabe da hawaye ta hade da majina,cikin dashashiyar murya tace"Ummi...Yazanyi da Mallam yahuza,da sonsa yafara samun gurbi azuciyata?

Ummi tace"Hakuri zakiyi Safina shine mafita kawai"Tsuru mata ido tayi tana kallonta hawaye suna kwaranya tace"Ummi taya zaku auramin wanda baku sani ba,bakusan addinin saba balle al'adansa ba,Ummi meyasa? takareshe tana kara fashewa da kuka.

Ajiyar Zuciya Ummi ta Sauke kan tazaunar da Safina kan gadon tamike tana cewa"Hakane...Ammh bakin alkalami yariga ya bushe Allah yaga zukatanmu Badon komai muka bada ke garesu ba sai dan Amanar dake tsakaninmu da Hajiya mama shekara da shekaru bazamu iya ture bukatarta ba"Safina takara jan majina tace"Ummi....Dakata"Ummi tafada tana tsaidata da Hannu kan tacigaba da cewa"Kada fa bacin rai yasa ki manta

matsayinmu agareki,munada daman zaba miki mijin daya dace dake...Ki dawo cikin Hayyacin ki Safina ki mika lamarinki ga Allah shine zai taimakeki.

Daga haka tasakai tafice cikin tsausayin yarta mafi soyuwa aranta,tana Fita Safina tafashe da kuka mai cinrai ta sulale kan gadon tana kara volume din kukan,ashe ashe shiyasa mallam yahuza ranar da suka dawo yana mata murna yaki kallon cikin idanunta in baza ta manta ba har kwallah tagani kwance cikin idanunsa,Allah sarki mallam yahuza ashe an rabamu ne wayyo Ni Safina ina zansa kaina"tafada tana kara fashewa da kuka kara dunkulewa tayi tana cigaba da kukan rashin madafa.

Haka Ummi ta tarar da Abbah cikin alhini dataga yadamu ita tadinga kwantar mai da hankali har yadan ware kadan.

Koda gari ya waye Har Abbah yafita kasuwa Safina bata Fito ba yasan zataji badadi shiyasa yace Ummi tabita Ahankali haka yasakai yafice cike da tsausayin yarshi aransa,sai wajen goma Safina tatashi idanunta sun kumbura kanta yamata Nauyi dayake tana Fashin sallah wanka tayi tashirya cikin wani jan material dinkin doguwar riga fuskarta ko hoda bata sanya ba ta fito ta tarar da Ummi A kichen tana gyaran wake tasanya Hannu zata karba Ummi tahanata tadago idanuwanta dasuka kumbura tace"Ummi...Ki.."Bani zaki ba hakuri ba Safina mune zamu baki hakuri dan mun bata miki"Tafada kanta tsaye daga gani ranta abace yake Safeena ta durkusa tace"Dan Allah Ummi ki yafemin wlh baran karaba"tafada hawaye suna zubo mata Ummi ta ijiye waken ta riketa ta data ita tsaye tasa hannu tana share mata hawaye tace"Shikenan Safeena kar ki kara irin wannan...Abbanki da damuwarki yafita inbaki bashi gwarin gwiwa ba yakike so yayi ehe?

"Safeena tarike Hannu Ummi tace"Naji Ummi kuma insha Allahu zaku sameni mai biyayyah agareku"Ummi tace'ko kefa diyar albarka kisaki ranki kinji...Ubangiji yasa albarka Arayuwarki kinji yata"Tafada tana matsa kumatunta Dariya Safeena tayi har hakoranta  suka bayyana tace"Nagode Ummi nagode daya kasance kika zama uwa agareni"Ummi tace"Nima haka Safeena na.

Daga haka suka cigaba da aiki suna hirarsu har lokacin da Usman yadawo daga mkranta,koda Abbah yadawo yaga yadda Safeena tasaki ranta ransa yamasa dadi yaji kaso dayawa na

damuwarsa yaragu yadinga sa mata albarka har sai da tafitar da kwallah na tsausayin iyayenta hakika in bata musu biyayyah ba data tabe duniya wa lahira.

•••••••••••••••••

*Kaduna...*

Haka Dr Safwan yadinga janma Dr Tahir rai shikuma yaki Hakura ranar dai suna cikin mota Dr Safwan ke tukawa zasu koma gida Dr Tahir yabiyosa zai gaidasu momma Dr Tahir ya kallesa yana driving ammh hankalinsa na wani wuri,Dr Tahir ya tabasa yana cewa"mr man...Wannan dogon Nazarin naka wai yaushe zai kare ne?"Mirmishi Dr Safwan yayi hankalinsa na kan titi yace"har Abada Tahir...Bansan yaushene zandinga hango kaina amatsayin cikakken Namiji ba"Yafada muryansa na bayyana Rauninsa.

Dr Tahir ya kallesa cikin tsausaya kan yace"verry soon Abokina...Allah nasane dakai kuma inaji ajikina kamar komai yazo karshe"Dr Safwan yayi mirmishin gefen baki yace"Kaji wata chakwakiyar da Haj.Mama takara jefani wai Aure tamin"Zuru Dr Tahir yayi masa yana kallonsa shikuwa yasan yana kallonsa dat why yaki kallonsa.

Cikin mamaki Dr Tahir ya maimata"Aure...Wai Aure na gaske kona wasa?"wai na gaske"kai tsaye ya basa Amsa kan yacigaba da cewa"shine mganar danace zamuyi tun last week aie...Yatabe baki yace"Kasan ma har an daura auren wai" wani uban ihu Dr Tahir yasa har saida Dr Safwan yaci burki yana binsa da kallo.

Cikin matukar murna Dr Tahir yace"Ehyyyyyyye.....Dis iz juz d begining abokina,Wlh wannan mganar kara aure tuni ke Raina kawai saninka ne yasa nakasa kawo maka wannan shawaran.Kai Haj.Mama tagama min komai wlh"Yafada harda buga kafa Dr Safwan yabuga tsaki yace"Mtewwww...Kai fa wlh dan juju ne to meye nawani ihu"Dr Tahir yace'eh naji...Nidai

yanzu ina amaryan take infact ma ya'akayi duk wannan abun cikin gaggawa,Dr Safwan ya zabgamasa harara yace"Gata goye abayana uban yan tsegumi.." Dr Tahir ya sheke da dariyar shedanci yace"Kace komai abokina lokacinka ne nawa nanan zuwa wlh sai ka raina kanka yaro"Yafada yana zunguran kafadansa,Banza yayi dashi yacigaba da tukinsa.

Suna isa sai da Dr Tahir yakara kular da Dr Safwan chan ya barshi gun Habu mai gadi yana tsinannan surutunsa ya isa shashen su momma,Hajiya ya tarar afalon tazuba ido tana kallon talabijin a tashar  Arewa 24 sallama yayi bata ji ba kawai ya girgiza kai ya wuce dakin momma ya tarar da ita tana goye da adil tana gyara kaya acikin wardrope,da sallama ya shiga ta amsa tana masa maraba da dawowa ya amsa yana fadin"Momma sannunku,da gida"ta amsa da cewa"Yauwa..Babana yawajen aikin"?ya amsa da Alhamdulillah yana tambayan Adil yayi barci ne tace"eh..Yanzu yayi,ficewa yayi yana fadin"Momma kizo ku gaisa da Tahir yazo gaisheku",daga haka ya fice.

Yana fitowa ya tarar da suda guda biyu Hajiya.Mama da Tahir sun kacema da hira dama mutunintane,kan kujera ya isa yazauna yana Fadin"Hajiya ikon Allah"tace"kwarai yaro nan gani nan bari wlh"Dr Tahir ya sheke dadariya yana Fadin"dole abar Hajiya domin bamai iyawa dake tace"wane mutum Attahiru bawanda ya"isa ne ma"'mirmishi kawai Dr Safwan yayi yafito da wayarsa yana latsawa,momma ta fito suka gaisa kan tashiga kichen zata zubo musu abinci,nan fa Tahir ya gyara zama yace"Hajiya ashe abun alkhairin daya samu abokina kenan?"Haj.Mama tace"Kamar wanne kenan Attahiru..,? yace'Na aure mana"haj.Mama ta washe baki tace'au ashe yagaya maka dan nema ninan dana fadamasa fuskar shanu yamin tundaga ranar ina lura dashi ko kallona baisan yi"tafada tana Nuna sa da baki Dr Tahir yayi dariya yace'ai Hajiya Allah dai ya biyaki da aljannah abunda kikayi yayi dai dai ko Allah yasa yadace wannan karon"Haj.Mama tace cikin jin dadi"Amin..Attahiru shiyasa nake sonka da fahimta...Nan Hajiya ta fede masa biri har watsiya ta kareshe da cewa'Nasan wannan Auren Alheri ne shiyasama nakeso cikin satin nan kuje ku ganta nasan zakuga abunda nake fada muku"Tahir yace"Insha Allahu zamu je hajiya karki wani damu.

Dr Safwan ya tashi yana cewa"ubanwa zaije dakai....Karma kasa rai",Dr Tahir yace'oho.....Haji.Mama tace"Uban wanda yayi mganan tafada tana mai dakuwa'kan tace kagamin ja'irin yaro fitsararre to ubanka zai je dashi'Hanyar fita yayi yana Fadin"kidaina

zaganmun uba"Tace"Allah...Habule to zoka dakeni ance Ubankane🤣🤣tafada harda mikewa ficewa yayi yana kunkuni tace"Dawo rasa kunya in nuna maka karyan tsiya kake"tana wani rike kugu,Dr Tahir yana ta kwasan dariya,momma takawomusu abinci ta ga ba Dr Safwan tace'Ina babana yayi ne Haj mama tace'Rashin tarbiya yagwada min na numasa nima A ce🤣"momma tayi mirmishi kawai nan Tahir yaci dambun zogale yayi nak kana yamasu haj.Mama sallama ya wuce.

Shashen Sakina ya shiga yako iske hakiman zaune afalo ta hakimce ana ta zuba lissafi,adakile suka gaisa yake tambayanta Dr Safwan dabaki tanuna masa dakinsa yako wuce yana zolayarta da"Hajiya madam tamu"da harara ta bisa dan taga zuwansu tundazu shine sai da yagama gulmarsa zai zoyana mata  wani rawar baki to daga shi har abokin nasa dai dai take dasu🤔

Koda shigansa dakin kwance ya tarar dashi kan gado atsaye Dr Tahir ya tsaya kan yace',plz serious mr man yaushe kake ganin zamuyi tafiyar nan?"banza yayi masa har saida ya fidda rai da zaiyi mgana kan yace"Dis coming weeked nake sa rai daga haka yajuya baya Dr tahir ya fice yana cewa"As u wish Sir...Nina ware,daga haka ya fice.

*Anitha...*

Commet
Share
Vote
Like
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*16*

"Ranar lahadi tun Safe Dr Tahir yayi ma Dr Safwan sammako,Shima Dr din yasan Halin Tahir din da wutar ciki dat why ya shirya da wuri,Dama gashi jiya da daddare kwana sakina tayi bala'i haka kawai yana Zaune adakinsa yana wani aiki a laptop dinsa ta shigo ta sameshi tace tana son mgana dashi don Sakina bata da kunya wai tafaramai complain yana wulakantata yadaina kulata kana yadaina bata Hakkinta na Aure abun haushi abun takaichi yaji wani bakinciki yayimin shar arai yaso yamata mgama ammh sai ya tuna Neman shiri take shikuwa yayi alkwari nuna ma Sakina shi cikakken Namiji ne _yauwa Namijina_

Kwashe laptop dinsa yayi ya fice ya barmata daki dayan bedroom din ya shige dayake 3 bedroom ne yasaka key cos yasanta yar hayaniyace sai ta samai ciwon kai,aikuwa taita bala'i hartana Fadin dole dai Azauna da ita don babu yadda aka iya da'ita mirmishi yayi aransa yana auna girman rainin da Sakina tayimin lalle kuwa tayi kuskure inhar take Tunanin tafi karfin shi ne kawai kyaleta yakeyi cos darajar mahaifinta ammh shi tuni tagama Siremai da munanan halayyanta shifa baida darajar da Sakina zata fita tafadamai sai dai yazo yaga bata gida,baida kimar da zatayimai abinci balle sauran abunda ba'a rasa ba, ji bi yadda Adil yarasa gatan ta ammh ko ajikinta ko nono sai taga dama in momma ta roketa ta bashi,to har wannan macece,shiyasa yadau ma kansa Nuna mata *TA TAFKA KUSKURE*

Cikin Wata shadda gezner deep blue ya shirya jamface zanna bukar ce bisa kansa itama da zaren blue akayita takalmin kafansa rufaffene na fatar Damisa,baki yafeshe jikinsa da turarensa Azzaro visit Kansa yadau gyara abunka ka mai kyau sai yafito yabada wani sirrin kyau wanda ba kowa ke ganewa ba sai wanda akayi dominshi.

Ko takan Sakina bai bi ba,tana dakinta ta kwana da takaichin wulakancin Da Dr Safwan yamata kuma tayi alkwari kafin ya Fita sai yagayamata meye matsayinta agidan dayakemata halin ko inkula _Topha lalle Sakina kunya bai ishe ki ba_🤔

Sashen Momma ya tarar Da Dr Tahir shima ya Shirya cikin shadda fara wagambari shima cikin dikin muhammd shima zannah bukar din yadora kafarsa shima cikin sawu ciki bakake Sororo yayi yana kallonsa tun shigowarsa momma Dake zaune gefe ita ta tsurama danta ido tana kallon yadda danta yau yake Fitar dawani hasken Annuri na dabam Haj.Mama dake tsaye gefe tasaki guda" Ayyiriri.....!!!!Masha Allahu Safiyanu lalle kanunamin kai jinin justice Habule ne,

Dr Safwan yayi mirmishi kan ya karisa ya duka yana gaida momma ta amsa tana Dafa kansa tace cikin farinciki"Babana nadade ban ganka cikin Annuri irin na yau ba'sunkuyar dakai yayi kan yace"Momma...Bbu komai wlh'tace"unhum...Fadamin gaskiya ko duk murnan zuwa ganin surukar tawace?"tafada tana dago kansa da hannunta,Mirmishi kawai yamata baice komai ba domin shima mamakin farincikin daya tsinci kansa yakeyi ayau din.

Adil dake Hannun Dr Tahir ya amsa yana cillasa sama yana Fadin"Bawan Allah damo sarki hakuri...Zaka bini ne"yafada kamar yana jinsa Haj.Mama tace"Bawan Allah yakusa samin uwata gari ba wacce tambadaddiyar ba"Tafada tana nuna shashenta da Baki Dr Tahir"Yayi dariya yace"Allah barmana Hajiyarmu"Tace"eh...Kona ga karshen tazurancinka ba" tafada harda mele masa baki,dariya yayi kan yace"Haba Hajiyarmu verry soon za'ayi"tace"kai kasan wani vari san ince dai ba zagina kayi ba..?😂😂😂Yace yana Rike baki"Wane ni Tahir"tace"Au na'aza zagina kayi wlh in ci ubanka domin ni ban yadda da wannan gwarancin naku ba"Tafada tana harare harare dariya sukayi gabadayansu

Har wurin mota suka rakosu Haj.Mama na jaddadamusu cewa su fara bi Safana Iyami ta hadasu da wanda zai kaisu zurmin kar suje su bace ko yan kiddappers su sace su😂😂.

Koda tara tayi suna Safana dayake da benz din Dr akayi Tafiyan sai da suka fara biyawa gun kawu bala suka gaishesu yayi murna da ganin Dr yayi mai Nasiha sosai kan yarike wannan aure da hannu bibbiyu saboda yarinyace data Fito yar babba gida,Jikinsu yayi Sanyi da Nasihar

kawu kuma daman shi baija da wannan aure cos har aransa baiji Haushi ba saima wani Annushuwa.

Iyami sai dai taga su Dr Safwan kwatsam taita ina tasaka dasu basu wani jima ba tahadasu da dan kishiyarta manu tace yakaisu gashi anyi ta neman mallam Aliyu awaya Afadamai ba'a sameshi ba gashi ita Ummi bata da waya balle Safina.

Karfe10:30 suka Dau hanyar Zamfara sai muyi Fatan isarsu lafiya.

*****

*Zurmi..*

Yau tun Safe Safeena taji gabanta na Faduwa bata kawo komai ba tayi addu'a taci gaba da sabgoginta,tana kammallah aiyukanta tayi wanka ta shirya cikin bakar doguwar riga da farin hijabinta har kasa da safa ta daura Nikabinta ta Fito tana Ma Ummi sallama kan zata  Duba Aisha bata jin dadi Ummi tamata adawo lafiya.saboda taji dakyar Abbanta yabarta fita dan tunda tadawo bata sake fita ko'ina ba saboda akwai Hakkin wani akanta.

Tafita badadewa Ummi tana bakin kichen tana tsinkan zogale domin shi yau mallam yace yana sha'awa wato tuwon shinkafa miyar zogale kawai taga Manu ya fado da gudu manu dai bazai wuce shekara tara aduniya ba sa'an Usman ne Ummi ta saki tsigan zogale tana Fadin"Kai Manu daga ina? kuma kai dawane? ajere ta jefamai tambayoyin haki yakeyi kan yace'goggo

Iyami ce tace na kawo wasu baki"Ummi tace"Baki..Kuma"Ta maimata da sigar tambaya.

Manu yace'eh...Tace mijim yaya Safeena ne"Ummi ta mike dafe da kirji tace mijin wa?"tafada tana zaro ido yace"Mijin Yaya Safeena tace"Ummi tayi daki da Sauri tana fadin"na shiga Uku ni zainabu zuwa ba shiri😂😂Ummi ta rude taji zuwan siriki.

Hijabi ta yaya tasanya kan tajawo tabarma ta Shimfida kan shararran simintin dake tsakar gidan tana Fadin",Maza manu ce su shigo.Yako ruga da gudu ya fice yana murna yasha dadin mota.

Suna tsaye ajikin motar Dr Safwan yana bin dan gidan su Safeena da kallo aransa yana fadin"wai daman akwai masu rayuwa a irin gidan nan" _Tab...Lallenema Dr to dankai kana gida mai kyau sai yazamana kowama hakane_

Shiko Dr Tahir anguwan yake bi da kallo dagani dai anguwan ta masu rufin asiri ce ba'a fadi dayan ba kofar gidansu Safeenar agyare tsaf dashi  aransa yace"Tab....Nan gidan kuma Hajiya mama takawomu" _Kaniyarka Tahir Gidansu Safeenar kake zagewa_😛

Suna zencen zucci ne manu yafito da gudu yana fadin"ance ku shigo"Dr Tahir yakalli D Safwan yace"to bismillah...Kaine maigidan aie"yafada yana dariya kasa kasa Harara ya wurgamasa kafin ya wuce ya rufamasa baya da sallama suka shiga abakinsu Ummi dake kofar daki ta amsa kanta na kasa tana masu maraba dukkansu zubewa sukayi suna kwasan gaisuwa Ummi ta amsa tana tambayan su Hajiya Dr Tahir ya amsa da "Suna gaisheku"

Shuru ya biyo baya Ummi kunya yahanata daga kai shikuma Dr Safwan tagefen ido yake bin gidan da kallon duk da dai talakawane ammh suna da tsafta ko'ina ashare shima Dr Tahir hakane ammh aransa fadi yake"Kar dai ace Wannan babar itace Safeenar😂😂😂,cikin kunya Ummi tace"Ku zauna kan tabarma bari insa asiyo muku ruwan sanyi' ciccire takalmansu Sukayi suka zazzauna kai aduke Dr Tahir sai dariya yakema Dr Safwan kasakasa shikuwa yanajinsa yama sa banza.

Ummi ta shga daki takwalama Manu kira yazo tabashi kudi tana fadin"Kasan gidan su Gaddafi...?ya amsa da eh tace to maza hanzarta kaje yaya Safeena na gidan kace ta yi hanzari tadawo inzaka dawo ka biya shagon basiru kasiyo min ruwan gora guda biyu.

*Shakira...*

Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

_*Dedicated to my wattpadians Fans and my Whatsappians Fans ina ganin sakonnin Fatan alheri da Addu"o'inku Allah ya saka da Alheri Tanque so much Allah ya bar Kauna da zaman Tare Ameen..*_

*17*

Yako zura da gudu ya fita Ummi tace"'oh ni Zainabu Allah dai yakai Ipy...",gashi tana so tamusu bayanin Safeenar tadan fita zuwa gaida kawarta,ammh kunya ya hanata Fita,uwa uba kuma tana son komawa kichen domin tadora miya aranta tace bari Safeenar ta shigo su dawo daki inba haka ba Takurani zasuyi oh ni Ummi kunya🤔

Manu kuwa da gudu ya shiga gidansu Aisha mamansu Aisha tace'kai daga ina?"yace"Ummi ce

tace Yaya Safeena tazo yanzu"Maman Aisha tace"Tom gatanan zuwa kara fice yayi yanufi shago siyan ruwa,itakuwa maman Aisha lekawa tayi dakin da su Aishan ke ciki tace"To iyayan daka kufito kusha iska ke Safeena Ummi ta aiko kije yanzu"Safeena ta mike da sauri tana Fadin"To lafiya...Dan Ummi bata taba aikomin ba"Maman Aisha tace"Nima dai..Ki hanzarta komeye mai mahimmacine kam"Hijabinta ta sanya saboda sauri Nikabin ahannu ta rikoshi.

Tana tafe ahanya tana zencen zucci Allah yasa lafiya domin yadda gabanta ke faduwa tun safe nan da nan ta kawo dayake babu tazara Daga gidansu zuwa gidansu Aisha, taga mota akofar gidansu ammh ko alama bata kawo gidansu tazo ba tasan dai bawani mai zuwa amota balle tasa rai _Allah sarki Safeena to yau gashi mai motarma mallakinkine_

Da siririyar muryanta tayi sallama tasawo kai cikin gidan,kanta na duke shiyaasa bata lura dasu ba ammh kamshin Turaren Dr Safwan ya cika tsakar gidan,da hadaddun takalmansu tafara cin karo  binsu da  kallo  take cikin Mamaki,har zuwa mamallakan takalman idonta yafara Sauka kan wani hadadden Namiji fari mai cikar zati da kamala da haiba mai dauke da doguwar fuskar sajensa ya zagayen bakinsa wanda yakaramasa kwarjini hakiki Allah yayi Halitta Anan gurin sai akayi sa'a tun lokacin da Dr Safwan yaji muryan Safeena cikin sanyi da natsuwa tayi sallama yaji muryan tadakesa yayi saurin dagowa ya zuramata ido yana binta da kallo daga sama har kasa yakasa dauke idanunsa daga kanta duk da babu abunda zai dora da kamanninta ammh zuciyarsa da gangar jikinsa sun Fada masa cewa wanna ce _*SAFEENARSA_ kaji Dr S S Safana wai Safeenarsa🤔

lokacin da idanuwansu suka hadu wani marganet ne yajasu dukkansu Safeena ta tsinci kanta awani yanayi na mutuwar jiki da sauri ta sadda kanta kasa jikinta ya cigaba da rawa kafafunta Sun kasa daukanta Dr Tahir ne yayi gyaran murya saboda yaga yadda Safinar ke gabda faduwa.

Waskewa Dr Safwan yayi yacigaba da latsa wayarsa ammh zuciyarsa na fat Fat kamar wanda yayi gudun famfalaki DrTahir yayi karfin halin cewa"kari so mana malama Safeena"cikin rashin kuzari Safeena tadaga kafa ta kariso sai data danganta da kofar dakin Ummi kana tace cikin rawar murya"Sa....sannunku da....Da zuwa"Yauwa Sannu Dr Tahir ya bata amsa yana kara kallonta yadda Hijabin yake wani zumbudede dashi harda Safa duk da kanta na duke adan kallon dayamata yafahimci yarinta karara atare da ita.

Tana cewa haka tafada daki da gudu tana Haki Ummi tayi Saurin mikewa tajawo hannunta suka shige kuryan daki tace"Safeena mijinkine fa suka zo"sororo Safeena tayi gabanta na tsananta Faduwa tace"mi...Mi...Mijina kuma Ummi..?"Ummi tace"Eh....Nima kwatsam na gansu kinga bbu lokaci na aiki Manu siyo ruwa shuru bai dawo ba bari ni in je inji da abinci da za"a musu,kekuma ki koma gurinsu"Safeena tace"Ammh..Ummi"Ke wai wata irin shashashace ko bakiji menace miki bane,"Ummi tafada ranta ya baci"Safeena tace"yi Hakuri Ummi zanyi yadda kikace daga haka tafice tayi tsaye afalo hannunta dafe da kirji tanajin zuciyarta nawani harbawa.

Sukuwa tana shigewa Dr Tahir ya zunguri Dr Safwan yana Fadin"Kai mijin malama kako ga malamartaka i think fa itace Safeenar"Banza dashi Dr Safwan yayi sai dannan wayansa yakeyi,ganin haka yasa Dr Tahir kama kansa agurguje Safeena tadan kara gyara falon ta shimfida musu darduma kan ledar dake tsakar dakin,cikin sanyin jiki ta leko da kanta tace"ku shigo ciki kuna zaune awaje"Dr Tahir yace"a"a ayi Haka ranki yadade"mirmishi tayi kawai atare suka mike Dr Tahir ne yafara shiga da sallama kana Dr Safwan wanda Safeena ke tsaye akofar dakin har yanzu suka zauna,ita dai Safina kanta aduke takasa motsi  Dr Tahir yazauna yana Fadin"Masha Allahu..Amarya baki tambayi wanene angon naki ba"yafada yana kallon Dr Safwan dashima yawani sadda kai

Wuf ta fice tana Rufe fuska dukkansu suka bita da kallo Safwan yanajin wani iri aransa kunya tab to shi ina ma Sakina takeda kunya balle ayi mgana taji kunya,mirmishin gefen baki yayi yana bin inda tabi da kallo.Dr Tahir sai kallonshi yake yana mai dariya kasa kasa.

Ummi ta fito itama cikin kunya suka kara gaisawa kana tafice ta tararda Safeena zaune a kichen tayi tagumi Ummi ta kalleta tace"Ke kam Allah yayi miki Sauki...'Safeena tayi saurin mikewa tana rufe fuskar Ummi tayi dariya kan tace"Allah ya shiryeki..Kinga nifa tuwon shinkafa nakeyi miyar zogale ya kike gani za'a sake yi musu wani Abun ne..?Safeena tace"Ki barshi Ummi wlh sai kiga sunfi son tuwon ma "Ummi tace"ok sai na musu zobe su hada dashi,maza ki koma gurinsu niban ma gane surikin nawa ba duka yaran masha Allah.

Ummi tafada tana dariya mirmishi Safeena tayi kan tafice tana fita manu yakawo ruwan swan din guda biyu ta amsa ta sanya cikin faranti tahado da kofuna da sallama tashiga suka amsa,ta

durkusa ta ijiye Tahir na mata sannu da aiki tadauki kofi tana tsiyaya musu Dr Safwan yana kallon ta ta wutsiyar idanunsa aransa yana jinjinama Hajiya mama ita aganinta wanna ficilar yarinya ne zata iya dauke Nauyinshi tab shi atunaninshi duk randa ya haikemata zata iya Mutuwa _see dis guy to ka gwadane_🤒

Gefe takoma bayan ta zuba musu ta zauna akasa kanta a duke tana wasa da yatsun hannunta kowani dakika na mintina zuciyarta na bugawa,Dr Tahir yasha ruwa yana fadin"Munsha ruwan Amarya.."Yafada yana mirmishi kan ya cigaba da cewa"an dawo lpy kuma nanawa aka ciyo mana...?"ta gefen ido take kallon Tahir kan tace cikin sanyin muryanta"Na biyu nayi...Lafiya kalau"Yace"Wow..Masha Allahu lallai kin cika Hafiza"Mirmishi kawai tayi Tahir ne keta janta da mgana tana bashi amsa da umh a"a shikuwa Dr Safwan yana ta danne danne awayarsa ammh hankalinshi kaf akansu yake lokaci kankani yaji yarinyar ta burgesa yadda takeda aji da kamun kai.

Mikewa DR Tahir yayi yana Fadin"Bari na baku guri ku zanta.."yafada yana ficewa Safwan yarakasa da Harara,yana waigowa karaf suka hada ido tayi saurin sadda kai kasa mirmishi yayi yasamu kansa da kuramata ido kur yana kallonta jikinta yabata ana kallonta tana dagowa idanunwansu suka sarke ma juna,wani miracle ne ke aiki atare dasu kamar ansa super glue an manne musu sun kasa daina kallon juna.

Safeena taji jikinta na saki da wannan azababban kalon da Dr Safwan ke binta dashi ita tayi saurin jaye idanunta saboda bazata jure wannan kallon daga Dr ba,jikinta yana rawa takara dukar dakai tana kara jin bugawar zuciya.

Dr Safwan kawai yaji yasamu kansa da cewa"An dawo lafiya...?Allah yasa albarka"cikin husky vioce dinsa ya furta haka tadago tana kallonsa aranta tana fadin"So sweet.."Tace"Alhamdulillah nagode..Daganan shuru ya biyo baya Ammh lokaci bayan lokaci suna satan kallon juna,sai suyi mirmishi atare.

Shikuwa D Tahir yana chan yatasa Ummi da hira ita kuwa haka takeso mutum mara bakunta tana bashi Ibrin amintar Haj.Mama da iyami shikuwa yanata jinjina girman Amintansu.

Abun Mamaki saiga Dr Safwan yana abunda bai sababa wato mgana sai gashi wai Safeena Ta chanzashi da surutu yana tambayanta kan matakin karatunta tundaga na boko har na arabi yayi mamaki na yadda karamar yarinya kamar Safeena take da ilimin sanin littafan addini haka gaskiya ya jinjinama iyayanta matuka,tadan Sake dashi sama sama ammh ita aranta mamaki take wai yau itace ta mallaki miji iri Dr Safwan miji na Nuna sa'a wanda ko wacce mace take fata ta mallaka amtsayin miji duk ko takamarta da nasabarta da ikonta kallon daya zatamai taji ta raina kanta da duk abunda ta mallaka kuwa.
salla kawai ke tadasu.

Tabbas su Tahir basu Nuna bakunta ba suka zage suka ci tuwonsu Dr Safwan yaji dadin cimar saboda abincinsa duk miyar da akayita da ganye masoyiyarsa ce ga lafiyayyah zobonsu wanda tas suka shanye suna hamdala da wannan gidan irin albarka,saboda dadin Hira basu ankara ba sai da Tahir yaga shida Saura yaleka su Safeena yana cewa"plz amarya ama na hakuri hakanan kada muyi dare a hanya"Safeena tayi yar dariya tace"To ni na rikesa"Dr Tahir yace"kece mana to inbake ba To waye"..?Yafada yana kallonta hannu tasa ta rufe fuskarta Dr Safwan ya tsuramata ido yanajin wani shauki na dibansa domin wannan sa hannun datake tana rufe fuska shike burgesa yakesamasa shauki wanda yarasa ko na menene.

Minti biyar minti goma shuru Dr Safwan yaki fitowa yana chan kawai ya zurama Safeena ido yana kallonta so yake ya fahimci wani yanayi yake tsintar kansa in yana kallonta ammh yagaza fahimta sam,dakyar ya yakice abunda yakeji ya mike yana kallonta yace"to madam mukam munyi harama"Da wutsiyar ido ta kallesa kan tace"daman ba kwana zakuyi ba..?"tafada da wani salo wanda ita batama san ta iya ba,mirmishi yayi kawai yana kallonta kasa mikewa tayi saboda idon daya zuramata yana kallonta yana wani shafa sajensa yana cizan lebensa na kasa yunkurawa tayi tamike tayi gaba tana Fadin"Allah yammh tayi kukoma kaduna yanzu"tafada tana isa kofar dakin da sauri ya isa ya cimmata tana kokarin fita ya bangaji kafardarta atare sukaji wani shock kamar wuta yaja su dagowa tayi tana kallonsa kawai sai yasamu kansa da dagamata gira daya yanajin wani farinciki na shigarsa,sunkuyar dakai tayi ta fice da sauri,Akasalance ya fito yana ma Ummi sallama.

Ummi tace"A"a Tahir dare bai yi ba yanzu fa za'a kira magarib..?'Dr Safwan yace"Babu komai Ummi muna da Aiyuka gobe asibitine infact ma bamuyi shirin kwana ba"Safeena dake gefe tsaye jikinta duk yayi sanyi yanzu shikenan mr handsome zai tafi ya barta _topha safeena har Dr Safwan din yazama mr handsome_😛

Ana haka saiga Abba yayo sallama yashigo hannunsa rike da manu da usman ummi tace"Shikenan ma ga Abbanta nan yadawo, Ummi tanamai Sannu da zuwa tana fadin"Allah yasa zaku hadu mijin Safeena ne sukazo shine wai yanzu zasu tafi"Abbah ya kariso yana fadin"Masha Allah...Sannunku da zuwa' zubewa sukayi suna kwaasan gaisuwa ya amsa yana tambayansu yasuka barosu suka ce suna gaishesu.

Abbah yace"to masha Allahu...Ammh dai zaku fasa tafiyarnan dan magariba ma ake kira'Dr safwan zaiyi mgana Dr Tahir yayi saurin cewa"Toh Abbah matsalar bamuyi buking din gurin kwana na bane"Abbah yace'Haba dan wannan babu matsala akaba na wajema balle ku nagida kuyi sallah Safeena tarakaku nan gidan su baffanta isuhu sai ku kwana"Ummi tace Shikenan kuwa"Abbah yace akawo musu ruwa abuta Safeena tazuba musu ta mikama kowanne tana Zuwan kan Dr Safwan sai da ta duka kana ta mikamasa zuru yamata domin a iya tsawon rayuwarsa Sakina bata taba bashi ruwan alwala ba balle har ta rankwafa karba yayi yana fadin"weldon..yanmatana"yafada ahankali da sauri ta wuce tana rufe fuska,tare sukayi alwala da Abbah dasu usman suka rankaya massallaci abun ya matukar burge su Safwan yadda Abbah yasake jiki dasu yana ta tambayansu aiyukansu abunda Safwan ya fahimta su Safeena talakawane ammh masu wadatar zuciya kaf da kanta har iyayenta lokaci daya yaji sun kwantamai arai,sai sukayi issha'i kana suka dawo koda suka dawo Safeena ta musu jallof din shinkafa da kifi sai kunun aya ta fesa wanka cikin riga da sikat tasauya hijabi humra ta shafa ajikinta tana fitar dawani sirrin kamshi Su Ummi dakin Abbah suka yada zango suka bar Su Safeena dakin Ummi.

Itama shinkafan sunci badayawa ba kunun ayan dai suka sha bil haqqi da gaskiyansu😂tahir gurinsu Abbah yakoma ya bar mata da miji su kebe,to banda kallon juna suna aikin aikama juna mirmishi babu abunda sukeyi kowanne zuciyarsa tab farinciki.anan ne yake Nuna mata hoton dansa hakika kallo daya Safeena tama Adil ahoto taji yashiga aranta duk da lokacin da Ummi tafada mata yanada mata ko ajikinta ammh haduwarta da Dr sai taji dama ita kadai ta mallaki wannan hot guy din🤔🤔

sai after ten Safeena ta rakasu gidan Baba isuhu wanda wa yake ga Abbah gidansu na gaba kadan danasu yafi Abbah abun duniya kuma yanada manya ya"ya maza shiyasa gidansa keda dakunan kofar gida to daman dayake Abbah yamai bayani dasuka hadu a massallaci har suka gaisa da su Safwan din nan suka bar motarsu kofar gidansu safeena koda sukaje anygra musu daya daga cikin dakunan mazan gidan mai dauke da katifa wacce ke kasa sai sai kafet dake dakin sai toilet dakin tsaf dashi gwanin shawa'a Safeena bata wani tsayawa ba ta musu sai da Safe ammh sam Dr Safwan yaki barinta tatafi ita kadai sai da yarakata har kofar gida shima din tsayawa yayi yana kallon fuskarta cikin hasken farin watan daya haske garin..shigewa tayi gida tana masa dariya.

sai da ya koma yasamu sukunin kiran momma yake Fadamata halin da'ake ciki tayi musu fatan dawowa lafiya Haj.Mama na gefe take fadamata abunda Safwan din yacemata haj.Mama tayi tafi tace"Allahu akbar oh ni Maryamu Allah na gode maka kingani ko Hadiza yaushene safiyanu zashi wani guri har ya kwana"tafada  harda rike haba kan ta cigaba dacewa"lalle Nasan yayaba da zabina kenan..Allah na godemaka.Itama momma murna take tana kara rumgume adil tanaji aranta komai yakusa zuwa karshe.

Dr Tahir yanata tsokanan Dr Safwan kin tankasa musa yayi wanka yayi yabaje a katifa daga shi sai boxer ya rumgume filo yana wani lumshe ido kamar wani tsohon maye sororo Dr Tahir ke kallonsa kan yadauki filo ya wurga akasa yana Fadin"Bari na barmaka katifan saboda tsaf cikin dare zaka iya turmusheni kazata Safeenar ce,Tunda na lura jaraba ce fal aranka..."Tsaki Dr Safwan yayi kan yace"gwanda dani nasan dadin abun kai kuwa har yanzu kana kasa ne...Banza dan sa ido kawai,Dariya kawai yayi ya juyamasa baya.

Itama Safeena anata bangaren kasa barci tayi  tana juye juye data juya ta rufe ido sai taga Dr yana mata wannan tsadaddan mirmishin nashi mai kashemata jiki,dataga barcin yaki zuwa tashi tayi ta dauro alwala tafara Nafila tana godema Allah daya mallakamata Dr safwan amtsayin miji aurenta.Tadade tana addu'a kafin takoma ta kwanta tana mirmishi ita kadai.

*Domin samun Damar Zamay Daya Daga cikin wacce zata Karanta Kayattacen Labarinmu na Silar Hallaci zata iya Tumtubata ta wannan Layin 09069067488 akan Naira 300 kachal*

*Anitha..*

Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*18*

----- Dukkansu barcinsu rabi da rabine domin kowani dakika zuciyoyinsu suna bugawa da sunan juna,amassallaci kusa da gidan su Safeena suka yi sallah sun gaisa da Abbah sundade tare suna mgana har Dr Safwan yafadama Abba,da zarar ya koma ammh insha Allahu yana komawa zai tanadarma Safeena inda zata zauna sai susa lokacin da za'a ayi bikin Abbah yafadamasa kar ya takura kansa Safeena kanwa take agurinsa.

suna dawowa sukayi wanka domin yau monday tushen aiki suna da aiyuka a hospital,shiyasa Allah yasa shi Dr yana ijiye kaya amota kamar yasani dinkinsa daya amso wajen kala uku su ya dauko ya sanya daya yabama Tahir daya kafin karfe bakwai sun zama ready.

itakuwa Safeena tana idar da sallar asuba bata komaba,fita tayi ta share gida tagyara dakunan

tazo ta musu abun karyawa kunun tsamiya tamusu da kosai daman tana tashi waken tafara wankewa,sai ruwan zafi wanda yaji citta da na'ana'a tashirya cikin riga da sikat na leshi milk and green kayan fiteed ne sun amsheta sun mata das da ita green din hijabinta ta tasaka,dogo har kasa ta dauki kayan akwando tama Ummi Sallama hakika Ummi taji dadin ganin yadda yarta bata Nuna wani damuwa ba duk da dai tasani aurene kawai ammh Dr Safwan ba ajin yarta bane _Abun Allah kenan_

Koda ta isa da kaya niki niki ta iske daga cikin gidan ankawomusu soyayyen arish da kwai harda kayan tea ta iskesu sun shirya ta duka har kasa tana gaishesu Tahir ne ya amsa yana dariya kan yace"Tashi mana amarya mun amsa gaisuwar aie"Shikuwa Dr Safwan tunda Safeena ta shigo kamshim humran data sa yashakeshi yarasa Natsuwarshi kallonta yake cikin wani yanayi wanda ya kasa gane kanshi Dr Tahir daya Fahimci haka ya fice ya basu wuri.

Tana nan durkushen kanta na kasa tana wasa da gefen hijabinta gaban na tsananta faduwa domim tasan wannan kallon nashi mai kadamata yayan Hanji yake mata ahankali tadago kanta caraf suka hada ido yana tsaye sanye cikin wani farin yadi milk mai sansti bayi da kauri tunda har ana hangan farar vest din dake jikinsa hulan kasan zannah bukar ce fuskarsa tayi fayau da ita yana furta da Annuri Kamar daren goma sha tara duka hannuwansa ya rumgume akirjinshi,kasa jaye idanunta tayi jitayi kamar kasa baza ta iya daukanta ba saboda wani kasala ke rufeta tsigar jikinta na tashi yarr!!!

saurin jaye idanunta tayi saboda tana gab da zubewa agurin mirmishi yayi kawai ya jawo kwandon data shigo dashi ransa yamasa dadi dayaga kunun tsamiya da kosai,masha Allahu yasha sosai kosan ma yaci sai ruwan na'ana'a shima yasha kadan ammh kowani lokaci tadago idanunsa na kanta,yana kammalawa yasa tissue yagoge baki ya mike yana fadin"Alhamdulillah...Yafada yana kallonta kai tsaye ya isa kusa da ita bata ankara ba shima ya durkusa har gwiwansu na gogan juna da Hanzari taja baya kallonta yayi kan yace'"yan matana yakamata amin ramgwame naga wannan kwalliyar kan in Tafi"Yafada yana wani lumshe idanunwanshi tuni jikin Safeena yafara rawa takasa dagowa sai ma kara dunkule data keyi cikin hijabi wani yanayi keJan Safwan yayi saurin mikewa kada yabi shawaran zuciyarsa na Rumguman yar mutane.

Wayoyinsa ya Dauka yayi Hanyar ficewa yana fadin"Shikenan tunda kin Hanani ganin Halas dina"yafada muryansa kamar zai yi kuka,taga da gasken  ficewa zaiyi da sauri ta mike cikin rawan murya"Am.... _*UNCLE*_"cak ya tsaya kafin ya waigo yana kallonta so yake ya tabbatar da itace takirasa da Unku kai verry interresting.

Cikin kunya matsananci ta yaye hijabinta ta rike hannunta kanta na duke tace"kayi hakuri…"tafada dajan Numfashi kamewa Dr Safwan yayi yana kallon Safeena tun daga sama har kasa yake kallonta idanunsa na yawo ko'ina ajikinta Safeena doguwace mai dauke da doguwar fuskar gashin idanunta sun matukar burgeshi structure din jikinta shi ya tafi dashi uwa uba Nonuwanta dasuke cike tab atsaye suna masa maraba cikin mutuwar jiki da wata irin fitinanniyar murya ya Furta'Tsarki ya tabbata ga ubangijin dayayi wannan Halittar...."Yafada still idanunsa kyam akanta ita kuwa yadda idanunsa ke yawo ajikinta haka takejin wani sanyi na ratsata kamar wacce zata yi masassara,cikin tafiyar kasaita ya karisa kusa da ita yasa hannunsa ya tallabo habanta yana fadin"Baki kyautamin ba Sam Safeena daki Ka hanani ganin wannan kyakyawan suran taki da wuri"Ya fada yana kokarin sa idanunsa anata itakuma taki saima runtse ido da tayi zuciyarta na bugawa tsuru yamata da ido yanajin wani magnet najansa wanda baisan sadda yasa Hannunsa duka biyu ya rumgumota ba yamata kyakyawan tarba afaffadan kirjinsa.

Ya salam Safeena ta furta akasan makoshinta saboda wani schock dayajata kamar ta wutar lantarki tunda take arayuwarta babu Namijin daya taba rike mata hannu balle har ya rumgumeta sai gashi tafada cikin wani yanayi wanda kwKwalwarta tagaza hasaso mata komeye shi,shikuwa Dr wani chemistery ne ke aiki ajikinsa wani dumi mai hadi sanyi dadi ke ratsasa hannunwansa yasa duka yakara matseta gam yana Fidda Numfashi sama sama tuni hijabin Hannun Safeena ya Sulale ya fadi dankwalin kanta yafadi gashinta data dunkule yawarware yarufemata fuska"wow..Shine abunda Safwan ya Furta yayin dayayi tozali da gashin Safeena haka yasanya hannuwansu duka biyu yana lailashi idanunsa arufe yanaji kWakwalwarshi na wani amsawa zut,zut kamar zai shida.

Sun dade ahaka Dr Safwan yakasa sakin ta Saida karar wayarsa ya fargar dashi cikin kasala ya sausautamata rikon yazaro wayar a aljihu yana dubawa yaga Tahir ne yana Dauka Tahir yafara cewa"Kai Dallah mallam kafa shanyani bakasan tafiya ke gabanmu ba"saurin katse wayar yayi saboda bazai iya mgana ahalin daya ke ciko ba so yake su hada ido Safeena taki yarda sai wani sunne kai take kan kirjinsa wayyo Dadi Dr Safwan suma kadai baiyi ba shi yaushe Sakina tatabamai shagwaba juz hug da kiss sai tace duk salon takurane.Mirmishi yayi kawai ya dauko dankwalinta yadora mata bisa kai yana Fadin"Sarkin kunya...Mu zamu wuce Tahir ne

yakirani,yana fadar haka yana mika mata hijabinta ta amsa ta sanya tana dukar dakai kallonta yakeyi yanajin wani bakon lamari na ziyartashi kardai ace in yakoma gida wanka yakamasa _Wanka fa Dr Tab koda yake andade ba'a hadu ba_😄

Tare suka fito yana gaba tana binshi baya sai da suka shiga cikin gidan ya musu sallama 20k yabasu suka amsa suna godiya,haka dasuka shiga yima Ummi sallama 30k yabata tace bazata amsa ba ya marairaice yace"Ummi...In baki amsa to kin Nuna min Safeena ce kadai yarki"Ummi tace"Kaima Danane duniya wa lahira Safwan nagode Allah yamuku albarka ya kaiku lapy"Suka amsa Da Amin Abbah kuwa daya bashi 30k kin amsa yayi sukayi sukayi yace'bazai amsa ba shidai burinshi ya rikemai Safeena da Amana"Hakika Mahaifan Safeena sun burge Su Dr Safwan matuka wanda har hakan yayi tasiri aransu.

Abun mamaki sai gashi kawai sun bude boot yara na jidan kayan abinci suna shiga dashi buhun shimkafa,katan din taliya katan din makaroni dadai sauransu narike baki cos nikaina bansan yaushe akasa kayan ba,sai dai Ummi su sukaga kaya kawai,Abbah baice komai ba saboda wannan karon in yace bazai amsa ba to surikin nasa bazai ji dadi ba.

Tabbas soyayyah gaskiya Safeena da Dr Safwan zukatansu sun aminta da juna domin daga ita harshi jikinsu yayi sanyi lokaci dasuka shiga mota zasu tafi Safeena na kofar gidansu tana kallonsu batasan sadda hawaye ya gangaro mata ba har Tahir ya tada mota Dr Safwan ya dakatar dashi ya bude mota ya fice sai dai ta ganshi agabanta kama hannunta yayi yana fadin'Kukan mekikeyi yanmatana"..?kallonsa tayi idanunta tab hawaye tace tana turamasa baki"Yaushe zaka dawo"..?tafada da shagwaba tab wlh badon mutane na wucewa ba abunda zai hanasa rumgumeta ya sumbaci bakin nan daya kusa zautar dashi ammh duk da haka sai da yakara matse hannunta yace"Yaushe kike so nadawo'..?kallonsa tayi ido cikin ido kawai sai tasamu kanta da furta"Ko gobene inaso"Mirmishi ya subucemai baisan sadda yace'Gobe. fa kikace,..?tagyada mai kai mirmishin yasake yi mata kan yace" Am srry bazai yuyi in dawo gobe ba,saboda in nadawo wazai kula da patient din..? "yafada yana kallonta kafin ya cigaba da cewa"kiyi hakuri verry soon zan dawo" yanzu tunda baki da waya ga wannan ki rike kan in dawo in siyo miki taki ko..?"yafada yana mikamata dayar wayarsa da hannu biyu ta amsa tace"Na gode Allah ya saka da alkhairi",wow....Shi yaushe Sakina yataba bata abu tagodemai ai gani

take dolema yabata ta amsa tana wani bude hanci kamar ta bashi ajiya,kura mata ido kawai yayi yana kallonta zuciyarsa yaji tana zafi in ya tuna Tafiya zai yi Tahir ne yaga abun bana karewa bane yadinga zabgamusu hon,Safeena ce tayi karfin juyawa tana Fadin"ka tafi....Kagaida hajiya da momma harda Adil Allah ubangiji yakaiku lpy"Tafada wasu hawaye na gangaro mata dagudu ta ruga gida wani kuka ya kwacemata.

jikinsa sa babu laka yakoma mota yana Shiga Tahir ya kallesa kawai ya girgiza kai ya tada mota suka dau hanya,sun Fita garin gusau jefi jefi yana kallon shashen Dr Safwan yake wanda yamaida kansa jikin kujera ya lumshe idanunsa kamar mai barci ammh hakika ba barci yakeyi ba gabadaya ransa da tunaninsa naga Safeena kwana daya kacal ammh tasamu wani gurbi mai girma azuciyarsa wanda baisan sanda tasameshi ba,ji yake tamkar yasakota cikin mota yazo kaduna da ita kallonta kawai da yanayinta kansashi nishadi balle yangarta da salon kunyarta.

Dr Tahir yakara kallonsa kan yace"Duk wannan Damuwar ta mecece Dr Safana..?"yafada kansa tsaye shuru yayi masa wanda har ya fitar da rai da zai yi mganasai chan  yace cikim sanyim murya"Bai shafeka ba plz Tahir karabu dani bana son damu"yafada still idanunsa suna rufe shuru Tahir yayi kan ya jinjina kai yace"I can belive my Dr fall in luv wit Safeena....Any why ta cancanta saboda kyawawan halayyata congratulation mr man wlh kadace ta ko'ina"Abun mamaki sai ga Dr Safwa yayi mirmishi yace'Thanks u mr Tahir bello suraj.

_to ya kuka gani kunga yadda soyayyar Allah take ko,sai Allah yabaka wanda ko a mafarki baka taba tsammani ba,juz imaging Dr Safwan yafada tarkon son Safeena konace sun fadama Juna,kuna ganin salon Safeena bakwa ganin lokaci kadan za'a Shafe babin Sakina arayuwar Safwan ba_?

*Shakira..*

Vote

Comments
Share
Like
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*Dedicated to my Sisi of Life Aisha Alto*

*19*

----Koda Karfe sha biyun Rana tayi ta musu a kaduna,duk Da sun sharara gudu ko ahanyama haka Dr Safwan yake sukuku dashi bayi da kuzari lokaci bayan lokaci yana sakin ajiyar zuciya shikadai daga karshe kuma yayi mirmishi shi kadai,Dr Tahir yayita kallonsa yana girgiza kai cos yasani tunda yacemai bayasan damu ko ya mai mgana tsiya zasu tafka dat why yakyalesa akwai lokaci.

Asibiti suka wuce saboda sunsan aikwai tarin aiyuka illai kuwa aiki ya rike su sai dare kana,yamaida Dr Tahir gida yamasa godiya da bangajiya,kana ya Nufo gida hon yayima habu maigadi yataso da gudu ya budemai yana mai maraba Abun mamaki yana sulala motar tasa parking space kawai yaga Hajiya mama tafito da sauri zani ahannu tana Fadin"Oyoyo....Safiyanu angon Safeenatu"tafada tana budemasa murfin mota cikin kasala da mamaki ya fito fuskarsa na nuna almar gajiya yace"Hajiya...Wai baki kwanta ba"..?ta rike hannunsa tana fadin"inkwanta banga dan jikalle na guda daya aduniya ba,to ina Ibrin Amarya Safeena yaka ganta tayi ko"..?Tafada harda dagamai gira😂dariya takusa kubcemai yace"oh...My god hajiya dawowata fa kenan wlh am tired"yafada yana yamutsa fuska rikosa tayi tana fadin"Koma u taya ne😂wlh alqur"an baka isa ba sai kabani Ibri daga farko har karshe karyan tsiya ke dawani turancinka na karya.."'tana fada tana jansa shi saboda mamaki ma yasa yakasa kwatar kansa jaye dashi har falo tana kwalama momma kira"Ke Hadiza ki fito ga danki yadawo dan nasan shigewa cikin duk na kewarsa ne"tafada tana dankwarar dashi akan kujera.

Momma tafito sabe da Adil tana Fadin"Oyoyo....Babana mutanen Zurmi andawo?Ya sauko yana gaida momma ta amsa da fara'a tana tambayan ya ya barosu da kuma Safeenar ya amsa da suna lpy Allah sarki hajiya ashe kichen ta shiga ta  zubomai sauran alqubus din da momma ta musu dazu da miyar alaiyahu taji naman rago da man shanu,tahadomai da furarsa masoyiyarsa

tana kawowa Adil na hannunsa tace"Maza ijiye yaron nan kazo kaci abinci dan nasan ka kwaso yunwa'baiyi gaddama ba ya mikama momma shi ammh kiri kiri Adil ya noke shi yasan ubanshi Haj.Mama tace"Kai kaci batar ubanka zonan...Inbanda kana butulu Hadizar zakayima kiyawa"Tafada tana rikosa harda dunkurinsa yayi nakwa nakwa yana kallon babansa zai yi kuka Haj.Mama tace"kul kamin kuka wlh in ci ballagazar uwarka"Ashhh....Dr Ya furta kan yace"plz hajiya stop it....Adil iz juzt 6 month fa mai yasani"yafada yananuna rashin jin dadinsa"Haj.Mama tagyara zama ta sunkuyar da kanta tace"Gani dakeni habule ko in kwantama ne..?tafada harda rusunawa,banza da ita yayi kan yayi bismillah yafara cin abincinsa Haj.Mama Tace"Au dan batan uba kawai wlh sufiyanu kafita idona wai tun yaushe nake cema kadaina zagina da wannan yaren eye..?"tafada da karfi,banza yayi da ita cos baisan hayaniya sam itakuwa ta kulu tadinga masifa tanayi tana hadawa da Adil oh ni jami ko meye ruwan Adil anan oho.

yana kammalla cin Abincin ya wanke hannu ya mike yadauko kwanon furar yana cewa"momma zan je na kwanta wlh gabadaya agajiye nake..But tomorrow zan yi mgana daku"Daga haka yafice momma tanamishi fatan tashi lpy ita kuwa Haj.Mama binsa tayi da tsaki mteswwww tace"Aikin banza da wofi yo harni za'a ma gorin da'  dan ubanka inda ban haifi ubanka ba za'a haifekane kuma in kayi zuciya zo kadauki dan kamaida ma uwarsa dama mungaji da reno wlh"Tafada tana dunkurar da Adil akasa ta mike tawuce fuu tana fadin"Ni za'ayima iskanci da bura uba.muda mukaga jiya mukaga yau muna shirin ganin gobe kuma da izinin Allah🤣🤣🤣

Adil kuwa ya fashe dakuka momma tayi saurin daukansa tana jijjiga sa ba daman ta tanka haj.Mama tadawo kanta ta lallaba ta kwashe kayan da Dr yaci ta kai kichen,takoma daki tana lallamin Adil shikuwa yayi luf a kirjin momma yana ajiyar zuciya _ho yahadu da fushin haj.Mama wo_

Yana zuwa sashensa abun mamaki Sakina na hakimce kan kujera tadora kafa daya kan daya sanye take dawata doguwar riga ta kamfanin armani baka rigar ta matseta kannan  babu dankwali gashi yaji gashin doki abun haushi abun takaichi yan aikinta guda biyu ke durkushe gabanta daya na mata tsausa daya na sama ta jan kumba  wa'iyazubillah tana yar musulma tana salla tana komai kumbanan zaro zaro kamar ta horo tayi wani shame shame kamar sakarya kallon daya yayi musu yayi saurin kauda kai ,ko gaisuwansu bai amsa ba yayi gaggawan  shigewa master bedroom dinsa domin jiyayi wani karni karni na tasomai yanaji kamar zaiyi amai.

Sakina tabishi da harara kofin dayake hannunta cike da madarar hollandian ta kurba kan ta furta afili"Rubbish.....Tana kallon yan aikinta dasuka zuramata ido tadaka musu tsawa dole kowacce ta shiga taitayinta.

Yana shiga ya maida kofa Ya rufe fridge yafara isa ya sanya furarsa ciki kafin yafada toilet yayo wanka tareda dauro al'wala daure da tawul ya fito daya akansa yana tsane ruwan kan dressing mirror ya isa yana shafama jikinsa mai sai daya kammallah ya feshe jikinsa da body spry kana ya zura jallabiyan blue ya shimfida sallaya ya data sallah.

sai da yayi shafa'i da wutiri yadade yana addu'a wa kanshi da zuru'arshi gabadaya sai ga _*Dr Safwan sale Safana durkushe gaban rabbil izzati yana rokonma kanshi da Safeena rayuwa mai dorewa ta har  Abada*_ yana kammallawa ya ninke sallaya ya ijeye saman stool ya koma ya kwanta kan gado hannu ya mika ya jawo wayarsa dake a ajiye a side drower din gadon kenan ta bude kofa ta shigo babu ko sallama wani kamshi ne mai tare da kwauri kwauri ne yadake hancinsa shyasa yayi saurin dagowa,baki bude yake bin Sakina da kallo sanye cikin wata uban night gwon pick colour kafinka tsirara saboda gabadaya surar jikinta ta bayyana rigar batada hannu daya gareta,tana wani takun yanga adole ita zataja hankali miji ammh kash bata iya abun ba kwata kwata bai mata kyau ba.

Bakinsa abude ta kariso kusa dashi ta zauna tare da cewa"Dr nah...Rufe bakin"Tab.....Lalle yarinyarnan yar tasha ne wato Dr na haka yafada aransa,binta yayi da kallo aransa yana ayyana tabbas tana bukatar wani abu ne ammh matar da yadawo ko kallonsa bata yi bane yanzu zata wani kwaso jiki miya miya tanawani fadin wai Dr nah. _kai Dr Safana wai miya miya kamar wata mage_🤣

Shafa sajensa tayi tana fadin"Brk da hutawa likitar zuciyata..."tafada tana wani fari da ido daure fuska yayi yasa hannu ya cire hannunta yana fadin"quickly ask wht u want.....Zan kwanta ne"yafada yana kallon idanunta tsam tayi domin taga yana neman harbo jirginta kanta maze ta yi wuf ta fada jikinsa tana mai kukan kisss biye mata yayi cos yana so yaga inata dosa bakinta tasanya anashi tana sumbatarshi hannunwanta na shafa kwantattacen gashin kirjinsa cikin wani salo yayi kokarin kar ya biyemata ammh ina zuciya da gangan jiki na bukata tuni ya tallabeta yayi saurin birkitata tadawo kasan sa yafara aikamata da nashi zafafan wasannin itama tana maida masa.

Shudewar awanni biyu ya fito daga toilet kansa na digan ruwa Ya kalli Sakina datayi share share kamar jaka yayi tsaki yana duba kirjinsa yace"Sakina kewai wata irin mai kunni kashin ne...Har saunawa zance miki kidaina pixsing din kumbunan kina yar musulma infact ma kina jimin rauni look out"yafada yana nunamata yadda ta karceshi a kirji tayi wani lum da ido kan tace cikin sakarci"Haba my Dr kai komai nayi banyi daidai ba"Tsaki ya sake ja mtsweee kan yace"kinga don Allah ki tashi kiyi wanka kinsan ban hada gado dake da najasa  and kuma ki tabbata wlh kin zubar da wannan turaran aljanun nan"Yafada da serious matter Tasan Halinshi dole yasa ta mike tafada toilet tana tuna turaren dayace na aljanune hajiyarta ta kawomanata kan tayi amfani dashi ko me tace Safwan yamata jiki narawa zai mata ammh gashi bata ma kai ga tambayaba ya kushe abun.

Koda ta fito har yakoma ya kwanta ita agurguje tasanya jallabiyansa tahayo gadon tadora kansa akirjinsa tana wasa da gashin daya kwanta da dashin ruwa tafara mgana cikin sanyin murya"My Dr.....Tafada tana dagowa" umhmmm"yace mata kan taciga ba da cewa"ammmh.....Ammmmh....Dama game da businees dina ne"sai kuma tayi shuru yace"inajinki business women zaki kara bude wani reshe ne aturai"yafada da yar dariya tace'No.....Kudi zaka bani 2million ina so na shigo da wasu bags ne zuwa nigeria  kuma duka kudaden hannuna in na hada baza su isheni ba shine nake bukatar taimakonka amatsayinka na mijina"Ta fada wit full comfident.

Mikewa yayi yana tuntsuran dariya harda rike ciki zuru tamai da ido tana kallon sa domin batace tataba ganin Safwan na dariya haka ba daure fuska tayi ta mike tana fadin"Am not a fool....Safwan stop It.."tafada tana kokarin ficewa,saurin mikewa yayi yasha gabanta yana Nuna ta da yatsa yafara mgana"SAKINA KABIR KANKI....gaskiya saiyau na yarda baki da kunya do u think am fool dazan dauki kudi har 2million na baki"yafada yana nuna kanshi kan yadaure fuska yace"oh kin manta sanda keda uwarki kukacemin banida kudin zan iya dawainiyarki sai dai ke kiyi dawainyata to nikuma har abun zuwa anemi wani abu aguna ne ai nazata ke kin isa kima kanki komai"yadakata kan yadaure fuska yace"Yanzu ne nakeda daraja irinta miji agurinki....To bari kji wlh tallahi indai ni Dan Hadiza ne da Sale bazan taba baki kudina ba koda rance ne kuwa",yafada da kakkausan murya sororo tayi idanunta sun ciko da kwallah kam tanuna kanta tace"Baza ka bani ba..?"kai tsaye yace"yes...Ko kudin kine ai kudi yana gurin bussiness women so kiyi amfani da abunda ke hannunki cos Kudin Dr Safwan bana ci bane abi..?"yafada yana zakuda kafada alamar ko ajikinsa .

Idanuwanta yakawo ruwa ta nuna kanta tana fadin"Ni safwan kaci ma mutumci ko...?.Ya amsa da "eh....Ko zaki ramane..?"girgiza kai kawai tayi kan tafice tana kuka tsaki yaja

yace"shashasha kawai gobema kidawo ni dake muga wanda zaiyi laushi yana fadar haka yayi swith off din light din ya kunna dumlight ya fada gado yana addu'an kwanciya barci.

sakina nakomawa daki tafada kan gado ta fashe da kuka wayarta tadauka da tsohon daren tadinga kiran hajiya kari no answer dole tayi wurgi da wayar tana shure shure kan katifa maganganun Safwan nakara dafamata zuciya,aranta tanaji kamar takoma tamaidamai martanin mganansa _chai...Daga baya kenan meyasa lokacin dayake miki mganan baki mayar mai stupid kawai_🤨

*******

Koda garin Allah ya waye cikin farin ciki Dr ya tashi domin yayima  kansa alkwarin daina damuwa da al'amarin Sakina domin ya shirya tsaf don fito na fito da ita don ya nuna mata kuskurenta  dan yasan sakina da taurin kai bata bari aga  gazawarta.

Tun 7 ya fita domin yasamu emergency cll daga asibiti ko sashen su momma bai shiga ba bai samu kansa ba sai after 12 office din DR Tahir ya biya suka gaisa kan ya komo nasa isa yayi kan kujerar office din nashi yazauna yana jingina kansa alamar gajiya idanunsa na lumshe cikin sakan uku ya mike firgigit yana fadin"oh my god......Na manta yayi saurin zaro wayarsa yana latsa wasu nombobi kan ya kara akunne.

Safeena dake cikin dakin Ummi tana muraji'a cikin suratul yusuf taji wayar da Dr safwan yabata tadau tsuwa zumbur ta mike ta ijeye qur'anin tadauki wayan jikinta na rawa taja inda taga kamar nanne wurin dauka cikin sa'a kuwa tana karawa akunno muryashi ta dakin dodon kunnenta"yanmatana....Badai aji ake jamin ba...?" rufe ido tayi kamar tana ganinshi kan tace"Assalamu Alaika...Ina yini"ta fada da siririyar muryanta cikin kasala yace'oh...Srry wa'alaikas salam...Lpy kalau yan matana shine ko ki nemi ko..?"Tura baki tayi kafin tace"to ka nuna min yadda ake bude wayarne"tafada da shagwaba tsam yayi wani abu na zirgamasa kafin yace"oh......Am srry na sha'afane kece kika mantar dani kina ta kuka"la....Ni yaushe nayi kuka..?"yace"la...Akofar gidan Abbah kin tuna.?"yafada yana kwaikwayonta tsuntsurewa tayi da

dariya kan tace"kai ko....Yace"ke ko....Yafada yana siririyar dariya"rufe fuska tayi tana mirmishi shima mirmshin yakeyi yana fadin"Yan matana sarkin kunya...Ya Ummi na da Abbana ina usman..?"ta amsa suna lpy ,yace'me kikeyi ne yanzu..?"tace"muraji'a nake tunda yanzu bazuwa mkrantan nake ba kada haddan ta gudu"tafada tana mirmishi da sauri yace"ah..Meyasa kika daina zuwa mkrantan..?"tura baki tayi kamar yana ganinta tace"ba Abbah bane yace nadaina zuwa ba wai yanzu ina karkashin ikon kane"farinciki ya cikamasa ciki ko bakomai an nunamai yanada matsayi rausayawa yayi kan yace"Hakane mganar Abbah don mkranta kigayamasa kicigaba da zuwa kafin nazo nayi caraf dake"yakareshe fada harda kanne ido daya kamar tana ganinsa saurin rufe fuska tayi tana siririyar dariya cikin shagwababbiyar murya tace"Ni....Kabari bani so"shikuma ya amsa da cewa"Nikuma inaso yaza ayi kenan...?Yafada yana dariya itama dariyar take tana rufe fuska janta ya cigaba dayi da hira tun bata saki jiki dashi ba har ta saki jiki suna hira suna dariya sunfi awa suna waya sai da wata Nurse ta shigo tana fadin"Sir....Emergency .....Ok yanmatana i u clll u later daga haka ya ktse kiran ya fice da sassarfa.

Itakuwa Safeena rumgume wayar tayi tana jin wani abu na fitowa daga kasan kirjinta yana kwarara asassan jikinta tafada kan gadon ummi tana fadin"I miss u Uncle....sai da tafada kana ta rufe baki tana kallon kofa sai da tattabar da bakowa kana ta jawo wayar tana kwatanta yadda Dr yafada mata zata bude password din wayar illai kuwa yabude batasan sadda tace eyyyyyyyye...... ba.

*Anitha...*

Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*20*

"Wurin ma'ajiyar hotuna tafara shiga domin tadan san kan waya domin Aisha yayanta yataba bata wata tecno D3 _my first phone wo...Ammh sai da akasamu barawo ya saceta_😡abun mamaki hotunan Dr ne dana Adil kawai aciki kala kala iya kallonta wani suna kwance wani suna zaune wani yagoyasa gasunan dai sai iya kallanta,abun da yaba Safeena mamaki shine shin uwar yaron nan basu tare da Dr ne domin taga koda sau daya bata ganta acikin hotunan ba sai dai shi da Dr to kodai ta rasu ne..? tayi saurin rufe baki aranta tana cewa"Da ta rasu da Ummi ta fadamin"haka dai taita kallon hotunan babu hoton daya burgeta sai wani hoton Dr yana sanye da american suit,black and white ya daure wuyansa da tektie baki kansa yasha gyara yana maiko hannunsa sabe da rigar likitocinsa yana mikama Dr Tahir abu abakinn wani office ya juyo da gilashin dayake karamasa da kwarjini yana dariya aka dau hoton hakoransa farare reras suka bayyana hakika yayi kyau matuka a hoton wanda har Safeena tayi serving dinshi a Fuskar wayar saboda kyan dayayimata.

tana cikin daki taji sallamar Aisha suna gaisawa da Ummi kafin tatambayi Safeena Ummi tace mata tana ciki da Sallama Aisha ta shigo Safeena ta amsa tana fitowa daga uwardakan Ummi hannunta rike da waya tace"Yar halak yanzu nake zencencenki araina"Harara ta sakarmata kan tace tana zama kan kujera"Bawani nan ai ni wlh baruwana dake yanzuma zuwa nayi naji Ipy baki zuwa mkranta kwana biyu"..?Zama Safeena tayi kusa da ita tana fadin"Allah sarki kawar arziki...Dalilin dazai kawoni kenan"Tafada tana dafata mikewa tayi ta isa ga botikin dake dakin tasanya kofi ta debo ruwa tana juyowa taga Aisha rike da wayar tana juyawa cike da mamaki gabanta ta ijiye ruwan tana fadin"Sha ruwa Aisha kafin muyi mgana"Shuru Aisha tamata tana bin wayar da kallo chan ta shafa saiga hoton Dr ya bayyana wow...Shine abunda Aisha ta Furta tana bin hotonn Dr da kalon kafin tadago tana kallon Safeena datake kallonta tace"Kawata waye wannan gayen..?...Ke wayarma tawaye wai? Safeena tayi mirmishi ammh aranta taji zafin yadda Aisha take kallon hoton Dr tana Shafawa cike da shawa'a da burgewa _ho kishi🤔 tashi tayi ta isa ga windo Dakin kafin tace *MIJINA NE* da saurin Aisha tace"Mijinki kuma? tafada da sigar tambaya da mamaki juyowa Safeena tayi tana mirmishi tace"Eh...Mijina ne Aisha wanda Abbah yadauramin aure dashi kusan wata daya dawani abu da suka wuce"Sororo Aisha tayi kan ta mike tsam ta ijiye wayar takama hanyar ficewa tana fadin"Kinga nidai nayi gaba don aiki nake na fito ban iyawa da shirmenki Safeena"Safeena tayi mirmishi tace"Wlh da gaske nake Aisha nima yadda kikaji haka naji lokacin da Abbah ke fadamun"cak Aisha ta tsaya kan ta waiwayo tace"Wai da gaske kike Safeena..?"Karasowa tayi tadafata kan tace"Da gaske nake Aisha dama shine abunda zai kaini gidanku kenan".

Tsuru tamata da ido kafin tazame hannun Safeena ta isa ga wayar tashafa hoton Dr ya bayyana ta nuna ma Safeena tace"Kina Nufin wannan balarabe ko ince bature shine mijin naki..?

Dariya Safeena tayi kan ta isa kusa da Aisha ta amshi wayar ta kurama Dr ido tace"Kema kina tamtama ko Aisha..?"tafada tana kallonta kan taja hannunta su isa kan kujera tacigaba dacewa"Nima haka naji lokacin dana fara tozali dashi amatsayin mijina Aisha wlh babu karya Dr Safwan sale Safana shine mijina"Aisha tayi shuru tana kallon Safeena kan tayi wuf ta rumgumeta tana fadin"Kawata u ar so lucky wlh....Nayi murna sosai lalle kin tabbata mai sa'a

Nan Safeena ta warwarema Aisha komai tundaga farko har karshe Aisha ta jinjina kai tace"Ikon Allah kenan Safeena wlh in Allah yaso ka da Ni'imarsa bbu mai hanawa...Kinga abun Allah ko"Safeena tace"wlh ko amafarki bantaba tsammani ba Aisha sai gashi Allah da ikonsa ya zartar da komai"Aisha ta jinjina kai tana kara tabbatarma da Safeena ita mai Sa'ace.

Haka Aisha takoma gida tafadama mamanta ita kin yarda tayi sai da tasawo hijabi tazo ta tambayi ummi,Ummi tace"da gaskene kana ta yarda tasa albarka tareda da addu'an zaman lpy.

****

Itakuwa Sakina tun da tatashi ko takan Dr bata bi ba tashirya kayanta a trolley dinta tafito ta shige motarta ta dinga zabga hon habu mai gadi yana kewaye shikuma iliya  bayanan hakanan ta jira domin jin kanta bazai barta ta fito ta bude ba, aikwai Habu yasha tsinuwa kamar itace uwarsa harda cewa zata sallameshi tunda yagaji da aikin tana cikin mai tijaran sai ga Haj.Mama ta fito dama tunda taji hon din namarasa hankali tasan jakarce,aikuwa tana zuwa sakina tayi shuru haj.Mama tana kallonta sama da kasa kafin kafin tace"Ikon Allah ke inbanda rashin kunya da fitsara kitsaya gaban sa'an ubanki kina zagesa harda cewa zai bar gidan ko"..?Takareshe fada ta tana rike da  kugu Sakina tace"plz hajiya niban saki cikin shirgina ba plz stay out"Haj.Mama tace"kinci ubanki nikike cema pulaz🤣hala nayi kama da sakaryan uwarki ce to wlh bari kiji ke kanki inbakiyi hankali dani ba to sai kin bar gidanan don banga uwar dakike tsinana mana ba"Sakina tayi tsaki mtseswwww tashige motar ta ta kirar vibe tana fadin"Inkin isa in yadawo kisa ya rubutamin saki uku,sai na tabbatar da kin isa uselless kawai"Tafada tana kokarin zuge glass din motar Haji.Mama takarisa jikin motar tana fadin"Ahayyye....Tayaro kyau take bata karfo ai ni maryamu bazan taba yarda Safiyanu ya sakeki ba yanzu so nake ki kirbi abunda kika shuka da hannunki kuma Alhamdulillah abun da namiki tanadi yakusa isowa gareki wlh sai kin raina kanki tunda ke ballagazar macece wacce batasan darajan kanta ba"Tana gama

fadar haka tawuce tana fadin kai megida wuce kakama harkan gabanka tunda ba ita ta daukeka aikin ba aikuwa da gudu ya wuce itama Hajiya ta shigewarta sashensu tana wake wakenta.

Sakina tayi turus acikin mota bakincikin kalaman Hajiya dana Safwan suka taru suka sata fitar da kwallah kamar ita Sakina mai aji da daraja ake cema ballagaza dama jiya  Dr yace mata shashasha,tashare hawayenta tace afili wlh both of dem they will pay 4it kafin ta kwarara hon habu yazo da sauri ya budemata saura kadan ta takeshi sai da ya kauce ya rike baki yayi yace"Kai wannan mata baki kyale kowa ba shikanshi yallabai baki kyaleshi ba balle uwarsa da kakarsa balle mu yan aiki,tab...Ubangiji yamana maganinki"yafada da karfinsa kan ya rufe get ya koma kan bencensa.

Katsina ta dikko dakin kara ta nufa saidai haj.Kari taganta kwatsam tana mata kuka dakyar tasamu tafadamata duk abunda ke faruwa Haj.Kari ta mike ta lailayo ashar tace"babban bura ubanchan har ni za'a kawoma iskanci....Shi Safwan din harwani tsiyane balle uwarsa da wannan yamutsatsan tsohuwar har ta isa ta saki kuka, ita din banza to wlh bari Abbanku yazo Sakina nagaji dawannan auren yazo yasan yadda zai yi dashi"tafada tana huci kamar mayunwacin zaki _chau chau Haj.Kari Allah dai ya biya_ Sakeena tayi saurin cewa"a"a Hajiya wannan ba mafita bane kema kinsan wlh in Abbah yaji zai iya tsinemin kema kinsani"haj.Kari tayi shuru kan tace"eh...Kuma hakane shima sun asirceshi ji yake in aka taba yaron nan kamar antaba ubansa"Tafada harda yamutsa fuska Sakeena ta jingina da kujera tace'kyalesu hajiya so suke suga na ijiye kasuwancina indawo ina kula dashi da uwarsa inzamarmusu jaka"Haj.Kari tace"Ina har abada wannan bazai taba faruwa ba domin ni ban haifi malalatan ya"ya ba kudine zan hada na hannuna laila ma zan mata waya takawo abunda take dashi ki wuce kikama hanyar ki tafi ki saro kayanki kizo ki dasa daga inda kika tsaya kibarmin komai ahannuna ninasan matakin da zan dauka"Sakeena ta saki dariya tana fadin"Dat iz my hajiya shiyasa nake sonki"haj.kari tace'karki damu in ban tallafa muku ba wazai muku tunda irin uban da Allah ya baku kenan solobiyo"Sakina tasaki dariya tace"Hajiya Abbane solobiyo kuma ..?tace"kona yi karya"Sakina tace"A"a Hajiya da gaskiyarki"Atare suka sheke da dariya harda tafawa

_oh ni jami Duniya harta kaimu ga haka_🤔

****

bayan la'asar Dr yadawo agajiye yake dat why yafara isa shashensu sai da yayi wanka ya huta kana ya fito baiji duriyar Sakeena ba bai damu ba dama kuma ba motsinta yakeji ba har zai fita sai yasamu kansa da tambayan daya daga cikin yan aikinta ina take kai tsaye tacemai tun safe

ta fice bai damu ba illa zakuda kafada yayi yafice zuwa massallaci sallar mangariba kana yadawo ya wuce shashen su momma chan ya tarar da haj.Mama da momma suna hira,hajiya dai batai fushi ba saida ta tsaitsayeshi yafada musu yadda sukayi da mahaifin  Safeena ya kareshe da cewa"Yanzu na yanke shawarar Safeena zata zauna gidana dake anguwan sarki tunda a nan din  babu inda zata zauna.

Haj.Mama tamike tace"kul...Karma ka fara Acikin gidan nan Safeena zata zauna anyi ba'ayi ba kenan ai inhar Safeena tabar gidan nan ban Nunama ballagazan matarka na amsa sunana maryamu ba"Dr Safwan yace"To hajiya ina gun da zaki sata..?Kai tsaye hajiya mama tace"dakuna uku ke shashenka ko?tafada tana kallonsa da kai ya amsa tace"To ka gayamata ta kwashe kayanta adaya ka saka Safeena aciki tunda duk kaine mijinsu in lokacin da Safeena zata koma chan yayi nida kaina zan fada maka"Tana  gama fadar haka tatashi tawuce har takai kofar bedroom din tajuyo tace"Umarnine ba shawara ba kafara shiri cikin sati biyu nakeso Safeena tatare,tana fadar haka tashige daki Dr Safwan yayi ajiyar zuciya aransa yace"Hajiya daru....Ita kuma momma tana ta jinjina kai kafin tace"kaji abunda hajiya tace ko"Ya gyada kai tace"to kabi umarninta kazauna lafiya"itama daga haka tashige kichen zata kawomai abinci shikuwa Dr Safwan yayi shuru yana so yagane dalilin hajiya na zartar da wannan hukunci ammh ya kasa.

_hoho hajiya mama kinayi muna jin dadi Jamuje Allah ja da mulikinki haj tamu_✋✋✋

*commet, share Vote domin kwarin gwiwata...*

*Shakira..*
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*Wannan Shafin na yau Gabadayanshi na Masoyan HAJIYA MAMA ne❤️tace na gaya muku Tana godiya da Sakonnin Jinjinawarku gareta Allah ya bar kauna Tace na sanar daku Gabadaya Masoyanta na Wattpad da Whatsap SON SO FISABILILLAH*

*21*

" Koda kwamishina yadawo ya tarar da Sakina agida fada yahau yi yace meya kawota sai ta shirgamasa karya da cewa da izinin Dr Safwan tataho aikuwa baiyi kasa agwiwa ba yakirashi yake tambayansa abun mamaki Dr ya amsa masa da hakane cos bayaso ta dalilin sa Sakina tarasa albarkar mahaifinta.

****

Babu yarda Safwan ya iya da mganar haj.Mama domin ko momma bata tsallake umarninta daya fadama Tahir shima yayi na'am da batun na hajiya domin yace abunda babba ya hango yaro ko yahau rimi bazai hangoshiba.

kullum sai sunkusa raba dare suna waya da Safina sun maida abu kamar ibada shakuwarsu na kara ninkuwa atare da juna koda Dr Safwan bai budi baki yayi mgana ba shikansa yasani Safeena tana kokarin jan ragamar rayuwarsa agida ko office cikin waya suke kamar wasu tantabaru😛acikin satin yace tasa ido yana tafe saboda shirye shiryen Tarewarta.

Kamar wanchan zuwan wannan ma tare da Tahir suka tafi Ranar Asabar wanda tun adaren da Dr Safwan yafada mata suna tafe takasa zaune ta kasa Tsaye,gari na wayewa taje akamata kitso dama tun adaren tasanyama kafarta sajen yayi ja sosai tana dawowa dama ta aikama Aisha suka zage suka musu alalan hanta da lemon kankana wanda Safeena tahada shi da hannunta,suna kammalawa suka share gidan suka gyara dakunan Safeena tashiga wanka itakuma Aisha takoma gida ta shiryo.

Karfe 12 tamusu kofar gidansu Safeena wanda suna isowa yadaga waya Yakirata lokacin tagama shiryawa cikin wata doguwar shadda light green taji aiki da Sallah Abbanta ya dinkamata turaren ta Wanda Humrace kanwar Abbah inna husai ta aikomata dashi ta shafa tuni tadau kamshi ba make up tayi ba hoda kadai ta shafa,sai liptick data sanya ammh ta fito ras da ita fitowa tayi tana sanya hijabi tace"Ummi sun iso"Ummi dake dakin Abbah tace"To Alhamdulillah...Ki shigo dasu".

Cikin takunta na natsuwa ta isa kofar gidan dukkansu suna jingine jikin motar Idanunta suka fara sauka kan Haskenta Yau kam sanye yake cikin wani farin yadi mai stantsi da yarari yana da ligo ligon zane a jikinshi ammh shara sharane domin hatta farar vest dinsa ana gani kafarsa sanye cikin bakin buddaden takalmin na fatar damisa hannunsa sanye da agogo na kamfanin rado,hularsa kansa kubece bakace idanunsa boye cikin gilashin dake karamasa kyau,cikin mutuwar jiki yake kallonta itama shi take kallo kasa kasa tana jifanshi da mirmIshi Dr Tahir ne yayi gyaran murya Yace"To mr and mrs love kunbarni atsaye fa"Da sauri Safeena tace"La...ya Tahir yi hakuri barkanku da zuwa ku shigo"Tana fadar haka tajuyawa suka take mata baya da sallama suka shiga cikin gidan Ummi ta fito tana amsawa zubewa sukayi suna kwasan gaisuwa ta amsa cikin farin ciki tana tambayansu mutanen gida sukace suna gaishesu.

Daki suka shiga suka iske Safeena ta turare dakin da turaran wuta mai kamshin dadi ta shimfida musu darduma a inda zasu zauna suka zauna Dr Tahir na fadin"Gamu akaro na biyu amarya kuma insha Allahu na karshe"Da sauri ta dago tace"Na karshe kuma..?

Tafada da tashin hankali yar dariya yayi kan yace"Eh man daga wannan zuwa sai dai na zuwa daukanki zuwa kaduna ko..?"Yafada yana kallonta da sauri ta rufe fuska tayi waje tana mirmishi shukuwa Dr ba baka sai kunni domin duk inda Safeena tayi yana binta da ido ne yakasa mgana saboda jiyake kamar yana wayo a gajimare saboda farinciki.

Daya bayan daya tajera musu komai agabansu Dr Tahir na mata tsiyan ta shirya likitan nata ci ne dashi ta shirya mirmishi kawai tayi batace komai tabasu wuri su ci abinci kafin takoma tayi mamaki taga yadda suka ci alalan lemon ma sun kusa shanyewa🤣

Dukawa tayi kana tafara gaishesu Tahir ya amsa yana ta mata tsiya itadai batacewa komai sai mirmishi ana haka saiga Aisha ta shigo itama ta shirya cikin kayanta mai kyau Safeena ta

gabatar da ita a matsayin kawarta suka Gaisa da Dr kana Tahir har yana cewa"Shine taki zuwa sai yau"Dariya tayi tace"Yau din aka gayyaceni"Harara safeena tazabgamata karaf a idanun Dr Safwan wanda ya mata kuri da ido yana cizan lebe ai su tahir sai suka fahimci sukadaine ke hirar Dr Safwan da Safeena hirarsu ta aikama juna sakonni ne ta idanunsu Dr Tahir ya mike yana fadin"Kinga kawarmu zo mu fita tunkafin mara kunyar nan yabamu kunya"Aisha ta mike tana fadin"Kwarai kuwa don itama ba kunyar ta isheta ba"mirmishi suka musu kafin su fice suna fita Safwan ya maida hankalinsa kachokan kan Safeena itama tanaji tasan kallonta yakeyi shiyasa taki dagowa ajiyar zaciya ya sauke tareda Numfashi da sauri tadago ta kalleshi yayi saurin langwabar da kai yace"Shine ko dan sannu da zuwa ko..?"Yafada idanunsa kyar akanta cikin sauri tace"la...Bana muku ba"Shima da saurin yace"NO...ke agarinku haka ake ma miji oyoyo...?

Tadago tana kallonsa lokaci daya fadi tace cikin shagwaba"To yayane akeyi..?"Mirmishi yayi yace"Gud girl bari kigani....Ya mike tsam ya isa gabanta yasanya hannu yadagota ya zaremata hijabin jikinta yana karema kallo cikin sha"awa kafin Safeena tayi wani yunkuri yayi wuf ya rumgumeta tsam akirjinsa yana fidda Numfashi sama sama hannunsa ya saka yazagaye kugunta dashi ya matseta sosai hannunsa yadauko yakara azawa bisa hips dinta atare sukaja Numfahi shiii!!!kamar suna shan yaji tuni Dr yaji wani abu na mai yawo tudun hip din Safeena yagama rikitasa baisan sadda yake sanya hannu yana shafashi a hankali ba cikin kwarewa itakuwa Safeena neman shidewa takeyi saboda Dr yazomata da wani al'amari mai girma wanda kwakwalwarta baza ta iya dauka ba tafara mutsu  mutsun kwace kanta dat why ya sausautamata rikon yadago yana kallonta idanunta arufe ya kurama ma lips dinta ido dayake wani maiko baisan sadda ya dora lebensa akai ba yafara wasa da harshenshi akan lebentakara kamkame ido Safeena tayi tanajin wani abu na zirgamata sai da yagama lailaya lebenta kafin yatura harshenshi cikin bakinta topha anan wasan ya fara wani irin sumbata ne mai tsaya aran masoyi yake mata tare da shafa ko',ina na jikinta tabbas Dr yafara rasa control dinshi yafara nishi sama sama ya neman turamata hannu cikin riga gashi tana tsoron ashigo agansu batasan sadda ta fashe maida kuka ba jin kukanta yasa yayi saurin sakinta yakoma ya jingina da bango yana sauke Numfashi idanunsa a rufe yace cikin murya kamar ta mara lpy"Shiii!iz ok bazan kara ba"da sauri tasa hijabinta zuciyarta na bugawa yadade tsaye kafin ya koma ya zauna abunda ta lura dashi jikinsa gabadaya yayi sanyi yadukar dakai kawai Safeena taji gabadaya ranta ba dadi tayi sanadiyarta da mijinta yayi fushi da ita shiyasa tatashi a hankali ta isa kusa dashi ta zauna kanta akasa tace"Don Allah Uncle kayi hakuri baran kara ba"dagowa yayi yana kallonta idanunsa sunchanza kala mirmishi yamata kafin ya riko hannuta yace"Karki damu yan matana dama nadade awannan yanayi kawai nidai fatane in kika tare bara ki dungamin rowa ba ko..?

"Yafada yana kanne mata ido daya"saurin kauda kai tayi tana mirmishi yace"Common tashi kije kifadama Ummi ina son mgana da ita tunda Abbah bayanan kuma sauri mukeyi yanzu zamu koma",tayi lau da ido zata yi magana yayi saurin cewa "Yaushe kika fara gardama"da sauri ta mike ta fice ta iske babu Tahir balle Aisha Ummi ke fadamata wai ta kaishi zaga gari rike baki

kawai tayi nan tafadama  Ummi sakon Dr tako sanya hijabi ta shiga bayan sunkara gaisawa Dr Safwa yace"Ummi dama mganar tarewar Safeena ce hajiya tace nan da sati biyu ina fatan babu matsala..?"Ummi tace'Sati biyu safwan gaskiya yayi kadan...Ina laifi wata biyu kan lokacin anfadama wanda yadace"mirmishi yayi yace"Duk don wannan ba mtsala sai a fadamusu yanzu ko..?"Ummi tayi shuru kafin tace"A'a Safwan abarshi ahakan kawai"Dr yayi shuru kafin yayi mirmishi yace"Ummi duk nagane meyasa kikace haka Safeena ko ba aure kanwatace nimai mata komai ne na Aure saboda haka Ummi karku tada hankalinku Safeena kadai na aura ita kuma zaku kaimun"Ummi tace"Ayi haka Safwan mahaifinta bazai yarda ba"Yace"Haba ummi in hajiya taji bazata ji dadi ba zata ga kamar kun waretane"Ummi tace to shikenan ubangiji Allah ya saka da aiheri yakuma bada zaman lpy,ya amsa da Amin.

Nan yayi sallama da Ummi kan tafito a waje suka hade da Safeena yacemata sauri sukeyi but komai kenan zasuyi mgana ta waya Dr tahir kuwa sai da ya dinga kiransa kana yadawo safeena tasha tsaraba kayan makeup dana makulashe ya siyo mata jibge da kudu 20k yabata itakuma Aisha 5k yabata sun nuna bazasu amsa ba ranshi ya baci dole suka amsa wannan tafiyar ma sai da Safeena tayi kwallah shima Dr dai sai ahankali karfe 4 suka mika hanya suna daga musu hannu.

Koda Abbah yadawo yaji abunda Dr yace cewa yayi "bazai yuyu ba zainabu, saboda komai ba sai saboda darajar yarmu zamuyi mata daidai karfinmu bazan janye lokacin dasuka sa ba saboda dama kyan aure mace tatare gidan mijinta zan ma yan"uwana bayani akwai kudade ahannuna kome suka yanke shikenan.

*****
Kaduna

Suna komawa yafara gyaran gida kuma har lokacin Sakina bata dawoba bai damu ba shiya bashi ikon yin gyaran gidan a tsanake kamfanin MARHABA Suka zo suka chanza tsarin dakunan bayan an shanza tsarin fentin, da kawatattun kayansu gabadaya sashen su dana su momma sai da aka chanza komai falon nasu an kawatashine da black and red shima bedroom dinshi an kawatashine da black and ash ita kuma Safeena pick and white na uwargida kuma daman kalanta k kenan blue and purple sukuwa su momma an kawata musu ne da kalan black and red ko'ina hakika gida yadau kyallin amarci kayan kaf habu da iliya yabamawa yace sukaima iyalansa sunrasa bakin godiya saboda alherin megidansu agaresu mai girma ce.

Kudi ya damkama momy mahaifiyar Dr Tahir itama yar kasuwa ce 2million yace tahadomai komai na bukatar aure na akwatin mace na Safeena kawai banda Sakeena ita kudi zai bata saboda sanin halinta ita yar tsarice.

Haj.Mama abu nasu mganin akwabesu tab ta shirya tatafi Safana tagayyaci yan'uwa da abokan arzuka na suzo su tayasu murnan tarewar matar jikanta sunyi sallama da iyami na sai sun hadu in sunkawo amarya,hakika Dr ya gwangwaje safeena akwati takwas shake da kyan alfarma momma da haj.Mama kowacce kala biyar biyar yayi musu bayan kayan abincin biki daya jibgemusu hatta Adil ma ba'a barshi abaya ba Dr ya gwangwajesa.

Ana saura Sati daya aka shirya kai kaya ai haj.Mama tabuga lamara tace da ita za'a dole kuwa akaje da ita sai matar kawu bala uwani sai momy sai wasu yan uwansu na Safana suka dunguma sai Zurmi wanda Tahir ya kaisu hakika mutanen zurmin sunga inda ake abun arziki domin kayan da'akawoma Safeena yazama abun yawo agari,su maman Aisha ne da matan baffa isuhu da su iyami da kanwar Abbahsu inna husai data zo daga cikin zamfara sai makota suka amshi kayan tare da kayan abinci buhu buhu na da kwalaye an amshesu cikin farinciki da karramawa to daman anzama Daya kawai aka baje ana sa albarka Ummi sai da tayi kwallar farinciki domin ko a mafarki bata taba zato ba.

Shikuwa Tahir gidansu Aisha ya Samu su Safeena ya basu sakon da yazo dashi kati na shaidar gayyata guda dari sai kwalayen cimgam da minti guda goma da tsabar kudi dubu Hamsi yace inji Dr in suna kuma bukatar wani abu samai mgana ta waya ai sunma kasa mgana saboda mamaki illar kawai godiya,sai wajen bayan la'asar sukayi haramar komawa cike da kyan soye soye irinsu dubulan cincin da alkaki cikin farin ciki aka rabu.

sunkoma suna bada Ibrin karamcin mutanen zurmi wanda suka kasa boyewa ita kuwa Safeena washegari inna husai ta tara ta suka wuce zamfara ita da Aisha domin ta gyarata sai dai tama Dr text tafadamai dariya yayi yace"Allah ya kiyaye hanya ai ni za'a gyarawa mawa ko"..?Dariya kawai tayi ta shareshi.

Tabbbas inna husai tadage da gyara yarta magunguna masu inganci irinsu kumbar da take sha da nono da wanda akeci hakanan sai kayan fruit data hada mata sai wanka lalle mai hade da sinadarin turare mai tsayawa aran masoyi cikin kwana biyu Safeena ta chanza jikinta yadawo yana fitar da wani kamshi mai dadi gashi tayi wani haske da sulbi ita kanta ajikinta tanaji ta chanza domin kullum cikin zubar da ruwan Ni'ima take ko wayama basuyi inna husai ta kwace Dr yanaji yana gani Dole ya hakura har komai ya kare.

Ana saura kwana uku tarewar uwargida Sakina ta diro gidan bayan shafe sati uku batanan daga katsina kano taje daga chan ta wuce dubai kwananta goma ta dawo sai da tsaya tagama clearing din kayanta suka iso hannunta tukun ta dawo tayi mamakin ganin chanji agidan bata gama mamaki ba sai da tashi ga sashensu taga ikon Allah batawani damu ba ita duk azatonta Dr neman sulhu yake da ita shiyasa tana shiga daki tace"Hmmmm dama nasan zaka nemi ni wlh zaka gane kuranka indai sakina ce"Tafada tana shekewa da dariya.

_lalle sakina kin cika sauna inbanda sakarci ko ada bai baki hakuri ba sai yanzu stupid kawai_🤔

*Shakira..*

Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*22*

"Koda Dr yadawo yaga Sakeena bai wani yi mamaki ba cos shiyanzu bata gabansa kokarin yadda zuwan amarya zai zama ready yake.

Bada wuri yadawo ba shiyasa sai da yayi wanka yayi sallah kana yadauki check din daya rubatama sakina kudi yanufi dakinta da sallama abakinsa ya shiga illai kuwa Yar mulkin na kwance kan gado tana zuba selfie tana daukan yanayin dakin dariya takusa kubcemai,saboda ganin yadda take wani ji dakai ita adole miji ya biyota dauke kai tayi kamar bata ganshi ba tacigaba abunda tajeyi mirmishi yayi kan ya isa ya zauna gefen gado yana fadin"Ashe andawo....Andawo Ipy..?

"kamar baza tayi mgana ba sai chan tace"Lafiya kalau aka dawo duk da akwai wanda baiso mutafi ba"Tafada tana wani girgiza jiki dariya yayi har hakoransa suka fito yace"Ai wani baice kar mutum yaje ba iyaka yace mutum yaje da kudinsa ne hakan da yayi laifi ne..?"Yafada yana kallonta basarwa tayi domin tagane yagasa mata mganane mikamata check din yayi takalleshi a wulankance tace'Na miye kuma mallam..?Yace"Ki karba nakine"amsa tayi awulakance tana dubawa check din 2000hud thousand ne arubuce dagowa tayi ta mika mai tana fadin"Ka makara ai ka rike tsiyarka domin ni yanzu nafi karfin taimakonka ko dama tsautsayi ya kaini Tambayanka"bude baki yayi kan yace"Ke...abunda kike tunani kenan..?"Yafada hannunsa a haba Sakina tace"Bangane ba"Yace"Kudin nan hakkinkine fa aure zan kara shine nafita hakkinki na baki kudin saboda kisai Abunda kikeso..."yafada yana kallonta kallonsa takeyi kan tasheke da dariya harda faduwa kasa kallonta yakeyi aranshi yana auna dabbancin sakina.

Mikewa yayi ya ijiyemata check din yanufi hanyar kofa yana cewa'Ki bar dariyarnan ina jiyemiki ranar da zaya koma miki kuka"Saurin mikewa tayi tasha gabansa tana cewa cikin shakiyanci"Tab...Wai aure zakayi kai bakaji kunya ba,ni zaka razana to ai bari kaji ni Sakina matar kaddarace mutuwace kadai zaisa kayi aure kai ko mutuwar nayi sai na ga dama balle da raina'Tafada tana nuna kanta kan takara shekewa dadariya,kallonta yayi kan ya girgiza kai yace"Kin Tafka kuskure sakina shiyasa har yanzu yake dawainiya dake kinyi kuskuren sawa aranki zan dauwama dake ke daya....watch and see"Yafada yana kada mata hannu kafin ya fice.

check din ta dauka kan tace"raba mugu da makami....Ibadane'tafada tareda fadawa kan gadon tana fadin"ji shi wai aure kamar auren banzane"Daga haka tajawo wayarta tacigaba daga inda ta tsaya

*Chai chai wlh kedai sakina anyi dabba wlh kin tabajin inda akayi wasan kishiya mtsssss mai kwakwalwar kifi kawai*😡

ko washegari tun safe Abuja tatafi saboda isar kayanta kotakan mganar Dr bata bi ba gani takeyi bazai taba iya kara aure ba sai da ta fito zata tafi yaganta shima zashi aiki yake cemata"Madam business sai ina kuma..?"Tayi mamaki ammh saita danganta haka da neman shiri yake a yatsine tacemai Abuja Mirmshi yayi mai kayatarwa yace"Allah ya kiyaye hanya madam business"Daga haka ya fice shashen momma ya barta nan itama daga nan tahaye motarta tayi gaba.

Ashashen momma daru suka sha da haj.Mama don yace tabari abincin sha'anin bikin yayimusu odar Daga Restaurant haj.Mama tace"Ina bazai yuyu ba tuka tuwon ne akafi su iyawa kokuwa miyar ne za'a nuna musu kukowa dafa shinkafanne za'a nuna musu to maza karya ya sake wannan ai barnan kudi ne yan'uwanta zasu zo Daga Safana suzasu komai yi kada inji ka gayyatomana wasu kedararru suna bamu abinci"Dole ya hakura ammh yana jinjinama  karfin halin hajiya mama na fadar abunda bamai sauki bane a gareta.

Tun aranar bakin Safana suka fara zuwa matar kawu bala uwani da abokiyar zamanta sai makotansu hakika haj.Mama tayi farincikin ganin baki sun fara hallata mussamman Haj.Mama tasa aka gayyatomata masu kidan kwarya daga zaria dushi  _wayyo za'a tuka tuwon babban gida_ momma kuwa farinciki yagama cikata duk inda ka ganta bakin nan har kunni goye da bawan Allah Adil.

Washegari kuwa sai ga mota  tahau sauke musu drinks kala kala da ruwa abun sai wanda yagani baki kuwa suncika gida harda yan garinsu momma Allah sarki aikin haj.Mama ce tace kowa yazo ataru anuna farinciki domin yanzu safiyanu yayi aure,koda Sakina tadawo daga Abuja taji hayaniya ashashen su momma ammh bata leka ba tunaninta yan kauyen nanne suka zo sucika ma mutane gida da hayaniya ko kallon shashen batayi ba tayi shigewarta shashenta agajiye take shiyasa wanka kawai tayi tafada gado sai barci yan aikinta naso suyi mata tsegumi domin gunsu habu maigadi sukaji yallabai zaiyi aure ammh ganin ba fuska yasa suka ja bakinsu sukayi shuru.

****

Zurmi...

Sai ana gobe tarewar Safeena tadawo duk wanda ya ganta sai yakara kallonta saboda wani sheki data keyi kamar daren goma sha biyar Koda tadawo tayi gyaran kanta da lallenta kawayensu na mkranta sunyi mamakin jin tarewar safeena kuma wai andaura tuni harta Mallam yahuza takaima katin Tarewar ya amsa yana sama mata albarka da aurenta gabadaya _Allah sarki loser_ batada wasu kawaye shiyasa daga ita sai Aisha suke gudanar da komai gashi daman Dr yace"Su zama cikin shiri karfe biyu za'a zo atafi dasu saboda kada suyi dare ahanya.

mganar kaya kuma hajiya ita tayi mgana Da Abbah tace kadama ya wahalar da kansa domin ko sunkawo zatasa amaidamai saboda safeena da safwan duk dayane agurinta ba bambamci to bbu yadda ya iya domin hajiya nada wata kima a idanunsa bbu abunda zaice sai godiya domin iyalan justice habule safana sun gamamai komai.

*YININ BIKIN TAREWA*
_*Both kaduna and zurmi*_

Tabbas inda ake dashi nan akeyi domin tuni takowani bangare shagali yakachame bari mu leka kaduna.

Haj.Mama tun asuba tasa aka dora tunkunya lamba talatin🤣🤣na tuwo da na miya aka shiga sha'ani atsakar gidan masu yanka alaiyahu nayi masu yanka albasa nayi wuri yahade sai hira ake ana shewa.

Itakuwa momma tana ciki ita da bakinta mommy na tare da ita ga dan Amanar ta Adil shima yaci gayunsa yau takefa ranar itama momma taci gayunta cikin swice less dinta tadau dauri momma ta fito ras da ita ita kuwa hajiya mama doguwar rigar shadda taci taji aiki abunta harda daurin gwagwaro🤣,kan kice kwabo am kammallah tuwo an kwashe aleda an zuba a kuloli miyama tuni ta sauka wacce taji naman rago zubu zubu aciki ga jallop din shinkafa itama an kammallah ansa a kuloli ga alalen leda shima an kammallah abun gwanin sha'awa tuni aka tsabtace wurin kamar ba'ayi komai ba.

Itakuwa sakina sai wajen 12 tatashi tayi wanka tafito falo koda ta fito taji hayaniya ta leka har sungama komai sun shige ciki sai hayaniyarsu kawai takeji tabe baki tayi takoma tasanya tashar bollowood tana kallo ko ajikinta shidaman Dr tun Safe yayi wanka yafice suna chan suna tsara yadda za'a tafi dauko amarsu ta ango.

Azurmi ma shima abunda ya gudana kenan domin ana hada hadan saukewa da dorawa ita kuma Amarya Safeena tana gidansu Aisha ita da kawayenta suna sitting cirewa kawai take tana zurawa chan bayan sallar azahar iyami tazo tatafi da ita gidan baffanta usuhu aka kaita yamata nasiha wanda tuni Safeena tafara kuka sun kawo kofar gidansu kenan sai ga motocin daukan amarya guda goma sha biyu hadaddu domin ba motar banza tahir da taufiq da jabir da Gidado,da sauran abokansu dai sukazo Tahir ne shugabansu.

Cikin gida akayi da Safeena domin kaita gun Abbanta yamata Nasihan zuwa gidan miji.

*Anitha..*

Commet
And
share
Vote
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*A hearty and Birthday to the most Adorable, and sweetest person i have know...Happy Birthday KHADIJA CANDY#Maama❤️Wish u Allah khairs and Noor*

*23*

'"Kai tsaye dakin Abbanta aka kaita wanda yake ciki domin anfadamai za'a tafi da safeena ita kadai aka bari dashi tana durkushe agabanshi sanye cikin dogon farin hijabinta tana kuka.

Abbah yayi gyaran murya Yace"Safeena kibar kukan nan hakan ki saurari nasiha mafi daraja da tsada daga mahaifinki wanda rashin sauraran zai sa kirasa abubuwa dadama arayuwarki"Yadakata cak kuwa kukan safeena yadauke Abbah yacigaba da cewa"Rana bata karya sai dai uwar diya taji kunya hakika yau ranar da amanarki zai fita ahannunmu yakoma ahannun mijinki ne to nasihata agareki yake yata shine na farko kiyi biyayyah zuwa ga mijinki ki kasance baiwa agaresa shikuma yazammiki ubangida kibisa sau da kafa domin aljannarki tana karkashin kafansa ne yake yata kada kizama mai bijirema bukatar mijinki akoda yaushe kisance mai goyamasa baya aduk abunda yasa gaba kada ki kasance mai gardama agaresa kuma kar ki kasance mai saurin fushi agaresa ki koyi mu"amala da kowa ki kyautatama yan'uwansa sai kema ya kyautata naki ki girmama abokiyar zamanki sai itama ta girmamaki domin keki ka auran mata miji kina kasa da ita sannan abu na karshe ki girmama mahaifiyarsa da kakarsa kamar yadda zaki giramamu Safeena ki kaunaci Safwan da duk abunda yadanganceshi to inkikayi haka kin rabauta duniya wa lahira yata'.."

yafada muryansa tayi rauni safeena ta fashe da kuka tace"insha Allahu Abbah namaka alkwarin baza kasameni mai saba umarninka ba'.."Abbah yace"Nasani Safeena bazaki bani kunya ba

tashi tashi asada ki da dakin aureki na har abada"Yafada yana mikar da ita tana mikewa ta rumgumesa kam tana kuka hannunta yakama ya sanya mata karamin al'qur'ani izu sitti kafin ya kira iyami yace suzo su fita da ita shikanshi hawayene ya gangaromai na rabuwa da yarsa mafi soyuwa agaresu su iyami suka banbareta jikin Abbah da kyar sunkusa fita da ita Daga Dakin yadaga murya cikin rauni yace"abunda na baki ki rikesa da kyau duk halin kuncin dazaki shiga to karki manta dashi domin shi din haske da warakane ga duk wanda ya rikesa ku tafi ubangiji ya kaiku Ipy yakuma sanya Albarka arayuwar Aurenki..

"Yanagama fadar haka yajuya baya hawaye sun gangaro masa haka aka fice da ita tana kuka gun Ummi aka kaita wanda tun shigowarsu take kuka ana bata hakuri iyami tace'",zainabu lokaci na tafiya kisama yarki albarka "Ummi tace cikin kuka tana dafa kan Safeena dake durkurkushe gabanta tace"Duk nasihar da zan miki yan uwana da mahaifinki sun miki nidai abu daya zan gayamiki kibi mijinki kibi mijinki ki mai biyayyah kana daga karshe ki kasance mai tsafta da kamshi akoda yaushe sannan ki girmama mahaifiyarsa da kakarsa in kika kuskura kika saba musu Safeena ban yafe miki"Maman Aisha tace"Ashsha maman Safeena"Ummi tatashi tadago safeena ta rumgumeta suka kamkame juna Ummi tace"ku tafi yata Allah yabaku zaman Ipy yasa  gidan zamanki kenan har mutuwa Allah ya miki albarka na yafemiki duniya da lahira"Allah sarki rayuwa duk mai tsausayi sai da yayi kwallah dakyar aka rabasu ummi na kuka safeena na yi haka Usman dakyar aka bambaresa ajikin safeenar aka sanyata cikin motar tahir wanda iyami da inna husai da maman Aisha suka sata a tsakiya sauran motocin kuma jama'a sukai ta shiga abun mamaki chan naga zugan Janaf novels 1&2 sunci ankosu na perper less blue and pick sundaura head pick su mom khadija mom Amira my xee Abi my juree name sake sahiba gun shiga mota harda faduwa, hakika sun bada kala domin kaf dinsu sun halarta ba wanda aka bari gadin gida wow.. Chan naga yan Na tafka kuskure fans suma sun kame awata jeep chan kuma na yan kungiyata Interlligent writers association suma da nasu gayyar suna sun kame awata bakar corrolla x hadaddiya na rike baki nace"Tab.  To yaushe suka zo nibanma san zuwansu ba nima dai na lallaba na shige motar kawayen Amarya kada atafi bani.

Karfe 4:00 dai dai muka dau hanya sai fatan Allah yakaimu Ipy.

******
Kaduna

Karfe 8:39 daidai muka shigo kaduna domin dai ba'ayi wani gudu ba domin Dr ya tsawartar yace"Kada ajamai asarar da baiyi niyya ba dole aka lallaba dasu ahankali ammh ina kallon yan janaf fans sai da suka ce atsula gudu dasu domin motarsuce akan gaba nidai nace to Allah yasa kada haj.Mama tace nayomata zuga😛.

Magadi najin hon yabude get motoci suka dunga sulalawa ciki aikuwa kikaji guda na tashi domin haj.Mama najin hon tayi waje matar kawu bala kuwa ta dinga sakin guda abun sai wanda yaji haj.Mama ta bude murfin motar amarya iyami ta fito da ita haj.Mama ta waiga tace wai ina matan ne banji guda na tashi bane ai kan hajiya tace me kuda ya kacame gidan domin yan janaf ma ba'a barsu abaya mussaman murya mom khadija data Name sake tafikowa murya sahiba kuwa muryanta kadai akeji  gida ya hautsine da murnan isowar amarya hajiya ta rike Amarya tana fadin"Aminiya kin biyashe ni domin kin kawomin safeena har gida ina kara godiya"iyami tayi dariya tace"hajiya duk mu godema Allah domin shine abun godiya"Haj.Mama tace hakane kam bari tashiga shashen hadiza tukun kafin taje barayinta tako amarsu kinzo gidan karamci gidan mutumci da amana tako da bismillah Amaryan Safiyanu tako da izinin Allah aifa nan aka dau sowa da guda anayi har shashensu momma itadai Safeena tana dunkule cikin hijabi tana kukan rabuwa da iyayenta.

SAKINA Na daki taji dirin motoci zuwa chan kuma sai guda na tashi ta ko'ina taji abun yawuce misali shiyasa ta fito ta isa ga windon falo ta leka sai ko taga tawaga guda ga haj.Mama rike da wata lullube cikin hijabi ana ta guda gabanta yafadi ras'ras lokaci na farko tareda rawan jiki a idonta aka wuce shashen su mommah jikinta asanyaye ta saki labule takoma kan kujera ta fada yaraf tana auna abubuwa akwanyarta ta tuna kalaman Dr _kudinki ne aure zanyi nabaki ki siyi ra'ayinki_ tatuna kuma abubuwan da ake tayi daga jiya zuwa yau ana shagalin biki ta tuna sanda taji wata nacewa"Brka da zuwa amarsu ta ango"zuciyarta ta buga lokaci daya tareda mikewa tana dafe kirji tace afili"Kardai da gaske auren Safwan yayi..........?

*Antiha..*

commet
Vote
Share
Like
[10/14, 20:01] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*24*

"Sai kuma takoma ta zauna tana cewa"Haba yama za'ayi safwan yayi aure haba nasan waye safwan mutum ne mai ra'ayin kanshi mace fiye da daya bata cikin tsarinsa"dariya tayi tace"Haba ni nasani"Kamar wata mahaukaciya tajawo waya tana dannawa ammh abun mamaki kowani dakika zuciyarta na bugawa takasa yarda da abunda kunnanta yajimata karfin hali kawai take.

Sukuwa tawagar Amarya suna shiga kai tsaye gaban momma aka direta haj.Mama tace"Samata Albarka Hadiza samata albarka da bakinki mai daraja"Momma tayi mirmishi tadafa kan safeena dake durkushe gabanta cikin hijabi tace"ina miki barka da zuwa ya ke yata ubangiji yasa albarka arayuwar aurenku da safwan"Tafada idanunta sunkawo kwallah anata amsawa da Amin cikin tsausayawa haj.Mama tace"Bar kuka hadiza da izinin Allah safeena haskece agaremu"Iyami ta amsa da "Insha Allahu maryamu sai ance gwara da akayi"Nan fa akayita addu'an zaman Ify agaresu gaba kidaya sai ga haj.Mama tadauko turare ta hau fesema amarya ana sakin guda guri ya dau sowa kowa na fadin Allah barna ke Hajiya mama.

Sun dan jima ashashen su momma kafin hajiya ta musu jagora zuwa shashen Amarya suna tafe ana guda sakina na zaune taji hayaniyar na ta karuwa kuma kamar shashenta ake dosowa bata gama mamaki ba suka shigo haj.Mama agaba tana kwarara sallama Amarya da tawagarta suna baya Sakina dake rike da waya batasan sanda wayar ta subuce ba ta fadi kasan tayels din dake falon ba,Da Sauri ta mike idanunta sun fito jikinta na rawa tana kallon jama'an dake shigowa da guda bata gama mamaki ba taga hajiya mama ta nufi dayan bedroom din dake kusa da nata tasa makulli zata bude Sakina bakinta na rawa tace"Am....Am....Nace ba..?

'Tafada murya na rawa hajiya ta dakata ta juyo tana kallonta kan tace"oh...Na manta iyami ku fara isa da ita gun uwargida ku mika amana yadda ake na al'ada"Tafada harda dariya iyami tace"hakane tako ja hannu safeena dake rike da kawarta Aisha sai gaban sakina dake tsaye kamar mutum mutum aka dukar da ita inna husai ce tace"uwargida ga Amanar kanwarki nan ku hade kai ku zauna Ipy da juna shine kwanciyar hankalin mijinku"tafada tana kallon

Sakina,Sakina ta zura ma safeena dake durkushe gabanta ido tana so tababbatar da ba mafarki take ba Hajiya mama tace"Ta karba Allah ya tayamu rikewa ku karasa da ita ciki kunsan uwargidan akwai mulki"Tafada harda shewa jikin wasu yayi sanyi domin sudan fahimci cewa sakina bata cikin hayyacinta,haka suka mike suka rankaya dakin safeena iyami tace"Kishiga da kafar dama safeena kiyi addu"an mutuwa ce zata fitar dake"Gyada mata kai Safeena tayi hawaye na kwaranyomata.

Hajiya mama data tsaya abaya saida taga kowa yashige kana ta kalli sakina dake tsaye dafe da kirji tace"Ahayyyye....Rana bata karya sai dai uwar diya taji kunya,nasan kina tunanin mafarki kikeyi ko? to kibude idanunki da kyau ba mafarki kikeyi ba da gaske Safiyanu yayi aure da Amaryarsa safeena itace aka kawota yanzu wannan shine amsa abunda kika taba fadamun watannin baya,kin manta ko? to bari in tuna miki kince in zan iya yima jikana maganin matsalarsa nace miki bani da ikon yayesa masa mtsalarsa ammh ina da ikon kawo masa wacce zata iya yayemasa"Hajiya mama ta dakata kan tacigaba da cewa"To yau shine ya tabbata....Ni maryama duk wanda yaci tuwo  dani miya sha Nasan ko ahaka na barki kingane kuranki"

Tana gama fadar haka tayi shigewarta dakin safeena tana fadin"ya banji guda na tashi bane kudaina daga kafa fa" Ai sakina lokaci daya taji wani abu ya dira bisa kirjinta ya gangara har sassan jikinta kafafunta suka hau rawa lokaci dayata zube akasa tana dafe kirji cikin karaji tace"Na shiga uku nalalace ni sakina aure"Tafada da karfi to dayake hayaniya yayi yawa ba wanda yajita sai yan aikinta dake kichen suka rugo suna tambayata lafiya abun mamaki sakina ce ke hawaye idanu biyu tana girgiza kai tace"Never wlh it can happen...Kai haba bazai yuyuba wlh sam"tana fadi hawaye na kwaranyomata masu zafi da radadi so take ta karyata abunda taji kuma ta ganine ammh saboda dakiyar zuciya takasa yarda din.

Suna ta mata sannu ko kallonsu batayi ba tamike dakyar tana dafa bango tashige daki tana fadin"Ina never 4ever wlh...Ni din kishiya tab wlh badai niba"tana fada tabuga kanta agaru ta fashe da kuka mai tsuma rai tana bubbuga hannunta agaru tana ta surutai"Na shiga uku ni sakina kardai ace da gaske ne sai kuma tayi shuru sai chan tace'kodai wasane wanine adanginsu yayi aure"Sai kuma chan tace'to ai hajiya bazata min karya ba "Sai kuma chan tace"Wlh da gaskene wayyo ni sakina na mutu na lalace tafada tana sulalewa akasa tana kuka mai cin rai.

_Ho ho chai chai diz girl kinada hauka taurin kan sakina na burgeni don ubanki kiga amarya da idanunki kiki yarda saboda muguwar taurin kai zaki yarda in kika ga Dr ya shige dakin amarya Addabun Arab inji mrs ibrahim_

Adakin amarya kuwa anata yaba dakin sabida yadda ya tsaru kowa sai san barka yake nan fa aka shiga shigowa da abinci kala kala da abunsha aka baje ana dibar girki ana hira safeena dai ko kadan bata ciba domin har yanzu kuka take muryanta ya dishe sai wuraren sha daya suka baro shashen safeena aka bar safeena da kawayenta sukuma iyaye suka koma barayin su momma.

Su kuwa su Dr tahir suna ijiye tawagar amarya suka juya gidansu tahir suka wuce domin chan suke daman suka iske ango na jiran dawowarsu sun tabbatar mai da amarya ta iso cikin aminci da salama ajiyar zuciya ya sauke kan yace"Ina ta kiran wayarta tana ringing but no answer tahir ne yace"To sai kayi hakuri gobe in mun kaika domin amarya harmuka zo kuka take"Kuka safwan yafada yananuna damuwa Tahir yace"Eh...kukan rabuwa da gidamana Dr safwan yakoma ya kwanta yana cewa"Allah yasa tabar kukan nan cos bani son ciwon kai yakamamin ita'!shekewa sukayi dadariya Gaddafi yace"Shege nawa karka wani damu gobe zaka fanshe kaji abokina"Kara fashewa sukayi dadariya shikuwa banza yayi dasu kusan kwana sukayi suna mai shakiyanci.

abangaren su hajiya mama sunkwana cikin farinciki da Annushuwa haka bangaren ango da abokansa bangaren Amarya ma sai dai muce Alhamdulillah domin kowa yakwana cikin murna safeena ce ta kwana da ciwon kai saboda kukan data sha bangaren Sakina kuwa kwanan zaune tayi domin barci sai da kwanciyar hankali gashi wayarta taki tashi balle takira hajiya kari a idanunta aka kira sallah asuba idanunta sunyi ja sun kumbura saboda kuka ana shiga sallar asuba tazare key din mota ko mayafi bata saba tafice tanajin hayaniya adakin amarya ammh ko kallon gurin batayi ba tafice da sauri motarta tafada ta bata wuta afusace take dannah hon habu megadi dake sallah sai da ya sallame saboda firgici ai yana ganin Sakina cikin halin kamar mahaukaciya yayi saurin budemata tafice dawani mahaukacin gudu tsaye yayi yana dafe kai kafin yarufe yakoma yakara tada sallah.

Katsina ta nufa da asubahin nan tana ta zuga gudu ahanya domin sam bata cikin hayyaacinta itadai burinta ta isa ga mahaifiyarta ko ta fada mata cewa karyane safwa baiyi Aure ba.

Koda gari ya waye ba wanda yabi takan sakina balle yasan bata nan abun kari mai rai da lafiya akayima bakin zurmi dakyar inna husai ta mtsama safeena taci abinci tasha magani ta kwanta

don ta huta karfe biyu nayi masu kidan kwaryan da hajiya ta hayo suka iso tuni suka baje atsakar wuri suka fara sakin kida nan wuri ta hautsine hajiya mama ta shge fili tana tikar rawa ana mata manni tayi shar cikin leshinta ciki da alaku🤣🤣🤣kai yan zurmi sunga rawan banjo ai hajiya ta chashe iya chashewa momma na gefe tana dariya domin tasan yau ranar farincikin hajiya ne, safeena da Aisha kadai aka bari adaki su kuwa sauran suna wurin kidan kwarya ana cikin kidan ne saiga motar Dr Safwan tasawo kai cikin gidan shida tahir wanda tunda suka doso get din gidan sukaji kida na tashi .

Da mamaki Dr Safwan ya bude murfin mota ya fito wuri ko yadau sowan ga ango nan ga ango nan jin haka yasa hajiya mama tafito cikin fili ta nufi Safwan tanamai dariya.

*Janafty...*

Commet
And
Share
Vote
Like
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*25*

"Tana isa kusa dashi ta rikosa tana fadin"Oyoyo safiyanu ango Safeenatu barka da zuwa..."

tana fadar haka tana jansa zuwa filin rawa jama'a nata rangada guda suna isa tsakiyar Filin tace"Anchanza salon kida ga ango ya shigo flil baki safwan ya sake kan yayi mgana sunfara kidan kwaryan tako ina yana tashi sunayi suna fadar sunanshi da safeena haj.Mama ta rikeshi tana rausayawa shidai binta kawai yakeyi guri yadau ihu da sowa shikuwa Tahir manni yahau zuba musu yana yi yana daukansu video ana tafi kai yan kida sunkwashi naira dakyar Safwan ya yakice kansa Daga Wajen Haj.mama ya fice daga filin yana zufa yana jinjinama hajiya mama daru to a ina tasan masu kidan kwarya _Niko nace kana wasa da hajiya mama_

sai alasar aka gama kidan kwaryan Haj.mama ta sallamesu suka tafi suna godiya da tarin alkhairin dasuka samu suma yan biki suka fara shirin komawa yan zurmi mota guda Safwan yasamo aka maidaasu bayan Safeena tasha kukan rabuwa da yan'uwanta da Kawarta Aisha safwan yacikasu da kudi itakuma momma da hajiya mama sun cikasu da abun biki sun koma suna labarta karamcin yan kaduna,Yan safana kadai suka rage sai gobe zasu tafi Safeena momma ta rikota tun bayan tafiyar yan zurmi suka shga takaita har dakinta tana rike da Adli safeena tasa hannu ta amsheshi bai mata kiyuya ba yako je gunta ta tsuramasa ido kaunarshi na ratsata shima ita yake kallo yana bamgalamata dariya itama batasan sadda tayi dariyar ba ga guntun hawaye a idonta ba.

*****

Kaduna....

karfe Tara da rabi Sakina ta isa gida saboda tayi gudu ahanya sosai shikanshi mai gadin gidan nasu sai da ya firgita da irin hon din da sakina ta dinga saki shiya fito da kwamishna daga daki wanda yaji abun yawuce misali yana saukowa falo yaci karo da sakina wurjajan bako mayafi kamar mahaukaciya tana kiran"Hajiya....Hajiya safwan ya kasheni"kwamishina yadakamata tsawa da cewa

"KE.....Sakina..."Yafada yana saukowa daga saman benen Hajiya kari dake daki taji kamar muryan sakina nakiranta kuma taji muryan Kwamishina ai da hanzari ta sauko kasa zani na neman faduwa abunda taganine yakusa sata faduwa sakina ce durkushe tana rafzan kuka ga kwamishina yana ta tambayanta taki mgana ai da sauri hajiya kari ta karisa tana fadin"nashiga uku ni karima sakina lpy meyake faruwane..?"Tafada tana rikota ai da gudu sakina tafada jikin hajiya kari tana fadin"Hajiya safwan ya cuceni yaci amanata yamin kishiya"Tafada tana fashewa dawani kuka haj kari ta zabura kamar taga abun tsoro tace Tana dafe kirji"na shiga uku wani safwan din ne yayi aure..?

tafada tana kallon Sakinar sakina tace cikin kuka "Hajiya aure dakika sani kishiya yamin

bansaniba"haj kari tace"kan bala'i ammh safwan anyi tsinanne wlh....."

Kice tsinanniya mara tunani..."Kwamishina yafada ransa abace hajiya kari tayi zuru tana kallon kwamishina kan tace"Ni ce tsinanniya kabiru...?yace"Kwarai kece Tsinanniya ba Safwan ba inbanda rashin ilimi mutum yayi aure kice masa tsinanne.."

!Sakina ta shanye kukanta hawaye dai baidaina zubo mata ba, hajiya kari tayi tsam kawai tana kallon ikon Allah yajuya ga Sakina yana fadin"Ke shashasha mara tunani don ubanki me na fada miki kwanaki..?"Yafada rai bace sakina tace murya na rawa"kace karna sake dawowa gida da sunan amun wani abun"Yace"to me ya dawo Dake ...?Tace"dady amanata fa yaci yayi aure bansani ba"Kwamishina yace"ungo naki yamata dakuwa kan yace" dan gidanku ke amanarsa nawa kikaci to billayil lazim ki ka kuskura kika kaso aurenki na rantse sai dai kinemi wani uban bani ba"Yafada da kakkausan murya hajiya kari data daskare tun dazu tace"Haba Alhaji acuci yarinya kuma ka hanata yin kuka ga dan iska chan.....shout up....!yakatseta da tsawa kan yace"Na rantse karima kika kara samin baki cikin mganata saina ci mutumcinki"Haj kari ta rike baki kawai tayi shuru saboda ganin yadda kwamishina ke huci.

Yajuya zai wuce yace"Ba wacce tatabamun yaji agidana sai ke saboda kece baki dauki aurenki da daraja ba wlh saboda abun kunyan dakikeyi gidan mijinki kunyan yaron nan nakeji duk sanda yakirani.....to ki bude kunnuwanki da kyau kjini kijirani yanzu zan shirya muje na maidake dakin Aurenki wlh tallahi Allah daya ko inkika sake kika kashe aurenki sai kingane kurenki sakarya wacce batasan meyakemata ciwo ba"yana fadar haka ya haura sama da Sassarfa Daga ganin yadda yake Tafiya kinsan Ransa a bace yake.

Sakina ta fashe da kuka tace"Hajiya ki taimakeni kada daddy ya maidani wlh baran juri ganin safwan da wata mace ba"hajiya kari ta jawo ta jikinnta tace"Bar kukan nan sakina kada kisa nima nahau yi  fa kimanta kece sakinar nan mai aji da kwalliya da dakiyar zuciya"!sakina takara fashewa da kuka tana jin zuciyarta ta kusa bugawa kamar zata mutu kan hajiya kari tasamu zarafin mgana Kwamishina ya fito cikin shirinshi na bugaggiyar shadda harda babban riga yace"oya taso mutafi....Ke karima samamata mayafi bazan maidake a haka ba!sum sum tashiga daki tadaukomata mayafi cikin mayafanta ta yafamata sakina na hawaye ta fice haj kari tace"Alhaji....ya waigo yace"Bakiji ba kenan..?"Jin haka yasa tayi shuru har suka fice sunisu direba ya tukasu suka kama hanyar kaduna.

Hajiya kari tayi tsuru zaune afalo kan tace"komai ya dagulemin lokaci daya na shiga uku ni karimatu.

*Ai komai ya gama kwabemiki haj.Kari sai dai hakuri...*

*Shakira...*

commets
Share
Vote
Like
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*26*

"Tafiyar yan zurmi ba dadewa su kwamishina suka iso wanda sakina tasha kuka a mota kamar ranta zai fita kai tsaye shashen su momma ya Nufa shine agaba kana sakinar abayansa haj.Mama na falo zaune itada iyami wacce sai gobe zasu tafi suna hira kwamishina yayi sallama ya shigo sakina na biye dashi a baya da mamaki hajiya ta mike tana mai maraba cikin mamaki sakina durkushewa tayi anan tana kuka mai tsuma wanda ke saurare hajiya mama tace"kabiru lpy kuwa naganga a gaggauce haka..?

"Kwamishina yace"Lpy kalau hajiya wannan yarinyarnan ce tazo gidana tun safe tanama mutane kukan banza,ina fatan safwan na nan..?Hajiya mama tarike baki tana kallon sakina kan tace"Ikon Allah kabiru kaga muko ko fitarta bamu sani ba,bashi gida sai dai ka kirasa awaya"Kwamishina ya ciro waya yana fadin"Iz ok hajiya yimin mgana da hadiza don Allah kuzo mgana zanyi daku yanzu ina sau rine"Hajiya mama da iyami suka mike suka wuce cike da mamakin sakina wacce ke durkushe tana kuka momma ma tayi mamaki da hajiya ke fadamata zuwan kwamishina hakama safwan yaji lokacin da ya kirasa to daman bayan sungama

sallaman bakine suka wuce asibiti ahanzarce ya shigo mota ya taho

Afalon su hajya aka zauna da momma da sakina da hajiya mama sai Safwan wanda ke gefe yana kallon yadda sakina tazama kamar tsohuwa saboda tashin hankali gyaran murya kwamishina yayi kan yace"Don Allah hajiya kuyi hakuri da halin yarinyarnan nasani tana bata muku sosai ammh kuyi hakuri mussanman kai Safwan don Allah kayi hakuri"Safwan ya sunkuyar da kai yace"Daddy bbu komai wlh kaima kayi hakuri nayi aure baka sani ba abun ne yazo agurguje"Kwamishina yace"Masha Allahu wannan ai karuwace ubangiji Allah yatayaka rIko bbu komai safwan...Gatanan na dawo da ita hajiya ku shaida wlh in sakina tayi abunda safwan ya saketa wlh sai dai ta nemi wani uban bani ba gabadaya yarinyarnan tafita zakka a gidana halin uwarta kaf ta debe to billahil azim daga ke har ita inkukayi abunda kuka kashe auren nan wlh dukkanku sai kun raina kanku" yana gama fadar haka yace"Hajiya dake da hadiza gatanan nadawo da ita don Allah ku kara hakuri don Allah"Hajiya mama tace"Bakomai kabiru Allah ya kyauta kawai"Yadakamata tsawa yace tashi kibani guri mutuniyar banza kawai"Da gudu sakina tatashi tana kuka ta fice hajiya suka bita da kallo tana tuna rabon dataga sakina cikin wannan yanayin lalle auren ya bugeta.

Kwamishina  yasa aka kiramasa safeena ya hadasu da Safwan ya musu  nasiha mai ratsa jiki kan su zauna lpy yana tashi tafiya ya ijiyema su momma dubu hamsin ya wuce direba yaja suka wuce ko takan sakina bai kara bi ba.

Safwan yadade tsaye har motar kwamishina tabace mashi kafin jiki asanyaye ya shige barayinsu kai tsaye dakin sakina wacce ke kwance kan gado tana rafzan kuka mai tsaya azuciya ya nufa  yadade tsaye yana kallonta yauce rana ta farko da safwan yaji tsausayin sakina ya tsirgamai asanyaye ya karisa kusa da ita yasanya hannu ya rikota tadago tana kallonsa idanunta sunjajur dasu kurama juna ido sukayi na tsawon lokaci kafin ita ta janye idanunta tayi saurin saukowa daga gado zata wuce yayi saurin riko hannunta tafada jikinsa ya rumgumeta tadinga dukan kirjunsa ammh yaki sakinta dole tagaji tadaina tayi lamo tana kuka shafa kanta kawai yake yana fadin"Srry....banyi wannan auren don na batamiki ba sakina kibar kuka hakanan"Ina saima kara volume take shdai sai aikin lallashinta yake ammh tatafasa batace maiba shiya yimata wanka ya shiryata saboda yadda tazama cikin kwana daya tal,Ita dai kukan ta kawai take ko kallonsa batayi shiyaje shashen su momma yataho da safeena bayan su hajiya sunkara musu Nasiha.

Dakyar da sodin goshi sakina tayarda ta fito falo inda safeena ke zaune tana jiranta tana zuwa tazame daga kan kujera tana gaisheta zuramata jajayen idanunta kawai tayi ammh tak batace mataba to shima kanshi Dr shirun Sakinar yafara batamasa rai haka dai ya musu nasihan su zauna lpy yakuma fadama safeena cewa sakina ya take gareta kada yaji ko yagani ta rainata ita kuma sakina yace takama girmanta itace babba kuma tasani in tazauna lpy to kamar ta taimakeshi ne mganar raba girki kuma yace tafada kwana nawa za"a raba shuru ta musu kawai idanunta na kallon kasa kwallah tataru a idonta kawai sai tatashi ta wuce dakinta wanda tayi hakane kada kukan datake boyewa ya bayyana.

Dr Safwan yabi bayanta da kallo kafin yayi ajiyar zuciya yadawo da kallonsa kan Safeena wacce ke durkushe kasa tana wasa da gefen hijabinta yayi shuru kawai yana kallonta jikinta ne yabata ana kallonta shiyasa tadago karaf suka hada ido ammh me sai taga kamar ma hankalinshi bai tareda ita sam tsuramasa ido kawai tayi tana jin badadi domin ta fahimci Antyna nata bata karbeta amatsayin kanwarta ba.

Hada ido sukayi da ita yayi saurin sakarmata mirmishi kafin ya mike yace"Yan matana don Allah ban minti biyu "yana fadar haka ya bi bayan sakina yana tura kofar yaganta zaune kan sofa ta chusa kai agwiwan kafafunta kai tsaye yakira sunanta tadago da sauri idanunta na fitar da ruwa tace"KA FITA SAFWAN KA FITA BANA SON GANINKA KA FITA NACE!!!tafada cikin karaji idanunta na zubar da kwallah Safwan yayi jagale yana kallonta yabude baki zai yi mgana kenan ta mike tace"KAFITA NACE KO!!!"tana zaremai ido kamar mayya ya lura tarasa natsuwarta dat why yace"iz ok zan fita shikenan ko..?

"yafada yana kallonta juyamai baya tayi tana jin zuciyarta na zafi kamar zata fashe cikin tsausayama sakina ya fice yajamata kofa yadade tsaye kafin ya karisa kusa da Safeena yasa hannu yadagota kawai ya rumgume yana jin shima kamar ya kurma ihu Safeena tanajin yadda zuciyarsa ke fat fat kamar wanda yayi gudun tsere,ahaka yakarisa dasu har dakin safeena gafen gado ya zaunar da ita yana kallonta da shanyayun idanunwa wanda babukomai acikinsu sai zallah desire yace cikin wata murya"yanmatana kidan jirani kadan yanzu zan dawo"Yafada yana rikeda hannunta da kai ta amsa kan tace"Tom adawo lpy"Mirmishi yamata kan ya saketa yafice da sassarfa,bayansa Safeena tabi da kallon tana jin tsausayinshi da wani sonshi na kara shigarta tayi alqawarin bashi dukkan goyin baya wurin yaye damuwarshi.

*Anitha...*

Commets
Share
Vote
Like
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO MY:Mommh Hajja Hadiza Muhammed Ba"are*

*27*

" Yana fita ya shiga mota sai yahuza suya ya siyo gasassun kaji guda biyu yakamo hanyar komawa gidane kiran Tahir ya shigomai yana dagawa tahir yace"Sannu batulu shikenan mun gama ma wahala ko ane memu ko...?Tsaki safwan yaja kafin yace"plz Tahir kakar batamin rai ina alfahari da wannan daren...Kunyi naku nikuma ku barni nayi nawa mana"Tahir yace"Rakiyar siyan bakin kai kadai zaka..?"Safwan yace"Kai wani irin nadawane yaushe kaga ana wannan kauyancin wai siyan baki to ni tuni na siya bakin yan kayata bani bukata kasha zamanka kakula da asibiti kan ingama hutun amarci gwaro na"Yafada yana dariyar keta Tahir yace"Kan ubanchan Allah ya isa"Dr yace"× 2 nima wlh"Yana fadar haka ya kashe wayar yana dariya.

Tahir kuwa chilli yayi da wayar kangado yace"Na rantse nima auren nan zanyi kodan innuna ma gayen nan kuskurensa"Yafada yana fadawa kan katifa kan yace aransa"Gaskiyan Dr Safana yau Daren Alheri ne agaresa niko yaushe zan yi katari da wannan daren alhairin. _Niko nace ga Sahiba zan baka dama tuni take sonka_ wani dirty look yamin wanda tasani ficewa ba shiri _sorry sahiba nayi iya bakin kokarina ammh Tahir yaki amincewa kibari zan ma Mallam yahuza mgana ko yana ciki_😛

Yana adana motarsa a parking space ya shige ciki da sassarfa dakin sakina yadosa yajisa adatse shuru yayi yana jinjina abun kafin ya isa kichen ya bude fridge ya sanya leda daya dayan ledan kuma ya dauko faranti yadora akai tareda kofuna guda biyu ya wuce dakin Safeena inda ya barta nan ya sameta harta zame tadan kwanta karar bude kofan shi yadata ta mike da sauri tana masa sannu da zuwa cikin hanzari ta mike ta isa kusa da shi tana kokarin amsan faranti kallonta yakeyi mirmishi saman fuskarsa yaki bata farantin yanoke kafada yace"Amarya bata aiki koma ki zauna aikin ki na nan zuwa yan matana"Yafada yana kanne mata ido daya mirmishi tayi ta noke kai kan ta koma kan gado ta zauna shikowa ya ijiye faranti akasa ya isa ga fridge din dake dakin ya bude shake yake da madarar hollandian saboda daga shi har sakina abun shansu kenan dat why ko'ina kaduba agidan shi zaka dinga gani.

Dauko guda daya yayi yazo ya ijiye kan Farantin lokaci Daya yana zama a kasa bayan ya Tankwashe kafa yahau bude ledar yana fadin"Sauko yan matana kici daga mijinki"kin tasowa tayi harsai da yagama juyewa acikin farantin kana yataso yazo ya mikar da ita tsaye kan yasa hannu ya zare hijabin jikinta yace yana kallonta"Daga yau na haramtami ki sanya hijabi mutukar muna tare"yafada yana kallonta sunne kai tayi yarikota har zuwa saman kafet din dake dakin ya zaunar da ita yana jawo farantin gabanta naman yayago ya nufe bakinta tayi saurin kauda kai yabata fuska yace"Bana son gaddama Safeena kinsani ko..?"Jin yafadi haka yasa tayi saurin bude baki ya samata yana fadin"good girl....Haka yadinga ciyar da ita ita kuma kunya yahanata sakewa bai matsa mata ba harsai da tace ya isa ya tsiyayamata madarar yabata tasha shima yaci ammh badayawa ba suna gamawa tamike zata kwashe kayan dasukai amfani da shi yayi saurin dakatar da ita yana fadin"Karki bari na sake maimatawa"Tanajin haka tayi saurin sakarmai shi ya kwashe ya kai kichen yana dawowa yace mata taje tayi wanka kai tsaye tace"Nayi fa dazu"Kallonta yayi yace"Bani son......Bai karisa ba tashige toilet da Sauri juyawa yayi yana mirmishi.

Dakinshi yashiga shima yafada wankan alwala yadauro kana yafito yashafa mai yafeshe jikinsa da body spry kayan barci yaso yasanyawa sai kuma yafasa kawai jallabiya yasanya ko boxers bai sanya ba yafito yanufi dakin Safeena fuskarsa na fitar da Annuri.

Yana shiga ya isketa harta kwanta harda uban hijabi gyaran murya yayi kan yace"Kinyi alwala ta amsa da eh ya wuce ya shimfida darduma yana fadin"oya taso muyi sallar godiya ga Allah"tana so tace ai itayi nata ammh ganin yadda yahade rai yasa tatashi sum sum tawuce raka'a hudu sukayi kan yadade yana kwararo musu addu'an zaman lpy da juna da zuru'a dayyiba.yamata tambayoyi kan addininta baiyi mamakin amsoshinta ba cos yasan ko wacece ita suna kammalawa jikin safeena narawa ta haye gado tana fadin"Unku mu kwana lpy"Dariya ta kusa kwacemai yace"To yanmata asha barci lpy" tadade batayi barci ba tana tsoron kar ya hayo gadon hardai barci yasaceta shiyasa sai dayaga barcin yadan yi nisa kana yatashi ya

kashe wutar dakin ya kunna dumlight kafin ya isa kan makeken gadon ya kwanta agefen safeena wacce ke sauke numfashi cikin kwanciyar hankali rumgumeta yayi numfashinta na sauka awuyansa shiyakara rikitasa lokaci daya ya zare mata hijabin jikinta harda dan kwalin yana shafa gashin kanta cikin jan Numfashi kara kamkameta yayi yana jin wani abu na mai yawo ajiki rumgumar da yayi mata shiya data ita tayi saurin bude ido bata ganinsa sai dai duhunsa bai bata zarafin mgana ba ya yadora harshensa kan lebenta yana mata yawo dashi tsam safeena taji tuni jikinta yafara rawa tabude baki kenan zatayi mgna yasamu nasarar tura harshensa cikin bakinta yana kissin dinta in romatic way wayyo safeena  tashiga hannu manya duniya tuni ya rikitata shima ya rikita kanshi cikin zumudi ya jaye mata sikat din dake jikinnta rigar kuwa dayaga zata batamai lokaci yagata yayi ya yarda da ita yar bireziyan ya fincike nonuwanta suka bayyana wow....Ai safwan ya kusa zaucewa dayaji hannunsa kan na shanun Safeena ai arikice yadinga kai musu damka ita kuwa safeena taji wani dadi na kwaranyomata ai sai tadinga toromai kirjin shikuwa yasamu abun so kawai sai ya kifa kanshi yafara mata sucking cikin kwarewa ai nan safeena tafara nishi sama tana tura hannunta agashin kansa cikin fitar hayyaci yadade yana abu daya kafin yagangaro kan mararta yana shafawa a hankali bata fargaba sai da taga yana kokarin zame mata pant tafara matse cinya safwan yace cikin wata irin murya"karki hanani Safeena plz ki barni"Yafada yana wani jan Numfashi ai tuni safeena tafara kuka domin tanaji yadda joy stick dinshi take mata yawo ajiki domin tuni ya cire jallabiyan jikinshi yazama dukkansu sun hada fatarsu wuri daya dakyar ya fincike pant din yaturama hannu...Shiiii tace cikin azaba fingering yahau yi mata cikin zafi zafi ita kuwa safeena Abba take kira da Ummi domin taji abun ya girmeta gani yayi tana batamasa lokaci kawai sai yadanneta yadoramata Nauyinshi akanta yatura harshenshi cikin bakinta yadatseta kawai ya ware mata kafa yadau hanya dodar yana karanta addu'an da Annabi ya koyar damu in mutum zai sadu da iyalansa yana gamawa yadanna kai da karfinsa duk da yasan budurwace ammh baida zabi inaji Safeena tasaki kara daga nan kuma naji dif sai karan fitar Numfarfashi kake ji...Ni to amun afuwa domin naga abunda bai kamata dole nayo waje.

Ina fitowa naga sakina na safa da marwa bata kofar dakinta bata kofar dakin su Safeena tana kasa kunni hawaye yana mata ambaliya fadi take"Safwan kaci amanata kacuceni yanzu ina gidan nan kashiga dakin wata zaka kwana"Sai kuma chan Tazube kan kujera tana kuka mai cin rai duk ta rame lkaci daya....

Dr S AND S ASHA AMARCI LPY

*Allah sarki sakina kin bam tsausayi yauce rana ta farko tunda na fara rubuta book din nan tsausayinki ya tsirgamin...Srry haka kishi yake*

*Anitha...*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar_Janafty_💞

*28*

"Shudewar awa Daya da wani Abu kafin Dr Safwan ya saurarama Safeena wacce tagama galabaita har kukanta yadaina fita sai dai na zuciya,kamkameta yayi na tsawon lokaci yana ji wani kwallah na ziraromai na farinciki bazai ce komai ba ammh safeena ya tabbata Ta dabamce acikin mata shidai baitaba mu'amala da wata macce ba illah sakina ammh bazai iya dora komai ba akan zamtakewarsu ba illah kawai yaji kuma yasani yau ce rana ta farko da yaji zam 100% yadade rumgume da ita yana mata addu'a tareda lallashi mai cike da soyayah da kauna ta har abada.

tashi yayi yafada toilet yayo wanka da alwala zuwa yayi ya shimfida darduma yahau sallar godiya ga Allah da Ni'imar da yayimasa na samu Safeena acikin dubban mata,yadade yana zuba addu'o'insa kafin yakoma yakwanta kusa da ita yana shafa fuskarta yake fadin"Komai naki mai kyaune yan matana.."Yafada yana manna mata kiss abaki.

_gareku yan matan wannan zamanin wlh kukiyaye kanku da biyema mazan wannan zamani to kinaji kuma kina gani mutumcinki shine kikai darajarki agidan mijinki domin samun soyayyah ta har abada wlh tallahi kika banzarta da kanki karema yafiki daraja agurinsa...Allah ya ganar damu Ameen_

Kiran sallar farko Safeena ta farka  taga Dr yana kamkame da ita dakyar ta zame jikinta daya mata tsami tana kokarin mikewa azabar dataji ne yasa tasaki kara"ochhu....Shiya farkar da Dr

dayake barci yayi saurin mikewa yana riketa yake fadin"ina zaki kiyi ahankali fa kinada rauni"Narke fuska tayi tana sunne kai tace"sallah zanyi..."Tafada cikin shagwaba yayi saurin mikewa yana fadin"Ok...Yanzu kuwa"Kan tayi mgana yana ciccibeta sai toilet cikin bath yadireta yahadamata ruwa masu zafi da kuka da komai yasamu Safeena ta shiga ruwan zafi ruwa biyu ya chanzamata kafin yabarta tayi wankan tsarki,fitowa yayi zashi dakin shi yaga sakina kwance akasa afalo daga gani barcin yadauketane bata shiryaba turus yayi yana kallonta kan ya isa kusa da ita ya dan bubbugata yana kiran sunanta...Firgigit ta mike tana fadin"Don Allah Safwan karka kwanta da yarinyarnan.."Tafada azabure da alama da abun ta kwanta kuramata ido yayi yana kallanta kan yace"meya sameki kike barci anan..?Saurin mikewa tayi tana kallonsa kallo na kurullah shima kallonta yake da mamaki afuskarsa cikin fitar hayyaci tace"Ka kwanta da ita ko..?"Tafada tana kamo hannusa Safwan galala yake kallonta kan yace"wa ..kenan...?Tace"Amaryar ka don Allah kace baka kwanta da ita ba"kallon cikin idanunta yake kan yaji dariya na neman subucemai yadda yaga tayi wani kalan tsausayi yace"Dama nayi miki alkwarin bazan kwanta da ita bane..?

Yafada yana hade rai kan ya fizge hannunsa yace"kinga wlh ki natsu sakina kada ciwon zuciya yakamaki don naga kina gab"Yana gama fadar haka ya wuce dakinsa ai sakina sai ta sulale tana fadin"shikenan wlh ya kwanta da ita...Shikenan wallahi safwan kagama kasheni"Haka take maimatawa kamar wata zararriya Kafin kuma tadiba da gudu tashige daki tana kuka kamar makauciya sabon kamu.

Wanka ya sake yi yayi alwala massallaci ya wuce saboda yaji an tada sallah koda ya fito baiga Sakina ba tsaki yaja yace"kawai mata kinsa kanki adamuwa kinason mijin naki kika banzarta dashi.

sai da gari yayi sha kana yadawo daga massalaci saboda anyi wa'azi ne shiyasa yadan jima koda yashiga dakin Safeena har tayi wanka tasanya wata bakar doguwar riga kirar armani tana kwance akan gado karisawa yayi yana mata mirmishi kauda kai tayi tana tura baki fuskarta tayi fayau da ita dariya ya saki yana fadin"ok kari kikeso to gyara..In dada miki daman bai isheni ba'yafada yana haurowa gadon saurin dira tayi tana fadin"wash...Yadda taji zafi akasanta saurin biyota yayi yana riketa yace"oh am srry....Kirinka bi ahankali fa kinsan kina da rauni"Tura baki tayi tace to ba kai bane kace zaka kara ba"Dariya yayi yace"To ai kene naga kinason kari"Tayi saurin cewa"Ni yaushe nace"yace yanzu kika fada'diddira kafa zatayi sai taji zafi sai tayi saurin fadawa jikinsa tana mai kukan shagwaba shikuwa yana mata dariya yana fadin"Zaki sanine...Inkika fama ciwonki baruwa na ni sai dai in kara famamiki shima.

Nan suka lalace tanamai shagwaba yana biyemata Momma ce takirasa tace"ga abun karyanwansu yazo ya amsam musu to yace dakyar ya yakiceta yaje ya amso mash hajiya

mama sai wani kallonsa take tana fadin"Ango mijin amarya ansha maiko"kasa kallonta yayi saboda kunyan data basa dundu tabugamai abaya tana fadin"Dan nema sai yanzu kake jin kunyata ko..?"Mirmishi kawai yayi iyami ke karemai da matar kawu bala Adil ne ya makale masa dole yataho dashi Safeena ta amsheshi tana murna tace"Oyoyo....Dana dakai na kwana arai"Tafada tana chabesa Dr yace yana ijiye kwandon breakfast din"Ke dai fadi gaskiya dashi kika kwana koda baban yaron"Yafada yana wani kallonta hararar wasa ta mai kan tace ashagwabe"ai ni ba ruwa na da baban yaro tunda bai da tsausai"jagale yayi yana kallonta kan yace"To bari in maida yaro...Sai baban yaro yanuna miki ainihin kalan rashin tsausayin"Tana jin haka ta rumgume Adil tana fadin"a'a kana da tsausayi sosai ma kuwa ko yarona"Tafada tana kallon Adil  shikuwa ya barke da dariya kamar yasan me ake yi Safwan yakuramusu ido kawai cikin sha'awa da burgewa zuciyarsa kamar zata zama takarda saboda fari.

Atare suka karya suna yi suna hirar kauna shikuma Adil daga yayi tsalle ajikin safwan sai yayi a jikin Safeena shikanshi Adil yasamu farinciki...Allah sarki yaroma kenan.

Sai zuwa yammah suka je shashen su momma lokaci yan Safana zasu tafi haka suka tafi kamar kar arabu Hajiya mama harda hawayenta da suka tafi sun dade shashen nasu shida safeena Hajiya mama tatasu da hirarta shidai danne danne yake awaya bai jinsu sai dai ita safeena ke samata baki sai da sukaci tuwon acchan da momma tayi da miyar kubewa kana suka koma barayinsu wanda dakyar aka bambare Adil ya makale shi sai ya bisu Hajiya ko ta amsheshi da karfin tana fadin"Kai kaga yaro da munafurci yana neman hana ubansa cin amarci"Ai sum sum suka fice da kunyar hajiya mama.

Sakina kuwa kuka ta wuni yi adaki gashi Anty laila ta kirata tana dura uban ashar tana fadamata ita ta zauna harshi safwan din wata tsiyace balle amaryansa da har zata zauna wata kishiya tadagamata hankali to tayi maza ta mike ga kanta tunkan ranar Nadama tazo mata...Kashe wayar kawai tayi tana kara fashewa da kukan ita Anty laila tana wani mgana batsan abunda takeji azuciyarta ba dabata fadamata hakaba ita yanzu bata da Natsuwar da zata gane menene yakamata tayi ita dai gatan nan ne dai bata da aiki sai kuka kullum abincinta hollandian sai ko in tasa yan aikinta sun dafamata indomie shima bada yawa take ci ba taji ya fita ranta kasuwancinta kuwa yayi kasa domin sai kranta ake kayan su yi kasa kuma gashi bata sake yo odar ba to inata ga kwanciyar hankaki tunda Safwan yayi auren nan gabadaya komai nata ya tsaya cak.

BAYAN SATI DAYA

Hakika acikn satin dayan da Safwan da Safeena suka kwashe atare sun gurji amarci iya son ransu wanda Dr ya zabura ya kusa cirema safeena kunya ammh har yanzu da saura sun murji juna wanda dukkansu suka murje sukayi kiba abunsu Hatta Adil yayi bul bul dashi kamar dan turawa,Tsakaninta da Sakeena gaisuwa in tafito falo ammh ko kallonta batayi itada bazata daina gaisheta ba domin ko amusulunci tafita hakkinta tun tana kwana uku agidan tacema Dr zata fara girki tahutar dasu momma haka nan yaso yahana ammh ta dage harda neman yin kuka dole ya barta kullum ita da danta zasu yi ta burumtunsu ita tana aiki shikuwa da rarrafe yaita barna inta kammallah aikinta tamai wanka ita tayi su shige sashen su momma sai kuma Dr yadawo wanda adaddafe yayi hutun kwana biyar yakoma asibiti.

Yau din kuma zai koma dakin Sakina wanda daga shi har safeenar kamar marasa lpy haka suka wuni sukuku dako yadawo bayan sungama taking dinner wasa yake da Adil ammh safeena tayi shuru kawai sai da Adil yayi barci kana yakaisa kan gadon yakwantar dashi kafin yazo inda safeena ke zaune kan stool din gadon ya mikar da ita yana kallonta itama shi take kallon kan kwallah datake boyewa ta gangaro saurin fadawa tayi jikinsa tana fadin"Unku...Shikenan nikadai zan kwana"tafada da sheshekan kuka runtse ido yayi kan yace yana rumgume da ita"Hakuri zakiyi yanmatana daga gobene zandawo mu kasance tare kuma ga danki nan yatayaki kwana"Matse hawayenta tayi dagota yayi yana kallon yadda hawayenta ke sauka harshensa yasa yana daukemata su kafin ya dora harshensa kan lebenta yana zagayawa dashi cikin kwarewa ta bude bakinta ta chafki harshensa ta rike kansa kam tana sumbatarsa cikin shauki da kauna mai dorewa shima kara hade kugunsu yayi wuri daya yana kara damke harshenta sun dade ahaka sai da taga hankalinshi na kokarin barin jikinshi kana tayi saurin fizge jikinta tafada toilet saboda jitayi wani abu ya tokaremata amakogaro yadade tsaye kan ya fice jiki asanyaye yacewa"Kar ki manta da addu"A inzaku kwanta,daga haka ya fice

Tadade abayin domin tagama kukanta wanka tayo da alwala tazo tayi shafa'i da wuturi ta sanya rigar barci tazo ta rumgume danta ta musu addu'a suka kwanta ammh bawai don barci zatayi ba a'a sai don bata da zabi ne.

Shikuwa dakinsa yayi direct sai da yayi wanka yayi sallar sa yasnya kayan barcinsa riga da wando masu ruwan toka masu taushi,ya feshe jikinsa da body spry kana ya nufi dakin sakina ammh sai da yataba dakin safeena yaji akulle kana ya murda na sakina yaji abude yasa kai yashiga da sallama.

*Shakira..*

Commet6
And
Share
Vote
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*29*

"Dakin yayi dumlum da duhu shiya sa hannu ya kunna makunni wutan abunda ya bashi mamaki yadda dakin yayi kaca  kaca chan kaya chan plate din abinci akan gado harda su kofuna da ledojin bickut...Kuma abun takaichi Sakina na zaune atsakiyar gado ta tusa kanta atsakanin kafafunta cikin dakiya ya karisa kusa da ita yana fadin"Shin wai sakina kinyi haukane...Kiduba inda kike zaune fa..?

"dagowa tayi tana kallonsa saida ya razana da ganin yadda idanunta yakoma jawur gashi kan nan dayaji attac duk yafara cirewa gayinan dai ba kyan gani jikin ta kuwa riga da dabam sikat dabam kallonsa take cikin fitan hayyaci kan tace cikin shakakkiyar murya"Bbu ruwan ka da muke damuna mallam ka fice min adaki don na tsaneka"daure fuska yayi kan yace"Bazan fita ba wai ke meke damunki kanki farau kishiya...Oho nazata bani da wani amfani agareki banzaci innayi aure zaki damu ba ai"Yafada yana wani zakuda kafada kukan kura tayi tadiro  daga kan

gadon ta chakumi wuyansa tace cikin karaji"Daman don kaga iyakata kayi ko safwan to wlh yadda ka ruguzamin rayuwa kaima saina ruguza naka"Ransa ya baci yasa hannu ya fizge rigarsa kafin ya tunkudata ta fadi kan gado yace rai bace"Nafi karfi inyi abu saboda ke Sakina..kina sona kikemin abunda kikemin kike banzarta dani kamar wani wawanki wani dama ne banbaki ba eye..?Ammh kika sa kafa kika shure kekina ganin kin isa kowa to wlh bari kiji infada miki in wani abu yasamu matata wlh tallahi kinji na rantse kotu ce zata rabamu ni dake kuma in kin musa ki kwatanta Nonsess kawai"Yana gama fadar haka yajawo blanket din dake kan gadon da filo ya jefa kasa yashimfida kashe wutar yayi yakoma ya kwanta ransa na masa kuna.

Daskarewa sakina tayi akwance kukanma ya kasa zuwa mata gyada kai kawai takeyi tanaji aranta zama bai ganta ba itace yau Safwan yama wannan bangazan yake kuma yabamata mgana son ransa harda kotuce ce zata rabasu in Tatabamai mata tabdijim wlh yadebo ruwan dafa kansa don kowa agidanan sai ya gane kuransa,kwanciya tayi tana sake saken zucci na yadda zata rama dukkankan abunda aka mata.

Kiran sallar farko ya farka dama akagare yake yatashi ya fice dakinsa yayi alwala kan yafice zuwa massallaci kotan sakina bai bi ba koda yadawo yasamu kira daga asibiti ashiryeshi ya iske Safeena ita da danta akichen suna soya wainar kwai Adil yadauka yana masa wasa ita kuma Safeena natsaye sanye da riga da sikat yan kati da hula akanta ta harde hannunta akirji tana kallonsu dagowa yayi suka hada ido tasakarmai murmishi,shima ya mayarmata sanye cikin american suit red and blck suit dinsun amsheshi matuka yar briefcase dinsa ke makale akafadarsa  kallo daya tamai ta fahimci baida fara"a kallonsa tayi kan tace'ina kwana....Ya amsa da "Lpy kalau ummi Adil yakuka tashi ta amsa da lpy tana kallonsa saurin fita yayi yana fadin"Zan makara yanmatana zo ki karbi danki"kashe gas din tayi kan ta fito tana fadin"Unku baka fa karya ba zaka fita"Kallonta yayi kan yace"Na makara sai dai in nadawo....Yana fadar haka ya mikamata Adil ta amsheshi shikuma ya fice  binsa tayi da kallo tana mamakin mai ya batamasa rai haka.

Ko achan hospital kowa ya fahimci baida walwala hatta tahir wanda bai ma tambayesa ba domin yasan duk sanda yaga Dr Safana awannan yanayin yasan mutum dayane ke sauya Dr Safana wato SAKINA.

Koda yadawo baiwani sake ba saida Safeena tadinga jansa da hira shiyasa yasaki ransa yau ma abun jiya aka maimata akasa ya kwana wanda ko mgana bata hadasu da sakina ba shi da badon yasan darajar aure da adalchi ba har Sakina ta wulakantasa never domin yanzu ba da bane.

*****

Kwanchi tashi Asarar mai rai gashi yanzu watan su Safeena biyu da tarewa gabadaya rayuwarsu ta chanza ita da Safwan da Adil domin suna cikin farinciki da Annushuwa hatta su momma suma sun ga chanji saboda su yanzu girki sai sunga daman yi domin Safeena ta daukemusu komai ita keyi in tagama abunda zatayi sai takoma shashensu suta hira da dariya da hajiya mama.

Ga Adil yanzu watansa goma sha daya gudu ba inda baya zuwa mami kuwa abakinsa da Abbu da hajiya da momma radam abakinsa ya Iya fada safeena ta shaku da Adil matuka bata son abunda zai tabashi kwatakwata tana jin dadin zaman gidan fiye da komai gashi Dr ya siyamata sabon waya kullum sai sunyi waya Da Ummi tana kara bata shawarwari wa'inda zasu amfaneta.

Ada Sakina bata cika fitowa ba ammh yanzu tachanza taku domin afalo take wuni in ko Adil ya kuskura yayi gefenta wlh sai yadawo da kuka itakuwa Safeena ko kallo bata isheta ba domin har abada bata da lokacinta kawai tana gama basu dama ne saura kiris abunda ta dana musu yatashi dasu.

*Janafty...*

Commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*30*

"Mtsala ta farko da sakina tafara fuskanta shine na danta ADIL....wanda indai yana wasa afalo tashigo yanzu zai yanka ihu yatashi da gudu yabi safeena daki ko kichen inko tace zata daukeshi yadinga yanka ihu kenan kamar yaga dodo sai Safeena tazo ta daukeshi tana rarashi yana kuka yana fadin"Mami....Yana nuna sakina,sai Safeena tasabashi su koma daki kana zaiyi shuru.

Abun yana damun Sakina matuka domin koda take rashin kula Adil bawai batason shibane yaza'ayi mutum yahaifi da da cikinsa yace bayason shi wannan ma ai karyane,tana son danta kawai abubuwane suka mata yawa ciwon abu biyu tahade mata ga na kwatar miji gana d'a domin yanzu Safwan tsakanin shi da Sakina ido ko kula da yadda take rayuwarta bayayi saboda shi yanzu kwanciyar hankalinsa kwanciyar hankali Safeena da gudun jininsa.Hatta da su momma sai suyi sati basu sata a ido ba Hajiya mama ko aranar data shigo shashen ta iske Sakina zaune afalo dariya tahau tsintsurawa tana fadin agaida uwargida sarautar mata shiyasa bahaushe yace kada kayi wasa da damarka domin watarana matsayin daka ke adama rasashi

kakeyi,babu shakka tasan da ita takeyi shiyaasa sum sum ta shige daki ranta na mata suya tana son tadawo Sakinarta tada ammh tarasa yazatayi.

Yau Tun safe Dr Safwan ya fice bayan yar rigiman sa Safeena tagama kukan Ita Umminta takeson gani tun yana lallashinta har yazo yana binta da ido domin kowani dakika kaunarta kara zurfi take aranshi,bawai bayason tafiyar nata bane A'a yadda Safeena tazama tallafinsu shida danshi yakeji kada suyi maraici,tana fushin yafice ya barta.

Sau wurin sha biyu tafito daga daknta Adil na biye da ita kamar jela yana mata gwarancinshi sanye take da wata atamfa milk and green riga da sikat kayan sun amsheta tayi daurin ture kaga tsiya ta daure gashinrta da band,tarasa mai zata dafa kawai sai ta soya musu doya tayi miyar kwai ta kammallah kenan taji ana sallama da sauri ta fito tana amsawa.

Wasu mata tagani guda biyu dayar tafi manyanta dayar kuma yarinyace dukkansu kallon banza suke binta dashi kamar sunga kashi Safeena taji gwiwarta ta sake tace cikin sanyi murya"Sannunku da zuwa...Ku....ke dallah rufema mutane baki"Anty laila kenan ta katseta tana binta dawani matsiyacin kallo Hajiya kari tace'yo kekuwa dole tamana sanabe mana anzo gidan daula anrabu da cin gabza"safeena taji wani abu ya tsayama amakogwaro kafin tace wani abu Adil ya fito daga daki dagudu da wayarta yana fadin"Mami....Mami...Abbu...Yana mikamata wayar alamar ana kira Amsa tayi tana shafa kanshi Dr ne ke kira shiyasa ta barshi.

Hajiya kari da laila suka hada ido suka futar lokaci daya"MAMI....."da mamaki afuskarsu kafin Laila tace"Hajiya kamar fa Adil ne fa yagirma hajiya kari tace"Shine Nima nayi mamakin girmansa rabona fa dashi tun haihuwarsa"Laila tace"Nima inaganin tun lokaci ammh naji yana cema watanan mami fa"Tafada tana kallon Safeena datake rumgume da Adil dake binsu da kallon rashin sani.

Hajiya kari tace'Ato sakarcin sakina ne baki sani ba"Tafada rai bace ai laila da hanzari ta ficikosa tana fadin"Bazai yuyuba kin asirce uba kuma ki asirce d"a ba.."Yako tsandara ihu iya karfinsa hajiya kari ta dunguremasa kai tace"Kinganin mun munafukin yaro kaci gidanku ni nan daka ganni kakankace ita kuma wannan yayar uwarka"Tafada tana nuna laila kana ta nuna Safeena dake daskare awurin hawaye sun taru a idanunta tace"Ita kuma wannan kishiyar uwarkace ga uwarka chan wacce tayi nakudarta"tafada tana figan hannunshi ta wuce dakin

Sakina dashi laila ta marata baya shikuwa Adil kuka yake yana mika hannu yana ta kiran"Mami.....Mami...ita kuwa hajiya kari nakara jansa tana fadin"Ko zaka mutu sai kabar mamin don ubanka".

Safeena da kuka yakwacema tashige daki da sauri tana maida kuka gefen gado tazauna tana sharen hawaye aranta tana addu"an kada Allah yabasu ikon Rabata da Adil domin wlh bazata iya rayuwar gidannan ba yaron nan akusa da ita ba.

Sakina na kwance akan gado su laila suka shigo cikin mamaki ta mike tana kallonsu rike da adil dake ta kuka harda hawaye,cikin mamaki su hajiya ke kallon sakina tareda bin dakin da kallo laila tace"Sakina....Haka kika maida kanki ashe..?"Sakina ta tabe baki kafin tadiro daga kan gado sanye da breziya da under bako kaya tace"Eh....Haka Safwan ya maidani Anty"Tafada tana fashewa da kuka rumgumarta Anty laila tayi tana lallashinta hajiya kari ta damkafar da adil akasa tana fadin"Kama ma mutane baki wlh ko in mauje ka munafinki yaro"Sakina ta saki laila tana fadin"Hajiya kuma kungani ko wlh yaron nan in yaganni kamar yaga dodo"Tafada hawaye yana zubo mata hajiya kari tace"badole yamaidake dodo ba tunda kin zauna kin maida kanki sakarya mara wayo har ita waccan sillan kara wata abace dazaki zauna su ruguza miki rayuwa'Sakina ta tsananta kukanta tana fadin"Ya zanyi hajiya ya zanyi wlh narasa ma ni mai zanyi"Anty laila ta riko hannunta zuwa gefen gadon tazaunar da ita tana fadin"shine dalilin dakika bar kasuwancinki ya ruguje ayanzu haka shagonki na kano an rufesa coz bbu kaya why sakina zaki sakaci da rayuwarki ta tarwatse lokaci daya"Sakina ta share hawayenta tace"Ni bata shago nake ba ta yadda na zama bola agidan nan shi yafi damuna ku fadamun yazanyi"tafada hawaye na kwaranyomata Hajiya kari tace"Abunda zaki ki mike ga kanki kidawo sakinarki danki kuma da ake miki iko dashi ki karbi abunki domin ba uwar wani ya haifar miki ba wlh sakina in har baki mike kin kwaci yancinki agidan nan ba to na yarda ke ba nonon karimatu kika sha ba"Takareshe fada da bacin rai Sakina tace cikin kuka'zanyi hajiya zan nuna miki nidin yar karimace ta halas ma kuwa"Hajiya kari tace"ke kefa kici mutumci duk wanda yanemi yadakatar dake koda uwarsa cw"Laila tace"Ai sune munafukai baran wannan katafiriyar tsohuwar mai kalan yan duniya"Sakina tace"Ai itace ke juya safwan din inaji ko auren nan ita tayimai shi"Laila tace"Yar tasha ita lokacinta ubanwa yasa amata kishiya"Hajiya kari tace'ai karta aragama kowa harda ita tahada taci uban shegiya kota koma kauye inda aka fito tana wani ji da baki kamar fanteka🤣🤣gabadayansu dariya sukasa harda tafawa.

Koda suka waiga ba Adil ba dalinlinsa ashe suna chan suna mgana ya sulale yakoma gun Safeena wacce taci kuka ta koshi yana ko shigowa yatafi ya rumgumeta yana ajiyar zuciya alamar yasha kuka rumgumesa tayi tana dariyar farinciki.

gabda la'asar sukayi shirin tafiya bayan sun cika sakina da mugayan shawaransu wanda bazai bulle da ita ba saima karin jawoma kanta wata fitinar...kwamishina bayanan yaraka gwanna jigawa shiyasa sukasamu zuwa domin ido yasanya musu ko laila yace tadaina zuwa sai anyi wani abu kwakkwara tukun..

Sakina ta rakosu kenan suka ga hajiya mama zaune adan barandansu ta shimfida tabarma tana jin radio ta sai gasu sun fito sun yi tsam da suka ga hajiya mama ammh sai suka waske itakuwa hajiya mama harda cemusu bata gansu wurin biki ba adakile hajiya kari tace"Sunyi tafiyane shiyasa...Suka shige motarsu laila ke jan motar suka fice hajiya
mama tabisu da gwalo.

*Anitha...*

commet
And
Share
Vote
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*31*

"Sai karfe 10 dawani abu na Dare Dr yadawo wanda Safeena da danta sun cakare suna tsumayinshi sanye take dawani riga da wando na pakistan pick colour batasanya gyalen kayan ba sai ta daure gashinta dashi ta sakeshi shikuwa Adil cikin riga da wando yan kati ammh wando gajerene,yau din tuwon semo tayi mishi da miyar kubewa danya sai lemon abarba dayake Dr bai cika cin abinci asama ba dat why take shimfida mai babban darduma afalo su zauna suci ko adaki.

yau din ma haka ta kasance afalon suka baje suna kwasan tuwonsu Dr naci yana zuba santi safeena da danta suna faman mai dariya kallonsu kawai yake azuciyarsa yana godema Allah dabai bijirema hajiya mama Ba dako yayi asara abubuwa mafi muhimmanci yau din kam bbu sauki domin kodaga irin kallon dayake binta dashi tagane akwai bayani dayake yau yadawo dakinta itama binshi take dawani sirrin kallo mai tsayawa azuciyar masoyi mirmishi yayi yana dafa hannunta yace"Ko acikin dubban mata keta dabamce yanmatana shiyasa kullum nake alfaharin samunki amatsayin matar aurena"tsadadden murmishinta ta sakarmai kan tace"Kaima acikin dubban maza ka bambamta wlh tallahi nafi kowacce mace samun sa"ar Adalin miji irinki Uncle"Tafada tana mai kura masa ido kuri sukama juna suna aika ma da juna kalamai wanda baki bai iya furtawa sai dai kawai ido yanuna da kuma hannu ya aikata.

Karar bude kofa ya fargar dasu suka bi inda karan yake Sakina ce tafito cikin wata doguwar rigar  less kayan su amsheta duk da ta rame ammh tayi kyau abunta kallon su takeyi kan tawani tabe baki tace"Andai ji kunya....Wlh"Wucewa tayi kichen tana sakin tsaki da kallo safwan ya bita yana mamakin chanzawar sakina kallon Safeena yayi kan yace"Anyi baki ne yau ko..?yafada idonsa anata cikin inda inda tace"Am....Eh Anty tayi baki"Mirmishi yayi yace"no wonder...Safeena ta kallesa shima ya kalleta sai ya waske da daukan Adil yana fadin'!maman Adil me kika ba yaronki ne yazama lukuti haka"Dariya tace"Tuwo miyar kuka"Yace"wow...Gaskiya kam koda nagani kinganni nan dad dina na biyo domin shi abincinsa gargajiyane shiyasa nake kara godema Allah daya bani mata daidai da ra'ayina"mirmishi ta mai kawai mikewa yayi rike da Adil yana fadin"Ke kinga nagaji dawannan jan ran...Kisame ni a dakina"Mikewa safeena tayi tana cewa"Yau kuma mulki akeji yace"Eh...Nima sai naja ajina.

Kwashe kayan tayi dasukayi amfani dashi takai kichen tana shiga taga Sakina na tsaye tasanya latifa yar aikinta tana dafamata indomie sai masifa take wai anmaida su gida gidan tuwo sai rufe hanci take tana fadin"Tsiyar a kawo maka dan kauye agida kenan baisan komai ba sai kauyanci"Ita dai Safeena kala bata ce mata ta ijiye ta fito tawuce dakinta aranta tana fadin"Bazan biye miki ba tunda nagane halinKI ko mijin naki ma baki kyale ba.

wanka tayi da Brush kana tazo ta sanya rigar barci wata karamace mai siririn hannu komai na jikinta ana gani pant kawai tasanya saboda sanin halin dr baison wani abu yamai shamaki, humranta da inna husai tahado mata ta yi ambaliya dashi zani ta dora kan rigar ta sanya hijabi tafito taja kofanta ta nufi dakin Dr.

Koda taje ta iskeshi har Adil yayi barci ya sanya sa kan dan gadonsa dake dakin dr yana zaune yana duba abu acikin kwanfutarsa tashigo tana shigowa tayi wurgi da zanin da hijabin tataka cikin takun ta na kasaita ta isa garesa kamshin turarenta shiyasa yadago yana binta da mayen kallonsa cikin zakuwa ta rumgumesa ta baya ta sakalo hannunta tazage cikinsa tadora kanta wuyansa tace cikin karyayyiyar murya"Unku...Gani takareshe cikin shagwaba tagama kashe mai jiki dat why yamata shuru kashe na'urar yayi ya ijiyeta kan doruwar dake gefensa ya birkitota yana binta da mayen kallo yace cikin kasala"sai da nagaji da jira to nama fasa"Yafada harda tura baki dariya tayi tace"Sorry zumata....ga madarar ka nan kasha sai kagaji don kanka"matse mata baki yayi yana yana fadin"Nine zuma ko"yafada yana kallonta tace"Kafi zuma dadi ma"Sai da tafada taji kunya dariya yayi yace"ehyye....Yanmatana haka kike"sunne kai tayi akirjinsa  tana dariya rumgumeta yayi yana fadin"to shikenan bari in baki zuma ni kuma kibani madara daga haka yasanya hannu ya rage wutan dakin yayi saurin doramata nauyinshi suka fara sumbatar juna cikin kwarewa.

Yau sun makara sai 8,Dr ya fita office cos akwai meeting  din da zasuyi da sauran likitochin asibitin breafsat ma a tsaye safeena ta matsa masa yasha ruwan tea...Ko shashen su momma ma a tsaye ya shiga.

Tun fitanshi Safeena takoma daki domin yau tun safe taji zazzabi na neman kamata kana bakinta na tsinkewa batajin dadin komai shiyasa tana yin wanka tama adil takoma ta kwanta ta hadasa ta kekensa da abun wasansa takoma ta kwanta yafita yana ta wasansa.

Sakina sai yanzu ta fito daga daki tana hamma kichen ta shiga ta hado tea tazo ta zauna afalo ta kunna talabijin ana wani film a mbc2 tana nan zaune sai ga Adil ya fito kan kekensa yanata wasansa kuramasa ido sakeena tayi tanajin wani sonsa na kwararamata acikin rai kawai sai ta mike tsam ta isa kusa da shi ta sanya hannu ta daukesa aikuwa tana daukan shi ya tsala ihu ranta ya baci tace"kai rufemin baki ina uwarka indauke ka ka hau ihu",shuru yayi yana kallonta hawaye na zubo masa sai kuma taji tsausayinshi rumgumesa tayi tana fadin"srry my boy...Kaine

kaban haushi"ai tana fadin haka yakara tsala ihu safeena dake barci taji ihunshi kamar amafarki zumbur ta mike taji kuwa daga falo ne takejin kukan da gudu ta fice hartana bigewa da gado.

Tana fitowa taganshi hannu Sakina tayi saurin isa tana fadin"Me kika mai...?"tafada arude jin yadda yake tsala kuka yana ko ganinta yafara zillo yana kiran mami yana mika hannu, tasanya hannu zata rikesa sakina ta jaye tana bin safeena dawani matsiyacin kallo tace"kul.....Kada kikara dora ahannuki ajikin dana kuma da kike tambayan mai na mai ai dana ne komai na mai nina haifesa"Galala safeena tayi kwalla ta cika idonta tace"A'a ba nufi kenan Ba...Naji kukansane nazata faduwa yayi"Sakina tace"to yana hannu uwarsane sai ayi gaba"Tana fadar haka ta juya zata koma daki ..Kamar daga sama sukaji muryan Dr cikim dakewa yana fadin"ADIL BA DANKI BANE, SAKINA DAN SAFWAN NE DA SAFEENA"yafada yana takowa tsakiyar falon mantuwa yayi yazo daukan file yadade tsaye tun farkon mganan yanajinsu.

dawowa sakina tayi kan tace"Da ubanwa ya bata..?"Kai tsaye yace"Uban yaron ya bata shi halak malak.."Sakina tajuya kawai tasanya Adil adaki ta kulle kana ta dawo tana cewa"Baka isa ba safwan wannan karan sai dai duk abunda zakayi kayi ammh na amshi dana"Wani sakaran kallo yake binta dashi kafin yace"Wai ma wanene dan naki ne..?"Cikin dakewa tace"Adil ne dana mana ko inada wani dan ne bayanshi"Cikin fusata yace"au sai yanzu kikasan danki ne sai yanzu kikasan kina da wani dan' kinmanta sanda kika banzarta dashi,kin manta sanda kika hanasa yaji duminko lokacin dayake bukatarki kika ki shayar dashi kikaki rainansa kika ki basa kulawa kika banzarta dashi kika wofantar dashi shine kike kiran kanki a matsayin uwa tirr da mai hallaya irin taki baki dace da akiraki da suna UWA BA"

Hawaye ya gangaroma Sakina ta nuna kanta tana fadin"Nikake ma Tirr Safwan'ko kallonta baiyi ba yawuce ya bude daki ya dauko adil yaci kuka ya koshi ya mikama Safeena yace " _KO BAYAN RAINA KECE ZAI CIGABA DA KALLO A MTSAYIN MAHAIFIYARSA....KEKUMA KI KALLESA A MTSAYIN DA' NA HAR ABADA_ Safeena ta amsheshi tana fadin"Insha Allahu zan kula dashi kamar yadda duk wata uwa zata kula da danta"mirmishi yayi mata kan yace"Nagode hanyar dakinsa yayi aikuwa Sakina tayi kukan kura ta isa kusa da Safeena ta bangajeta ta fadi ita da Adil kan ta daukeshi tana fadin"kunyi kadan na bar miki dana in nabar miki mijina wlh bazan bar miki dana ba.

Safeena dake dafe da ciki da kurma ihu Ai da gudu Dr Safwan ya isa gareta yana rikota tana dafe da ciki tana kuka yana duba kasan kafarta saiga jini cikin tashin hankali da karaji yace" *SAKINA.....!WLH TALLAHI IN KIKAMIN ASARAN KWAN HAIHUWA SAI NA MAKA KI A KOTU* tsam ta tsaya tana kallonsa kan tace"Shege kafasa Safwan dama dan adam da butulci

akasansa asibitin dakake takama dashi inace ba ubana yataimaka maka ka bude sa ba to indai har baka sake ni ba BAKA CIKA DAN HADIZA DA SALE BA"cikin wani bakin cikin Safwan ya saki safeena ya isa kusa da Sakina yana kallonta idanunsa sun kawo ruwa yace"Tabbas da taimakon mahaifinki nake wannan matsayin ai banzata kina kallona da abun ba....To ammh yau ya kare ni _*NI DR SAFWAN SALE SAFANA ZAN NUNA MIKI NI DAN HALAS NE....KIJE NA SAKEKI SAKI DAYA!NA SAKEKI SAKI BIYU!NA S........*_ A'a kada ka karisa kada ka karisa Safiyanu"

Hajiya mama tafadi haka da karfi ita da momma ce suka shigo tun bayan ihun da Safeena ta zabga hajiya mama tace"Kabarta haka Safiyanu ko ahaka ka barta kanuna mata kai dan halas ne"Juyawa kawai yayi ya isa inda safeena ke kwance momma na rike da ita ya ciccibeta yana fadi cikin raunin murya'momma muje asibiti inaga Safeena bari zatayi" da sauri momma ta mike tana salati ta rufamasa baya har yakai kofa yace"Hajiya ki karbi Adil don har abada ba danta bane"Yanagama fadar haka ya fice dauke da Safeena.

Sakina dake tsaye kamar mutum Mutum hajiya mama ta fizge Adil tana cewa"Naso ki gane kuskurenki tunkan saki ya shiga aurenku ammh kash...Kin kasa ganewa ammh ina fatan wannan karon ki gane KIN TAFKA KUSKURE

Daga haka ta fice dauke da Adil....Ai Sakina zubewa tayi cikin firgici da tashin hankali tana fadin"na shiga uku wlh Safwan da wasa nake maka wayace ka sakeni wayyo ni...Sakina na mutu na lalace"

*Hmmmm....Ai kinyi kuskure ba'a wasa da abunda bana wasa ba Allah ya kyauta*

Commet
Share
Vote
Like

Share

*Anitha...*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE.."!*

*Wattpad:Janafnamcy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*32*

"Momma ta shiga motar direct suka wuce S&S SAFANA SPECIALIST HOSPITAL Ma'ana asibitinsa suna zuwa suka rufi kanta dashi da Dr. Tahir don bai yarda sauran sun tabamai mata ba Alhamdulillah sun gano ciki dan sati hudu da kwana biyu wata daya kenan,buguwar datayine jini ya yanke mata anyi saurin xuwa asibiti dat why cikin bai zubeba sun yi nasarar tsaida jinin suka mata allurai suka kaita dakin hutu.

Sakina tadade tana kuka nadama mai karfi ta shigeta lokaci daya domin tasan duk takamarta da Safwan take gashii yanzu ya saketa ina zatasa kanta yanzu...yan aikinta ta kira suka hada mata kayanta kaf bazata iya tuka mota ba saboda halin datake ciki direba tasa yakaita tasha ta hau mota sukuma su latifa taba kowannesu na mota tace su koma gida tareda albashi.

Sai yammah ta isa katsina dan adaidaita ya sauketa tabashi kudinsa mai gadi ta kwalama kira yazo ya jidan mata akwatuna yana kaiwa cikin gida Hajiya kari dake zaune afalo tana kallo taga ana shigowa da akwatuna saurin mikewa tayi tana fadin"Kai daga ina kuma..?

"Bai bata amsa ba Sakina ta sawo kai Falon sororo Hajiya kari tayi  tana binta da kallo da gudu

Sakina ta isa ta fada jinkinta tana Fadin"Hajiya ya Sakeni wlh ya sakeni"Cikin karaji hajiya tace"Yame....."Sakina tace"ya sakeni hajiya safwan ya sakeni"

Ya sakeki kuma shine kika zomin gida"Muryan kwamishina ta katsesu wanda ke kofar falon yana takowa cikin bacin rai sakina da Hajiya suka kalli juna kafin hajiya tace"Haba Alhaji tanada inda yafi nan ne"Kai tsaye yace"Wannan ya rage nata ammah na rantse bazanyi kaffara ba duk randa sakina ta kaso aurenta bawani dalili bazata zaunamin agida ba"Sakina ta sulale akasa tana Fadin"na shiga uku dady in ka koreni ina zani"Ya juyo ransa abace yace'"inda kika zaba sakina...Duk hakurin yaron nan sai da kika kuresa ko..?"girgiza kai tayi tace"Abbah hajiya da Anty lailane sukaje gidana suka na amshi Adil ahannu Safeena wanda Safwan ya bata shi tana rikonsa"Hajya kari tace"Wata Hajiyar don ubanki"Tafada tana ballamata harara.

Sakina tace"Wlh Daddy susaka sani na aikata abunda har Safwan yasakeni"mirmishin takaichi yayi yana fadin"Very gud naji dadin haka kinga yanzu sai itama tabi ki....Sai ku nemi inda zaku"Hajiya kari tace cikin tashin hankali"In bita ina Alhaji...?Ya fara taka step kan ya waigo yace"Ki bita ku tafi koma ina ne Nima na sakeki Saki daya"Hajiya kari tasa ihu tana fadin"na shiga uku ni karima Alhaji ka sakeni fa kace"Yace idanunsa cike da kwallah"Eh....Haka nace ba abunda zance miki sai Allah ya isa tsakani na dake karima aurena dake babu abunda na karu dashi sai tabarbarewan rayuwa kije duniya takoya miki hankali keda yarki.

Yana gama fadar haka ya haye sama yana share kwallan daya ziraromasa hannu akai Hajiya kari ta dora akai tana kwarma uhu tana fadin"Shikenan Sakina kinzo nima kin kashemin aure"Sakina dake gefe tana kuka tace"ni dakuka kashemin nawa fa hajiya"Hambari ta kai mata tana fadin "Don ubanki waya kashe miki aure kika dai kashema kanki...Ai sai ki tashi mu san nayi"

akwati daya Hajiya kari ta dauka sai Atm dinta suka rankaya suka fice cike da takaichi megadi na musu mgana sukayi banza dashi suna fita kwamishina ya kira Anty salma ya labarta mata komai kuma yace ko sun kira ta zasu zo gidanta tace basunan sunyi tafiya Salma saboda bakinciki saida tayi kwallah ta amsa to ammh aranta tana so tasanya mizanin wata irin uwa Allah ya basu.

Sai da suka fita suka fara tunanin inda zasu yanke hukunci kiran Laila sukayi Sakina ta kirata take fadamata Abunda yafaru cikin razana laila tace"mun shiga uku Daddy yasaki Hajiya"Sakina

tace"eh...Nima fa ai saki na Safwan yayi har Saki biyu"Anty laila tace"garin yaya sakina"Sakina tace cikin fusata"garin bin shawarar dakuka bani....Yanzu Daddy yace bazamu zauna mai agida ba to gamunan zuwa"Zuwa ina......Ta fada cikin firgici cikin mamaki Sakina tace"gidanki mana"Da sauri Laila tace"Kut...Wlh badani ba nima kuzo ku kashemin nawa aure tab...Ku tafi kankia gidansu hajiya zuwa goben ina tafe"daga haka ta kashe wayar sororo Sakina tayi da waya ahannunta tana kallon Hajiya kari dayake wayar a handfree ne taji komai.

laila ta rike baki tace"kutumar uba in barku kuzomin gida yadda mujaheed yake kume dani ai sai yace mu rankaya dukkanmu....Tab....Su karata chan nima ina lallaba rayuwatane

Sakina ta fashe da kuka tace"wlh bazan iya zama a kankia ba hajiya"Cikin bacin rai Hajiya kari tace"to don ubanki sai dai ki nemi gun zuwa domim banda nan bbu inda zamu a amshemu"Sakina batayi mgana ba ta kira Anty salma sai da tabata 2miss cll kana ta dauka cikin kuka take fada mata abunda ke Faruwa mirmishi mai kama da kuka salma tayi kan tace"Ayy bamu kasar mun tafi kasar turkey baban shahid yaje wani aiki ne"daga haka ta yanke wayar.

Basu da zabi illar zuwa tasha suka hau motar kankia sakina kuka taketa yi tana fadi  su suka kashe mata aure...Itakuma hajiya tana fadin ita ta kashe mata aure abu har yazaman musu fada amota sai kallonsu ake ana tirr dasu.

Sai bayan issha"i suka isa kanki koda suka isa gidansu Hajiya kari wanda daman iyayanta sun rasu  yayyintane agidan wanda ta gujesu sai tayi shekara bata leko ba sunyi mamakin ganinta matuka anan take fada musu karya da gaskiya basu yarda ba adaren sukama kwamishina waya yafada musu komai game da hallayar Karima suna ko jin haka suka ce babu ruwansu da ita sai da ta shiga wani yanayi ne zata nemesu to sukan babu ruwansu da ita gidane tazo ta zauna ga dakin mamansu chan data rasu su share kafa su zauna tunda zaman suka zaba.

Haka suka ja jiki asanyaye suka wuce koda suka shiga dakin sai da suka kusa kuka saboda yadda dakin ya lalace ga ruma tako'ina rufin dakin na azarane duk ya kusa ruftowa ga simintin duk ya banbare beraye na Safara ga gefe daya wasu buhuhunan kaikayi ne bbu ko katifa sakina kan akwatin ta ta haye tana kuka ita kuwa hajiya gyalenta ta shimfida ta zauna ga yunwa

na addabansu rabonsu da Abinci tun na safe.

haka suka kwana Sakina kuka ta kwana yi hajiya ko da takaichi ya cika ta dunga durama sakinar zagi tana cewa"ki rufema mutane baki duk wayaja bake ba inda kinyi hakuri agidanki har yaushe za'a sako ki balle har kizo nima kashemin aure"Sakina tace cikin kuka"duk baku kuka kashemin auren ba wlh hajiya keda Anty laila ba abunda zence muku sai Allah ya isa"

Hajiya kari tace"Nima Allah ya isa tsakani da ke inda daya sakeki kin nufi wani wurin har yaushe Alhaji zai sakeni...Duk iya abunda nakemai baitama furta sake agareni sai akanki ni yakamata na miki Allah ya isa sakina"

_Hmmmm haka Rayuwa ta gada daman_

Haka suka kwana wanda Sakina dakyar taga Safe saboda cinnaku da beraye sun hanata sak,ita hajiya haka abun yake agurinta matan gidan kuwa ba wacce ta kallesu saboda daman tuni suka tsaneta domin ko gidanta kaje tadinga kyamatarka kenan.

Sakina gari na waye tafice mota ta hau tatafi banki tayi ciro kudi dubu dari tatafi kasuwa tayo musu siyayyah don tace baza ta iya rayuwa ahaka ba, komai ta siyo su kayan tea indomie macrooni complex kai katifa da fridge saboda bazata iya shan ruwa bbu sanyi ba ta siyo fanka komai da komai mota ta sauketa har kofar gida tasa aka shiga dashi matasan gidan tasa suka kwashe tarkachan daki suka gyara musu kana suka shiga mata da kayan ta biyasu,sai dai Hajiya kari ta ganta da kaya kawai aranta taji dadi domin daman ko ita da'aka haifa anan bazata iya irin rayuwarsu ba.

Commet
And
Share
Vote

*Shakira..*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*33*

"Babu wanda yace musu kala kowa yayi banza dasu to da fari dai sunfara gudanar da rayuwar tasu cikin aminci da jin dadi kadan duk da atakure suke ko wanka sakina zatayi batayi sai dare yayi tayi awaje kan wai bazata iya shiga bayi ba gani take kamar kasa zai rufta da ita hajiya kari kuwa haka dai take lallabawa.

*****

Safeena kuwa sai da ta kwana uku a asibiti kafin a sallamota ta dawo gida wanda momma da Hajiya mama da shikanshi Safwan suka maida hankali gurin bata kulawa Ummi tazo dubata kwananta biyu takoma tareda sha tara na arziki daga sirikinta masha Allah.

Kwamishina da kanshi ya kira Dr yana bashi hakuri inda yake fadamai hukunci daya yanke hakika Dr Safwan ya tsausayama Dady domin shi shekara uku yayi da bakin cikin Sakina shikuwa Daddy shekaru tun ana kurciya bbu jin dadi da kwanciyar hankali hakika shi yafi kamata atsausayamawa.

Koda Safwan ya fadama su momma sun Nuna alhininsu matuka Hajiya mama tayi ajiyar zuciya tace"Hakika kabiru yayi hakuri matuka da karima walh da wanine da bazata kawo warhaka ba....Har ga Allah ba niyyata bakenan karabu da sakina ba A'a kawai so nake tagane kuskurenta to ammh ko yanzu Sakina ta gyara halinta wlh bani da ja zaka dawo da ita"gyada kai momma tayi tace"Tabdijam sakina ce zata iya zaman kauye"Safwan yace"Ai momma awannan lokacin ne zata gane TA TAFKA KUSKURE.

Hajiya kari tace"Kwarai ma kuwa fatan Allah yasa wannan yazama sanadiyar shiryuwansu suka Amsa da Amin.

Allah Sarki Safeena dataji sakin da Safwan yama Sakina sai da tayi kuka taita rokonsa kan yadawo da ita zata bata danta domin tafi ta gaskiya dantane data haifesa da cikinta.Dr yaso ya tsorata ta sai ya sha mur yace"ok kema bazaki rikesa ba kenan gud...Zan kawo wacce zata rikesa aie"To yana fadar haka tayi saurin basa hakura daganan bata karamai mganar ba ammh abun na damunta matuka.

******

KANKIA😂

Tabbas abunda hausawa kan ce komai yayi farko zai yi karshe to hakane tafaru dasu Sakina domin yau da gobe bata bar komai kwanchi tashi sai da suka karar da komai nasu kaf kudaden dake account dinsu suka gama dasu na kokarin su na inganta rayuwarsu shagunan Sakina tuni masu shi suka amshe domin bbu kaya kasuwanci tuni ya rushe,hatta da su Fridge din da suka siya sun saida kayan sawansu da daidai da daidai suke zara wai duk dai karsu bar rayuwar jin dadi.

To daman komai ubangiji yaso ma bawa sai ya amsheshi gashi ayau sun wayi gari basu da komai abincin dazasu ci ma garararsu yakeyi sai da Hajiya kari taita rokon yayyinta kan suma matansu mgana su dinga basu abinci suma din sai da suka ce sai da sudinga fitowa suna

tayasu aiki don wallahi bazasu cida kardawa ba dole tasa suke fitowa domin samun abunda zasusa abakinsu Yau sai gashi Sakina ta rame tayi baki domin bbu mayukan da"aka saba shafawa,kayanta duk sun kode sunyi yage saboda wahala haka zaki ga Sakina ta tike tana buga bowol din ruwa ta cika bokitai takai gida ayi tuwa a yarfa musu akwano wanda ko Sakinar tacinye bazata koshi ba agari ko Ibrinsu ya bazu duk inda suka bi ana tirr dasu Rayuwa tajuya musu baya domin hajiya kari har gidansu Daddy taje tasamu goggonsa taita rokonta kan tasa baki ya maidata ammh sai ta kalleta tace"Ada dai munmai dole ya aureki ya zauna dake ammh yanzu dayasan halayyanki karima bamu da ikon sashi yakara zama da ke sai dai inhar shi yake Ra'ayi"gwiwa a sacce tadawo da tarin nadama duk ta rame tazama tsohuwar karfi da yaji.Har satan hanya tayi taje katsina ammh sai megadi yake fadamata Alhaji yafi wata biyu bai nan yana london yaje hutun karshen shekara tayi tayi yabarta ta shiga ko kaya tadauka ammh yayi kemene yace"yallabai yace kada ya barta ta shiga"To yazatayi bata da ko sisi tana kuka take rokion maigadi yataimaka mata da na mota kallonta yake aransa yana Fadin"Kowa yaki sharan massallachi yayi na kasuwa yau shi Hajiya kema kuka tana rokon shi kudi,dubu daya ya bata ta amsa tana godiya kamar ta tsugunnah mai saida tatafi ya girgiza kai yace"wlh Hajiya kin tafka kuskure dakika bari kika rabu da gwarzo mai hakuri da nagarta irin yallabai....Allah yasa kin tuba harga Allah.

Sai da tadawo take fadama Sakina ga inda taje da abunda yafaru"Sakina dake zaune akasa bbu ko leda riga dabam zani daban tana ta shoshe soshe tace"Hajiya kinga yadda Allah yamaidamu ko kowa ya gujemu saboda hallayanmu hatta da Anty laila yanzu bama asamunta awaya ita kuwa Anty Salma nasani daddy ne yace karta nememu saboda abunda muka aikata akan son zuciyarmu"Takareshe tana fashewa da kuka hajiya kari tatashi ta isa kusa da ita tadafata tace cikin karyayyan murya tace"Hakika Sakina duk abunda ya Sameki nine sila domin amtsayina na mahaifiyarki banta nuna miki abunda kikayi ba daidai bane saima kara miki gwarin gwiwa danikeyi akan abunda kikeyi tabbas Allah ya nuna mana kuskurenmu tun ba aje ko'ina ba"

Sakina takara fashewa da kuka suka rumgume juna Hajiya kari tace cikin kuka"mun Tafka kuskure sakina...Sai dai munada yadda zamuyi mu gyara kuskurenmu kafin lokaci ya kuremana.

sakina tadago idanunta jawur tace"taya Hajiya taya zamu gyara alhalin bamu da wanda ke goyan bayanmu'Hajiya kari tace"Safwan....Kije kibawa Safwan hakuri ya hakura ya maidake Dakinki indai kika koma dakinki ni ko ban komaba nasan  Allah zai dubeni ya yafemin abunda na aikata in cigaba da zaman anan harta Allah ta kasance"rumgumeta Sakina tayi cikin kuka tace"A'a Hajiya wlh bazan iya kallon Safwan da ahalinsa ince su yafemin ba saboda ban kyauta musu wlh bantaba kyautata musu ba koda na rana daya ne.."Hajiya ta runtse ido hawaye na kwaranyomata ranta namata daci Nadama mai tsanani ya baibayeta.

_Allah Sarki ita daman Duniya haka ta gada inkaine yau bakai bakai bane gobe_

*After Three month*

Wata mata nagani chaculate colour Ce sanye cikin wata doguwar rigar abaya tayi rolling din bakin veil din akanta har zuwa wuyanta kafanta sanye da cover baki hannunta rike da jakar gucci baka sannan dayan hannunta rike da wasu littafai kallo daya zakamata kazata yar kasar maroco ne saboda yanayinta.

Tsaye take abakin get din KADUNA STATE UNIVERSITY Wato KASU sai gawata rantsantsiyar range cover baka tazo tafaka a gabanta aka bude motar akafito wow....Abunda na furta masu karatu kunsan wa Nagani DR SAFWAN ne cikin wata rantsatsiyar farar shadda wacce tafito da zatinsa da kyawunsa lokaci guda tareda murjewa irinta hutu yarinyar naga ya Nufa yana cewa"Am srry yanmatan..Nayi latti ko..?"ai sake baki nayi kardai ace min wannan matar Dana Gani tun dazu SaFeena ce ai bangama mamaki ba naji muryanta cikin wayewa tace"bbu komai..Unku ina yarona"Yace"yanzu zamu biya mudaukosa daga islamiya"mirmishi tamai yana budemata motar tashiga sai alokacin naga dan cikinta dayafara tasawa Araina na Furta masha Allah.

Mkrantansu Adil suka biya suka daukosa wanda yadan kara girma da wayo kana suka nufi gida.

Bayan dawowar Safeena daga Asibiti bata sani ba ashe Safwan ya nemata gurbi karatu ajamiar kadunar sai da ya kammallah komai kawaai yakawomata addimmision letter dinta da time table dinsu na karatu taga zata karanci Nursing wayyo dadi Safeena sai da tayi kukan Farinciki taje shashen su momma ta nuna musu tana murna haka takira su Ummi tana fadamusu suma sun yi murna kwarai.

To daman lokaci yasanya adil wata mkaranta mai Suna command sch dake kaduna yakuma sanyasa a islamiya shiyasa gari na wayewa dasungama abunda zasuyi sai su shirya yadaukesu yafara kai Adil mkrnta kana ya biya ya kai Safeena mkranta  ranar kuwa da bayanan  direba ya

kaisu.

hakika Safeena na jin dadin karatunta sosai shiganta mkranta takara wayewa tasan me yadda ake taraiyaran mji da kwalliya mai tsari da yabawa hakika Saferna tasamu chanji rayuwa mai inganci ga dan cikanta wanda ke cikin wata hudu kenan yanzu.

Commet
and
Share
Vote

*Janafty*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO *My Momma Hajja Hadiza muhammed Ba'are*

*34*

"Kunya tareda Nauyi sun hana Sakeena zuwa tabawa Safwan hakuri duk da Hajiya kari ta Matsamata taje tagwada sa'arta azahirin gaskiya dukkansu sunyi nadama kuma suna ta tuba ga Allah hajiya karima tanemi gafaran yan"uwanta kuma sun yafemata ammh sunce basu da hurumin dazasu roki Kwamishina yamaidata dakinta sai dai ta cigaba da addu'a Allah yasa tsakaninsu akwai Sauran Zama

wuni yana shudewa kwana yana shudewa ahaka har watanni suka shude awannan lokaci Safeena cikinta nada wata takwas aduniya tayi kiba cikin kuma yayi girma sosai kamar dan wata tara gashi tana karatunta cikin nasara da jin dadi tareda taimakon mijinta kuma gwarzonta Dr Safwan Sale Safana wanda duk abunda bata gane ba inta koma gida yana kara koyamata,Shi da kantshi yakemata awo ammh shikanshi girman cikinta na bashi tsoro duk da yamata scan kuma yaga komai lpy.

Su hajiya mama da momma kuwa rayuwa sabuwa domin yanzu basu dawani mtsala sukam damar Sakinace damuwarsu kuma yanzu batanan shiyasa yanzu bakajin Hajiya mama na kwakwazonta na fama sai dai in yan abun sun motsa kunsan mai hali bayasa Halinsa.

KANKIA

awannan watannin in ku ka ga yadda su Sakina suka koma sai kun zubar musu da kwallah saboda yadda suka rame suka kammajame sakina fuska tayi baki ta kuma cika da kuraje ga kan nan yayi duku duku kamar na mahaukaciya kumbuna sun yi baki sunyi datti hajiya kari kuwa kamar tsohuwa takoma saboda wahala.

Yau tunsafe Sakina taje layin bowol ammh sai wurin takwas tasamu zuba ruwanta tadauko daya akanta daya yana hannunta tana tafiya zata gida taji ana mata hon abaya kaucewa tayi domim bata zata da ita ake ba sai da motar tazo daf da ita kana ta tsaya cikin mamaki take bin jeep din da kallo kafin taga anbude murfin mota anfito wazata gani...Daddy ta furta cikin mamaki ya amsa da "Na'am sakina kece kika koma haka "yafada idaninsa sunkawo ruwa zatayi mgana kenan wata farar mata ta bude mota ta fito sanye cikin leshi da mayafinta bawata babba bace bata wuce sa'ar Anty salma ba.

Ta nufe sakina cikin tsausayawa tana fadin"Innalillahi...Sweety badai dota Sakina bace wannan..?"Kwamishina yagyda mata ta yi saurin saukemata ruwan ta rumgumeta tana fadin"Baka kyauta ba Sweet hrt kowa yana kuskure ko Allah muna masa laifi yayafemana ko"baicemata komai ba sai ma cema direba yayi su karisa.

Sakina sai kallan matan take datake rike da hannunta har cikin gida ai sakina sai ta shiga kwalama Hajiya kari kira tana fitowa Daidai kwamishina yana shigowa ai sai tayi cak tana kallonsa shima ita yake kallo yana nuna ta da mamaki hawaye ya zuraroma Hajiya kari sai ta koma daki da gudu tana kuka...dakin matan tabita tana rike da sakina.

Hajiya kari dake durkushe tana kuka tadafa tadago tana kallonta murmishi ta sakarmata kafin tace"Don Allah kibar kukan nan hakanan ko Allah muna masa laifi yayafema na balle mu mutane"Hajiya kari tace cikin kuka wacece ke!...MATATA CE....dana aura bayan Rabuwarmu...atare sakina da hajiya kari suka kara kallonta itakuma tana musu mirmishi.Dady Yafadi haka bayan ya sawo kanshi dakin yakarasa shigowa yana fadin"Bayan na koreku kwana biyu kawai na kara nabar kasar sai da nayi wata uku baninan karkuyi mamaki duk halin dakuke ciki inada Ibr...Dagacham saudayi na wuce achan na hadu da Mariyatul kibdiyya wacce asalinta yar gombe ce tayi aure mijinta ya rasu ammh bata taba haihuwa ba mahaifinta shine wazirin masarautar gombe munyi aure wata hudu da suka wuce daman nafadamata yayana hudu shine da bata ganki ba ta tambayeni nikuma na fadamata komai wlh tallahi tunda na fadamata ta kasa sukuni akan lalle Saina yafemuku kuma saina zo mun dauko ku.....mu koma gida.

Sakina tafada cikin rawan murya"mu Dady...Kayafemana mu koma gida harda Hajiya"Dady yace"kwarai ma Sakina tare zamu koma domin tun jiya da asuba na sanya aka maida aurenmu....Da mahaifiyarku nasan ko ahaka na barku kun fahimci rayuwar danike gayamuku"Sakina ta guce da kuka kan zube gaban daddy tana kara basa hakuri dagota yayi ya sharemata hawaye yace"ba'a san raina na muku haka ba wlh sai dan ku gyaru kuma ku gane yadda Rayuwa tasa gaba,sakina tace"Ba komai daddy hakika kaci ka uba nagari...Wlh ko ahaka nagane daddy nagane mutum ba komai bane.

gurin Mariya taje ta durkusa tana fadin"mungode Anty hakika bamu da bakin gode miki Allah ya saka miki Aljannah"kamota tayi ta rumgumeta tana fadin",babu komai yata...Karki damu inaji kamar nina haifeki Sakina.Mirmishi sukama juna lokaci daya kan taja hannunta suka fice.

Hajiya kari takasa dagowa ta kalli kwamishina saboda kunya shine yayi gyaran murya yace"Basai kin ce komai ba karima Allah yayafemana gabadaya.."Tadago idanunta jawur tace"Ban chanchanci yafiyarka ba kabiru wlh ban chanchanci yafiyarka ba sam"takareshe fada da kuka takawa yayi ya isa gareta yadagota yana sharemata hawaye yace"ko alama karima duk nasan kin min abubuwa masu yawa ammh tunda kingane kuranki wlh har ga raina na yafemiki kuma nasa anmaida auranmu..da zuciya daya sai dai bansani ba ko zaki iya zama da kishiya"da sauri Hajiya kari tace"wane ni daja da abunda Allah ya halarta...Ai samun abokiyar zama irin mariya sai an tona...Ngd sosai Allah yakara girma.Mirmishi ya sakarmata yana kara gogemata hawaye.

nan suka wuni har su yayyen hajiyan suka dawo sukayi mgana da kwamishina yasaukemusu kayan abincin dayazo dashi sukuwa su sakina yace kada su dau komai aikuwa murna gurinsu ba'a mgana dazasu tafi suka roki gafarar kowa suma mutan gidan suna neman tasu ankara musu fada kan sundai ga rayuwa inzasu natsu yarage nasu,gidansu kwamishina suka biya suma chan din albarka sukaita sanyawa musu har suka tafi.

Amota mariya babu ruwanta sai jan Hajiya take da hira ita da Sakina su kuwa sunkasa sakin jikinsu da ita itakuwa ko ajinkinta sai jansu take ajiki.

Suna komawa takai Sakina har daki ta hadamata ruwan wanka tadauko mata wata doguwar riga ta ijiyemata hakama tama Hajiya kari wacce kunya ya hanata mgana bayan shiganta wankane hawaye ya zuraromata wai yau itada take iko da gidanta sai gashi yau watace ke iko dashi...Ba shakkah duk wanda bai godema Allah da Ni'imar sa ba zai godema wuyarsa.

Ita tai ta dawainiya dasu suna godemata kayanta ta daukoma hajiya kari kafin gobe aje asiyama su nasu kayan.

Allahu akbar Sakina da Hajiya dasuka sa hakarkarunsiu akan katifa suka furta domin ko amafarki basu taba tsammanin zasu dawo rayuwarsu ta baya ba..Koda gari ya waye hakanne yafaru a dining suka ci abinci tun basu sakin jikinsu har dai suka fara sakewa da ita.

Kwanan su biyu dawowa komai yafara zama normal tuni an musi sabbi dinkuna abunsu hajiya kari tazama wata so cool da ita kamar ba itaba itakuwa Sakina Anty na iya bakin kokarinta na ganin ta saki jinkinta,washegari sai ga Laila tazo gidan tana ba su Sakina hakuri na rashin

zuwanta kankia Sakina ta mata dariya kawai tace"Anty laila kenam bbu komai Rayuwar kenan...Sai kuma naji ance ya mujaheed yayi aure"tace"eh...Wlh wata biyu dasuka wuce"Sakina tace"to meyasa kika yarda"tazaro ido tace"so kike in tada hankali nima ya sake ni ko"Sakina ta kalleta hawaye ya ciko idanunta tace"oh..Ammh ni kikace in tada hankalina ashe kinsan Safwan zai iya sakina in namai abunda kikace kenan ko"Shuru Laila ta mata mikewa Sakina tayi tace"basai kinyi mgana ba nagane komai domin ni yanzu ashafin rayuwa ba abunda bangani ba"da sauri Laila tasha gabanta tana fadin"kiyi hakuri yar'uwata nima nasan sam ban kyautaba amtsayina na yayarki....Ki yafemin don Allah"Kallonta sakina tayi kan tace'shikenan bbu komai...Harda haihuwar dakikasa na dakatar duk na yafemiki duk da ke kinata haihuwa kamar naga ga wani karuwar  nan mun samu"tana gama fadar haka ta fice tana sharan kwallah,hajiya kari dake gefe tace'Mumaka sa sakina ta tafka kuskure mune sila wlh"Anty laila tace"Allah ya yafemana....Ammh tadade tana saka mganar sakina tasan mgana ta saka mata.

Asatin Anty salma tazo ita da Ummi daman tana hannunta tuni tayi murna matuka kuma ta kara musu fada sosai lalle ta yarda duniya tahora hajiya koda yarda tayi sanyi Anty mariya tana ta fadin"Yaya kaza,yaya kaza...Hajiya na amsawa da kulawa...Zamansu gwanin sha'awa kamar ba kishiyoyi ba,Anty kwananta biyu takoma ammh kafin takoma sai da tace ta shirya taje har gida ta ba Dr hakuri ko ya maidata dakinta tabbas tayi na'am da shawararta shiyasa washegari nayi ta shirya cikin dogon hijabinta har kasa Anty mariya ta aramata motarta tamusu sallama ta fice suna mata fatan sa'a.

Cikin sanyi jiki ta dumfari gidansu Safwan lokacin da Habu mai gadi ya budemata get bai ganeta ba sai da ta paka motar ta fito tana gaisheshi take tambayansa ko Safwan yana gida,ya amsa mata da "eh...Yana nan hajiya mirmishi ta mai kawai tace"Sakina sunana ba hajiya ba"Ai sake baki yayi yana kallonta kan yace"Au...Sak...Oh hajiya barka da zuwa"wucewa kawai tayi ta barsa sake da baki har yana kara lekata.

Shashen su momma ta nufa ta shiga da sallamarta wanda Hajiya mama ke zaune afalon ta amsa tana fadin"Maraba shigo......

Commet
And
Share.
Vote

*Shakira..*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE...!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*Dedicated to my momma Hajja khadija muhammd Ba'are*

*35*

"Karisawa tayi cikin falo tasamu gefen hajiya ta zauna kallonta hajiya mama keyi ranta na bata kamar sakina ammh kuma tana karyatawa Sakina tadago ta kalli hajiya kan tace"Hajiya baki ganeni bako..?

.Hajiya mama tace"eh...Kiyi hakuri ban sheda ki ba yan"nan"Mirmishin takaichi Sakina tayi kan tace idanunta na tara kwallah"Sakina ce fa Hajiya"Ai da Hanzari tamike tana salati da karfi ta furta"Sakina...Nashiga uku ni Maryamu Sakina ciwo kikayi naga kin lalace haka"Fashewa da kuka tayi tana Fadin"wlh hajiya nagani kuma nagane koda kika samin tsama sona kike...Don girman Allah Hajiya ki yafemin'Hajiya ta karisa kusa da sakina tadagota tana fadin"Mekika min Sakina wlh bakimin komai ba duk abunda kikaga ina miki don ki gyaru ne...Allah yayafemana gabadaya"Rumgumeta Sakina tayi tana godiya cikin kuka momma dake tsaye tundazu ta kariso

tana cewa"Tabbas baki mana komai Sakina har yanzu kallon ya'muke miki"Sakin Hajiya tayi kan ta isa gaban momma ta durkusa tana fadin"Momma...Ban chanchanta kiyi afuwa agareni ba ammh gani durkushe agabanki kiyi duba ga Allah ki gafartamin wlh na tuba nabi Allah baran kara ba nagane kune masoyana na gaskiya"Momma tadagota tana sharemata hawaye tace"Har Abada ban chanzaki ba sakina ki na nan amatsayin yata ta har abada...Karki damu daman baki man komai Allah yayafemana gabadayanmu"Rumgume momma tayi tana Fadin"Nagode momma Allah yakara girma.

Kan kujera suka karisa nan Sakina tabasu Ibrinta tun bayan sakin da Safwan ya mata Hajiya mama tace"Allah sarki kabiru hakika ya jarabtu sai dai mu fatan Allah ya kara shiryar damu"Suka amsa Da Amin.

Adil ne ya shigo da gudu yadane cinyar hajiya mama yana Fadin"Hajiyata...Turesa tayi tana fadin"A'a Alhajine...Kai wai bana ce ka kiyayeni ba"Tura baki yayi yatashi ya isa ga momma ya haye cinyarta yace"Bani chonki...Momma nake cho"Yafada yana rumgumeta Hajiya mama tace"To sai me...Aikin banza chan da tsiyarka ni nan har akwai soyayyar data kai na marigayi Habule na nane wallahi bata"Tafada harda jaddadawa.

Sakina dake gefe tana kallonsu ta share hawaye tana kallon Adil dayakara girma da wayo ga yayi kiba abunshi alamun yana Samun kwanciyar Hankali abun takaichi wao ace danta na cikinta ma baisanta saboda wani sakarci nata...Hannu tasa ta share hawayen daya zubomata kada su hajiya su gani ammh ina sun riga sun ganta.

Sallamar Safwan shi ya dakatar da dramar dake tsakanin Hajiya da Adil Tafe yake shida Safeena dake sanye da doguwar riga baka ta sanya mayafi ya rufema cikin jikinta wanda yakusa rinjayarta saboda girmasa kanta na gefen kafadarshi shima ya zagayo hannnsa ta kugunta yana Sanye cikin bakar jallabiya tunda suka shigo Sakina tayi galala tana binsu da kallo ganin yadda suka chanza cikin lokaci kankani Dr Safwan yayi kiba ya murje yakara haske itama Safeenar,tunda suka shigo momma da Hajiya suka mike suna ma Safeena Sannu shiya taimaka mata ta zauna akasa yana mata Sannu Safwan yace"Momma...Wlh zan dawo muku da Adil damun yanmatana yake d kiriniya wai harda goyasa yakecewa ayi fa"Hajiya mama ta dunguremasa kai tace"kaga min mugu...Don ubanka da uban cikin da ubanka yamata zataji kokuwa da goyaka"😂kunya takama Safeena da momma shiko Safwan ko ajikinsa Tabe baki yayi zai fashe dakuka tace"Kaji gidanku wlh kanamin kuka zaneka zanyi ja'iri kawai"Kuka yasa yatafi da gudu gun momma yarumgumeta Safeena tace'Amana hakuri Hajiya kin manta yace zai Siya miki jirgi"Hajiya tace"Bani so Raggo kawai'dagowa yayi hawaye shabe shabe yace"Ba chan chiyanmiki jigi ba Daddy da mami na jan chiyama wa...Kuma baja ki hau ba"Yafada harda murguda mata baki dariya sukasa mishi gabadaya.

Safwan yadago yana dariya kawai caraf idanunsa suka sauka kan Sakina dake zaune gefe tana ZUBAR KWALLAH...Aziza idiris gombe...Bana gajiya da Novel dinnan walle....Kuramata ido yayi cikin mamaki da firgici kamar fa Sakina yake gani ganin inda yake kallo yasa suka bi gun da kallo Safeena takurama Sakina ido tana kallonta Aranta tana so tace Anty ammh wata zuciyar tana cewa ba ita bace"Sakina tayi saurin mikewa tana fadin"Momma..Zan tafi dama nazo gaishekune"Tafada tanayi hanyar waje...SAKINA..Dr Safwan ya furta da mamaki cak ta tsaya ranta na mata kuna Hajiya mama tace"kwarai...Tun dazu tazo neman gafararmu"Kai tsaye yace"kuma kuka yafemata"Juyowa tayi cikin kuka tace"Daman nasan ban chanchanci yafiyarku ba...Safwan"Tafada kuka yaci karfinta baya ya juyamata kawai ransa namasa kuna rarrafawa tayi ta isa zuwa gabansa tana fadin'Na san ban chanchanta ka kalleni ba Safwan ammh kadubi darajar Allah kadubeni da idon Rahama kayafemi ko naga daidai Rayuwata"shuru yamata Safeena ta mike dakyar ta isa kusa da Sakina ta durkusa tarike hannunta dagowa tayi tana kallonta ita kuma ta mata mirmishi kallonsa tayi tace"UNcle....Saurin jiyowa yayi yana kallonta kan yayi saurin cewa"Ke kina da hankali kuwa bakiga halin dakike ciki ba...Tashi tashi.."Kin tashi tayi saima cewa datayi'Kazama mai yafiya unku...Kaima sai Allah yadubeka da idon Rahama...Anty tayi kuskure kuma tagane kuskurenta Don Allah kabata dama baxata sake ba"Shuru yayi kan yace"ki tashi nace itama kallon idanunsa tayi tace"Bazan tashiba sai ka furta ka yafemata"kallonta shima yakeyi kan yayi ajiyar zuciya yace'Taji albarkacinki....na yafemata Allah ya yafemana gabadaya"Alhamdulillah...Haka cikakken musulmi yake"Hajiya mama ta furta.

Sakina tasa hannu tadago Safeena ta rike hannunta tana fadin"Bansan mezan cemiki ba Safeena...Ban sani ba'Tafada idanunta na kawo ruwa"Safeena ta damke hannunta tace"Basai kin ce komai ba Antyna wlh kin wuce haka agurina ammh alfarma nake nema agunki"Sakina tace"Ki fadi komiye safeena indai baifi karfina ba zan miki shi Safeena"kai tsaye Tafada tana kallon Dr Safwan"Ki dawo kizo mu zauna mu reni ya'yanmu tare kuma mu rumgumi mijinmu...Mu zauna har Abada"Kallon kallon aka hau tsakanin Dr Safwan da Sakina saurin sadda kai yayi yace"A'a.....Safeena tayi gaskiya ka maidata dakinta ku taru ku rufama juna asiri...Ku zauna lafiya da juna"Hajiya mama tace"shikenan kuwa...Allah yayi miki albarka Safeena Allah ya rabaki da cikin jikin ki lpy"gabadayansu suka amsa Da Amin.

Rumgumeta Sakina tayi tana kuka tana mata godiya safeena tadagota tana sharemata hawaye tace"Kidaina godemin Anty kin wuce komai agurina"Itama sai hawaye sharr Adil ne yaga suna hawaye duka biyun zuwa yayi ya rike ma Safeena hannu yana Fadin"Mami...wacece wannan.."yafada yana Nuna Sakina shafa kansa tayi kan tace"UMMINKANE...Itace mahaifiyarka"Kallonta yayi yace yana kallon Sakina"UMMI.....Yafada still yana kallonta sakina ta rumgumesa tana hawaye tace"Ni Umminkane ta haihu Ammh Mami mahaifiyarkace ta har abada"Tafada tana shafa kansa abun mamaki shima rumgumeta yayi yana sharemata hawaye.

_Allah sarki Uwa Uwa ce komai lalacewarta_

Komai ya daidaita cikin lokaci kankani Sakina nan ta wuni tana dawainiya da Safeena da Adil ita tataya momma Aikin girkin dare sai da suka kammallah kunsan Raba dare sukai suna hira kafin safeena ta barota cikin dakinta takoma gun Dr Sakina tayi kuka awannan daren na ganinta kwance kan gadon tabata tsinana komai ba sai lalacewa...Raba dare tayi da ibada da asuban fari tatashi kokan Su Safena su fito Sakina ta tsaftace gida ta hada musu break kwai ta soya musiu da ruwan tea suna karyawa DR yayi harama  abun mamaki har Adil na zarin shi zai bita lallabasa sukai suka shiga mota suka kaisa mkranta kana suka biya suka ijiye Safeena asch tana da test tai musu fatan dawowa lpy,suka kama hanya shida Sakina direba yana binsu abaya da motar data zo dashi,Shizai kaita saboda mganar Maida aurensu.

Hakika kwamishina  yayi murnan dawowar Safwan amtsayin sirikinsa a kashi na biyu...Hajiya kari saboda godiya harda kuka tarokesa gafara kuma tace ya rokan mata su Momma kan tazo...Anta dawainiya dashi an fahimci juna sosai cikin mutumci da girmama juna sai la'asar yayi shirin tafiya rako sa tayi gun motarsa kallonta yakeyi bako kiftawa Kauda ido tayi kan tace"Wannan...Kallon fa"mirmishi yayi yana Shiga mota yace"Mamaki nake wai Ke Sakina kabir kankia ce kika zama ustaziya"Dariya tace"Ka adana mamakinka sai Auren ya maidu tukunnah..."Tafada tana rufemasa murfin mota kallonta yayi yace"Sure....Gyada kanta tayi kawai dagamasa hannu tayi har yafice daga gidan.

commet
And
Share
Vote.

*Anitha...*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE...!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*36*

Shirye shirye takowani bangare ya kamkama Tahir dayaci Ibrin komai shima kansa yayi mamaki ammh kuma mamakinsa ya gushe domin tare suka koma kt shida Safwan jin shirye shiryen da take gudanarwa abun mamaki Sakina tace bata dawani shiri itakanta walima ce kuma sunyi mgana da Safeena ranar asabar za"a shirya ma'ana bayan ta taren.

Ranar jumma"a Daddy shi yazo kaduna bayan sallar jumma'a amasallachin sultan bello aka maida aurensu akan sadaki dubu talati,kuma ana gama daura auran Tahir ya wuce yaje ya taho da',ita domin daddy yace kada wacce taje Anty salma dama bata samu zuwa ba Anty lailace tazo itama kuma Daddy yace gobe takoma gidanta,Anty mariyace kadai tarakata bayan tarin masihohin data sha gakuma gyaran da Antyn nata ta zage ta Mata.

itakanta Anty mariyan bata jima ba ta musu sallama Daddy ya zo suka wuce...Suka barta nan shashen momma ita dasu Safeena da Adil wanda ke yaketa tsalle Sakina tadawo gidansu bbu wani gyaran da Safwan yayi ma gidan  sakamakon yana chan yana kera musu wani gidan a Malali Gra katon gidane sama da kasa shima din bangare biyu yayi musu ammh shi wannan din wlh duniyace ko su hajiya basusan da gidan ba Shida Tahir ne kadai suka Sani.

Sakina Da Safeena sai da Dr Safwan yadawo su hajiya suka tarasu suka musu Nasiha kan su hada kansu su zauna lpy,sai wajen 9 na dare suka Nufi shashensu achan din ma dumguma sukayi dakin Sakina suna hira Safwan duk sanda ya kalli Safeena ransa kara fari yake domin komai yake faruwa ayu wlh itace sillar daidaituwan komai...sai da taga Dare yayi kana ta musu sallama Safwan yadaukan mata Adil dayayi barci yarakata daki wanda Sakina tace ta yafe yaje gun Safeena ya kwana tunda ita tana da lalura...Kin yarda Safeena tayi shiyasa yana kwantar da Adil  tashige bayi tana fadin"Unku mu kwana lpy...girgiza kai kawai yayi yawuce saboda yasan da gangan tashige bayin don karya mata wani mgana ne.

dakinsa ya koma yayi wanka ya sanya jallabiya yafeshe jikinsa da body spry masu kamshi kan ya nufi dakin Sakina da Sallama ya shiga ta amsa tana ninke darduma kallonta yayi kan yace"Me kikayi...?Tace"sallar issha'i...Yace'ok...Koma muyi sallah don yau ta dabam ce you know...Mirmishi tamai kawai yajagorancesu sukayi Ra'ka"a hudu yadade yana musu addu'a kafin su kammallah yasan Sakina nada rauni a addini dat why yai mata alkwarin koyar da ita Insha Allahu.

Tabbas Daren na Alkhairi ne domin Safwan da Sakina sun darji juna iya son ransu an famshe watannin da'aka diba ba'a tare...Tun asuba sakina bata koma ba tahau gyaran gida tana kammallawa takoma kichen doya ta soya musu da kwai sai ruwan tea domin dai girkin ba wani iyawa tayi ba wannan ba don komawarta ne take gani gun Anty mariya yasa ma ta iya wasu Abun.

Hakika zamansu yana gudana cikin kwanciyar hankali da zaman lpy duk da Sakina na iya bakin kokarinta yanzu ammh duk da hakan tasani kuma tana gani safeena tanada wani mtsayi agidan wanda daga Safwan har su momma girmamata sukeyi...Tasani ita tabar damanta har wata ta kwace sai dai kawai tayi yar hawayenta ta share,kwana uku yabar dakinta bisa na al'ada yakoma suna kwana daya akowani daki.

Bai bafada musu mganar sabon gida ba saida ya bari weekend kana yace kowa ya shirya za'a fita hardasu momma mota biyu sukayi safwan na tuka su momma da hajiya sai Tahir ya tukasu Safeena basu gama mamaki ba sai da suka gansu a wani makeken gida upstair kamar kasar turai ba kai tsayawa bada Ibrin wannan gidama kauyancine sai dayagama zagayawa dasu ko'ina na gidan yaji alatun kayan more rayuwa gida dai wallahi ko akasar turai.

Sai da suka koma gida ya tarasu yafada musu cewa achan zasu koma dukkansu bayan haihuwar Safeena kwarai da gaske sunyi murna ammh sai Hajiya mama tace"Hakika naji dadi safiyanu kuma muna maka murna ammh zahirin gaskiya nida Hadiza bazamu biku ba domin me muke nema arayuwa komai kagama yimashi sai muyi ta maka addu"a da fatan dacewa muna nan gidan ya ishemu jin dadin rayuwa ko yi komawarku chan kai da matanka Allah in kunsamu lokaci kwa leko agaisa"Babu yadda sukayi iya domin Hajiya mama da ce wlh baza koma chan ba dole aka barshi ahakan.

yau Sakina keda sati uku da tarewa misalin karfe goma da wani abu na dare barowansu kenan itada Safwan daga dakin Safeena safwan yana bayi itakuma tafito falo daukan wayanta sai kawai taji nishi kuma daga dakin Safeena abun ke fitowa ai da gudu ta shiga dakin ta isketa durkushe tana nishi gashi wani ruwa na biyota ai A sitti takoma daki tana kwalama Safwan kira fitowarsa kenan daga wanka da sauri yazira jallabiya suka rankaya Suna zuwa kofar dakin sukaji kukan jariri ai da gudu suna bugan kafadar juna suka antaya dakin shigansu yayi dai dai da sawo kan dawani jinjirin yayi da sauri Safwan yasa hannu ya jawoshi Safeena takoma ta kwanta tana maida Numfashi cikin farin ciki Sakina tadauki dayan tana fadin"Alhamdulillah Ala kulli Halin Safwan yan biyu ne Safeena ta haifa shima bakinshi yaki rufuwa Safeena kawai yake jerawa sannu harda hawaye da jinin da komai yahada da yayan ya rumgume yana zubamata godiya sakina sai da tayi kwallah tana tuna da itama yamzu Safwan zai ma wannan rawan jikin.

cikin lokaci kankani suka gyara komai Safwan ya yankema yara cibi itakuma Sakina tagyara wurin safwan dakanshi yadauki Safeena sai toilet yahadamata ruwan wanka yahau gasata yabarta ciki saboda taji dadin jikinta,komawa yayi shida Sakina suka zage suka wanke yaran tas suka sanya musu kaya suka jerasu kan gado suna kallo,safeena na fitowa suna rigen rigen mata Sannu sakina tahadomata shayi mai kwauri tasha ...Kai in takaice muku nan suka kwana

suna dawainiya da Safeena sai da Safe da Safwan yadawo sallar asuba yashiga yake fadama su momma safeena ta haihu cikin farinciki suka dumguma kan kace kwabo haihuwar Safeena tazagaya dangi shida kanshi suka tafi asibiti yaduba da ita da yaran ya tabbatar da komai normal kana suka dawo,mutane sai zuwa barka suke da ganin yara masu kama da ubansu akuma haihuwarne hajiya kari da Anty mariya suka zo harda kwamishina da kayan arziki iri Sunkoma washegari sai ga Anty laila itama harda amaryan da'a mata sunzo barka suna da abun arzikinsu hakika safwan da su hajiya sunji dadi sunkuma yarda yanzu za'ayi zumunchi mai tsafta sakina kuwa Allah kadai zai biyata domin tadaukema su momma hidima ita ke komai na gidan ga dawainiyar mai jagejage Safeena tayi alkwari yadda Sakina take kokarin farantamata ita sai ta faranta mata shikanshi Safwan tun bai sakin jiki da ita har yafara domin alkhairan Sakina yadakushe sharrinta na baya,shikuwa Adil kuka yake dayaga Safeena da dauki yaran sai yahau kuka wai a ijiyesu adaukesa sai Safeena ta mika sakina su tajawoshi ta rumgume tace ya'yanta gaka ma nabata abunta akai kadaine dana ko"sai yahau murna yace"Mami ai ya'yan Ummi ne ko ta gyadamai kai shikuma yana dariya.

Sai ana gobe suna suka samu damar komawa sabon gidansu tareda rakiyar yan"uwa da abokan arziki ciki harda Aisha kawar Safeena da inna husai harda maman Aisha da matan kawu isuhu momma da hajiya sun rakasu suma komai yaji baanda tsiya kowa yaga gidan sai dai kaji ya furta masha Allahu dare nayi su momma suka koma gida su koma akabarsu nan da masu shagalin suna.

Su suka zauna akasa mai dauke da falo guda biyu da manyan dakuna guda hudu kowanne yana dauke da falo da toilet sakina ta dau daya safeena ta dau dayan sauran biyun kuma daya aka barma baki dayan kuma ba'a budesu ba

Commet
Share
Vote

*Shakira...*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Mommah Hajja Hadiza muhammed Ba"are*

*37*

"Hakika taro yayi taro domin yan'uwa da abokan arzuka sun hallata bbu laifi Safwan yabaza bajintarsa awannan haihuwar domin sa guda yagada bayan ragunan da'aikata yankawa abun sai wanda yagani.Safeena shiga kawai take tana cirewa domin akwatu guda Safwan yayimata na fitan suna ita da babies sakina ma kala biyar yamata itama na fitar Sunan,baki sunzo tako ina har hajiya kari sai tazo itada Anty mariya wanda suka zo da abun arzikinsu niki niki kafin su wuce gidansu momma don suma achan suke nasu taron.

odar abinci kuwa Restaurant uku suka zo domin bawa jama"a abincin da sukeso,aikuwa anci ansha harda masu guziri baki tako'ina sunzo ciki harda Yan Janaf fans,Hibbatullah fans,yarima suhail fans1&2 da Na tafka kuskure fans,da yan kungiyata Interlligent writers suma sunzo wannan wurin my Anty sis Naja'atu anci harda guziri ajaka my leema ma har ariga su Sahiba kuwa anci kamar za"ayi amai bai isheta ba leda guda tasamu tana guziri,Anty sainah,Anty hafsat,mummy zil,maman kausar,kuwa bayan angama nadan na gidan Dr ai suna ganin mota zata koma gidan Hajiya mama suka shige suna Fadin bari suje suga kuma wata wainar ake soyawa achan kuma....Oh ni jami,Yan sch dinsu wato yan faculty su sunmata kara domin kwansu da karkwatansu su hallarta.

Anrarraba abubuwa irinsu Robobi botikai dinnerset kofuna da jakukkuna masu dauke da hotunan yaran wa"inda sukaci Sunan Hajiya mama da mijinta wato MARYAM SAFWAN SALE DA ABUBAKAR SAFWAN SALE...Hakika Safwan ya farantama Hajiyamama rai wanda farincikinta yaki boyuwa kwatakwata harda kwallanta saboda murna.

Sakina itace kan komai domin tazage ana hidima da ita Anty laila tazo suna ita da amaryanta itama suna zaman lpy abunsu basu kwana ba suka koma Sakina tasani cewa ta tafka kuskure tun abaya domin fadar data ke dashi ada ayanzu banata bane domin safina tarigaya data kamkame ko"ina Dr baya ganin kowa agabansa sai Safeena itadai kawai yana rakatane...Wani lokacin in abun yadameta sai dai tashige daki taita kuka ita kadai gashi kwanakin nan tana ta zubar jini tun abun nazuwa kadan har yafara yawa ada tazata period ne ammh daga baya tasan

abun ya wuce haka.

Anyi suna Ipy an tashi Ipy bakin Safana da na zurmi hardama na zamfara sunkoma gidajensu Aisha ce kadai bata wuce ba wai Saita kara kwana biyu...dariya kawai Safeena ta mata kan ta ce"munafuka wlh nasan meya tsaidake"Sakina ce tace"Ai Tahir wlh sai ya gundireki ne"Aisha tace"Daman masoyi na gudinran masoyinshi ne"Dariya suka mata gabadaya.Tabbas soyayyah mai zafi ta kulli tsakanin Dr Tahir da Aisha wanda suka sha tsiya gun Safeena da Sakina yan tagwayen Dr.

Inna zulai kanwatake ga Mallam Aliyu ita akabarma Safeena tana kula da ita Sakina ma ba'a barta abaya ba tana iya bakin kokarinta wurin taimakawa domin in Safeena tatafi mkranta ita da inna zulai suke wahala da yaran....Su momma kuwa kullum kwanan duniya in Safwan zai fita aiki sai ya biya haka kuma inyadawo su Safeena kuwa indai basu dawani abu da zasuyi to haka zasu saka yayan amota su kaima su momma wanda Hajiya mama tahana achanza musu suna ana kiransu da Hajiya da Justice.

Babu wanda yataba lura da halin Da Sakina ke ciki sai Ranar da Safe weekend ne Safwan yana Dakin Sakina yana kwance tundazu tashiga bayi ammh yajita shuru tashi yayi tsam ya bita abunda yaganine yasa shi daskasrewa sakina ke tsungunne cikin bath jini yana zuba guda guda Da Sauri Safwan yace"Sakina....Meye haka kuma jini nagani"Kallonsa tayi idanunta sunkawo kwallah tace"Bansani ba Dr bansani ba wlh"Tafada tana bayyanan da Rauninta kallonta yayi kan yace"Tun yaushe kika fara bleeding din"Sanda kai tayi tace"Bansani ba ammh tun haihuwar Safeena ne".....What...Kina haukane Sakina ace kina zubar jini almost 4weeks ammh kika kasa mgana what wrong wit u ne"Yafada ahasale sakina ta fashe da kuka tace"kayi hakuri naji tsorone..."Juyawa yayi yana Fadin"Ki shirya muje asibiti kawai malama"Yafada yana wucewa sulalewa tayi tana zubar kwallah domin ta tsorata daganin yanayin da Dr ya shiga.

Shiko dakin Safeena ya shiga yake Fadamata salati ta saka har inna zulai taji ta fito shine

Safeena take Fadamata ita fadan ta hau Sakina dashi tana cewa"Haba Sakeena wannan ai sakarcine kina ganin halin dakike ciki ammh ki kasa mgana keda kike da likita agida....Haba don Allah karki kara Sakarcin nan"Gyada kai kawai tayi tana hawaye har bakin mota suka rakasu suna daga musu hannu.

Achan hosp.kuwa ba shi kadai ba harda sauran likitochin asibitin suka dukufa kan sakina domin gano meke damunta Safwan tsurama abunda ya bayyana jikin yar"Na'urar datake haskomasa cikin Sakina zuface ta yankomasa siririn gilashinsa ya cire yana share zufa kallon sakina yayi wacce ta zuba mashi ido cikin rashin hayyaci kada kai kawai yayi ya fice shima Tahir binsa yayi da sassarfa Runtse ido Sakina tayi aranta tana ayyana Abubuwa dadama.

commet
And
Share
Vote

*Shakira..*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My mommah Hajja Hadiza muhammed Ba"are*

*38*

Yana shiga Office dinshi Tahir shima ya shiga yana Fadin"Dr Safana wai Sakina wata irin macece...Ace kidinga ma kanki illar ammh kebaki sani ba kina haukar banza

"Yafada yana kallon Safwan dayake kokarin bude karamin fridge din dake kafe a office din ruwan yadauko ya bude ya kafa kai sai daya sha fin rabi kafin ya dire ajiyar zuciya ya sauke kan ya zauna yana cewa"I do'nt know Tahir....Sakina tagama illata kanta tana ganin kamar ni tamawa ko..?Yafada idanunsa sunkawo ruwa Dr Tahir yace"Wlh bakai tamawa ba kanta tama domin awannan stage din da mahaifarta takai masalaha shine fiddata kawai..."Zuru Safwan ya mishi kan yace"A'a Tahir bbu wata dabara da za"ayi sakina fa danta dayane aduniyan nan kuma sai aciremata mahaifa"yafada da jaddadawa Dr Tahir ya gyara tsayuwa yana cewa"Kafini sanin illar cancer mahaifa Dr S S kuma kaganin ma idonka har ta kumbura saboda bayan tasa an mata juyin mahaifa ta cigaba da shan pills cikin rashin akida wannan shiyasa basa zuwa cikin mahaifan sai suka dinga taruwa guri daya suna mata illah shi ya haifarmata da zubar jini mai yawa...Barinshi zuwa wani lokaci Dr zata Fashe ne da kanta kuma in ta fashe am srry to...."Iz ok a shirya mata operation"Dr Safwan ya katsesa cikin rauni kafin yafice daga office din binsa da kallo Tahir yayi kan ya girgiza kai yabi bayansa.

Safwan dakin da Sakina take yakoma tana ganinsa ta mike tana Fadin"Safwan...Meke damuna ne..?Kallonta yayi kai tsaye yace"Abunda kika kullama kanki ne kina ganin nikika mawa to dayake kinsan Allah ba azzalumin bawan sa bane sai abun yakoma kanki"yafada muryansa na rawa cikin rudewa Sakina ta dirko daga gadon datake tana Fadin"Na shiga uku ni Sakina ashe har yanzu bangama kwasan KUSKUREN DANA TAFKA BA"Safwan ya juya baya yana Fadin"Wannan shine kuskuren dazaki Tafka na karshe Sakina domin Yau din za"ayi miki aiki a fidda mahaifarki"Mahaifata....Tafada da karfi kan tasha gaban Dr tana Fadi cikin kuka"Safwan...mahaifata to meyasamu mahaifan Tawa"Shima kallonta yayi kan yace"Bayan kin Haifi Adil kin kara komawa an rufe miki bakin mahaifa ko..?"yafada still idanunsa na kanta sunkuyar dakai tayi tana hawaye tace"eh...Yace kuma bayan nan kin cika gaba da shan pills ko"nan ma tadaga kai wucewa yayi zai fita kana yace"Abunda kika aikata shiya jawo mahaifarki ta kumbura har kikafara zubar jini nan da wani lokaci in aka barta zata fashe ne gabadaya kuma ke zaki rasa ranki...Yadan dakata kafin yace"Kizama cikin shiri karfe biyar za"ayi aiki.Yana gabama fadar haka yafita sulalewa Sakina tayi tana kuka harda kara wani tashin hankali wanda

ba'a samasa suna tashiga kuka take harda majina na nadamar abunda ta aikata domin ayanzu itace ta kashe kanta bawani  ba.

Shiko Safwan kai tsaye gidansu momma ya nufa yaje yafada musu sallallami kawai suketayi Hajiya mama harda kwallanta na tsausayama Sakina nan da nan ta shirya tace ya kai ta Asibitin taje ta zauna da ita domin awannan halin tana bukatar wani kusa da ita Haka Safeena dataji Ibr sai da takusa faduwa imani da tsoron Allah suka shigeta lokaci daya gabadayansu suka dumguma zuwa asibitin koda suka je sun Sami sakina ba yarda take tasha kuka Da Gudu Safeena ta isa ta rumgumeta tana kuka sakina fadi take"Abunda na shukane nake girba Safeena kidaina min kuka ni najama kaina"Hajiya mama da momma ne ke ta bata baki da inna zulai shiyasa tayi shuru duk mai imani yaga Sakina sai ya tsausayamata na halin data ciki,safwan kuwa kasa zama yayi saboda yama rasa wani yanayi yake ciki.

Koda biyar din tayi angama kowani shirye shirye hatta kayan tiyatan asanyamata Dr Safwan da Dr Tahir sai Dr Sainah sune zasuyi aikin suma sun kammallah komai lokacin da'aka gungurota za'a shiga da ita ne ta rike Hannu Safeena tana hawaye tace"Hakika duk wanda yaki godema ni'imar Allah to zai godema akasin haka Safeena koda ban tashi ba banda haufi akanki dama Adil danki ne na har Abada ammh don Allah inaso ko bayan Raina kada kibashi Ibrin mugun halina saboda kada ya tsaneni"Kuka ya kwacemata Adil dinma shima kuka yake duk bai fahimtar meke faruwa ammh yasan cewa bbu lpy.

Safeena tayi saurin sakamata  little Hajiya mama da justice akan jikinta tana kwallah tace"Wlh har Abada sune yayanki Anty nabaki su halas malak...zaki tashi kuma ki renisu da hannuki ni Safeena Uwar Adil ce kadai"Mirmishi da kuka atare suka kama Sakina ta rumgumesu tana Fadin"Da gaske safeena kin bani su 'Tagyada mata kai kawai sai Sakina ta fara dariya tana hawaye tarike hannun safeena kam tana mata godiya kowa awurin saida ya zubar da kwallah tsausayi momma da hajiya suka amshi ya"yan suna Fadin"muma mun yaba da wannan kyauta ya"yan kam na Sakina ne"Dr na gefe baice komai domin shikanshi yana cikin wani yanayi ahaka aka shiga da sakina tana kuka suna kuka.

Shudewar awa hudu kana aka fito da ita lokacin Safeena takoma gida tayo musu abinci koda aka fito da ita kamar matatta aka kaita dakin na mussaman wanda daman don iyalan Dr akayishi Dr Tahir ne yafada masu Hajiya kan su kwantar da Hankalinsu komai ya tafi Normal sunyi hamdala da godiya Ga Allah shikuwa Dr Safwan ko adakin tiyatan bawani abu ya tsinana ba saboda rashin kuzari ace wai yau shine ya jagoranci fidda mahaifan matarsa uwar dansa kai Abun da ciwo wlh.

Sakina Sai washegari ta farfado kuma Alhamdullilah bawata mtsala sai asannan Dr ya kira kwamishina yake Fada masa abunda ke Faruwa aranar kuwa suka iso hajiya kari sai da tayi kuka tana rokon Sakina tayafemata domin harda da ita adorata hanyar datafada to meza"ayi aikin gama ya riga da ya gama komai ya kare Safeena kuwa godiyar tasha babu adadi domin samunta cikin mata sai antona sai washegari Anty laila tazo itama dai Hakurin taita badawa domin itace ummul aba"isin komai.

Sai da Sakina ta shafe Sati kana takoma gida tana cigaba da Shan mgani ya"yanta kuwa in kun gansu gun safeena to nono zata basu suna nan gun Sakina tana lailayansu Tuni inna zulai takoma da sha taran arzikinta daga Safwan da damginsa Allah Sarki Ummi da Abbah sai da suka zo duba Sakina kuma sun yabama diyarsu bisa kyautar yaran data bawa Sakina wacce tazama abun tsausayi,shikanshi Dr yanzu sakina takoma tana bashi tsausayi matuka daman Rayuwar kenan kabi komai Sannu shine daidai.

Satin Sakina uku dadawo wa asibiti Dr yazo musu da wani Ibri mai Dadi wani babban Asibiti dake Portugal sun gayyacesa aiki dasu na tsawon shekara biyar tuni upper tadade ahannunsa kawai shine baiba da dama ba ammh ayanzu da yafada mu momma suka bashi gwarin gwiwan zuwa kam yaji yana sha"awar inyin aiki dasu sunbashi gidan zama da motar hawa unyaje chan kuma lasisin zama agarin na dindin..Sunyi murna kwarai da gaske dasa albarka saidai shizai Fara wucewa tukunnah tunda Safeena na shayarwa itakuma Sakina bata da wani ishashen lpy.

Ranar asabar da misalin karfe biyu na dare jirginsu ya tashi a lagos wanda Dr Tahir yamasa Rakiya sun rabu cike da kewar juna domin tunda suka dawo nageria basu taba rabuwa ba yabarmasa Amanar kula da asibiti har zuwa wani lokaci...yatafi yabar Su momma da matansa

da kewarsa.

*Safe journey Dr S S Safana*

Commet
Vote
Share

*Anitha...*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..!*

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty_💞

*DEDICATED TO:My Mommah Hajja Hadiza muhammed Ba"are*

*Assalamu Alaikum....Kafin naje gaba naji sakonninku masu cewa in ramgwantama Sakina insaka takara haihuwa kuma Dr yadawo yasota...To azahirin gaskiya kuna manta wani abu karka ku f manta Ada Sakina ita kadai ce ke Da Dr taci karanta bbu babbaka baitaba daga ido yakalleta ba cos tanacin darajar mahaifinta tarainasa tarainamasa uwa da kakansa karfa ku manta akaron farkon cikinta agefen mahaifa ya bayyana bayan tasa anrufemata bakin mahaifa sanadin dayaja sai da mahaifinta ya tsawatarmata ammh hakan bai hanata bayan ta haihu takoma asake rufemata....Kada ku manta ada tasamu Dama ammh tayi wasa da damanta dama ita Rayuwa mai dauka da ijiyewa ce,matukar Sakina takara haihuwa kuma mtsayinta ya

zarce na Sakina to tabbas KUSKUREN DATA TAFKA BAI MANA AMFANI BA GABADAYANMU....Haka kaddararta take ba"a Bari akwashe duka koda ka kwashe sai ka bar Wani akasa....Janaf*

*39*

"Alhamdulillah Safwan ya isa kasar portugal lafy asibitin yafara isa yayi report kana ya wuce muhallinsa hakika Safwan yayaba da gurin wani upstair ne mai kyau da tsari ga motarsa range cover baka gabadaya yayaba da tsarin komai gabadayan likitochin turawane da larabawa sai shine kadai bakar fata ya kara tabbatar da cewa Allah na sonshi ne daya zabosa zuwa wannan wurin gashi duk wani cigaba sun daramu komai nasu cikin tsari ne da kwarewa,sai da ya kwana da zuwa kana ya chanza layi yakira gida sunyi murna jin ya isa cikin kwanciyar hankali yayimusu fadan zaman lpy itakuma Sakina yace tacigaba da shan mgani yayi musu alqawarin dakomai ya daidaita zaizo yatafi da daya daga cikinsu bayan ya kira su momma Tahir yakira yakai mai bayanin yadda yasamu komai Normal.

Kwanchi tashi asarar mai Rai gashi Dr na neman cin wata bakwai a portugal kullum yayi waya sai dai ya basu hakuri domin aikin yayi masa yawa gashi bakar fata kuma mai kwazo shiyasa asibitin tabasa mtsayi mai girma kwatakwata bayasamun lokacin kansa wani alokacin agidansa na asibitin yake kwana..Sudai kawai addu"a suke ta mai Sakina ta warke garas abunda taciga da taya Safeena kula da yan biyu wa"inda suka girma sukayi bul dasu akallah suna da wattani goma da haihu dayake suna da karambani har sunfara mikewa itakuma Safeena yanzu hakan Pratical take a asibitin barau dikko dake kaduna itama bata da lokacin sai abun yakoma kan Sakina gashi daman sun shaku da ita duk inda tabi suna biye da ita suna Ammi Ammi,shikuwa Adil an girma don shima Akallah yanzu shekararsa biyar primary 3yake domin yaron kaf kwakwalwar ubansa yabiyo amkranta abun alfahari garesu domin SALISU SAFWAN SAFANA badaga nan ba.

Safwan bai Samu damar dawowa gida ba sai daya hada shekara daga cur kana ya iso gida wata daren jumma'a dare masu daraja aranaku ta Abuja ya sauka Tahir yaje ya taho dashi yana shigowa gidansu ya furta no place like home cikin farinciki momma da hajiya tun safe suke gidan haka ya rumgume momma da hajiya yana murnan ganinsu bai ida mamaki ba sai da yaga yanbiyu suna takawa da kafafunsu rumgumesu yayi yanajin farinciki aransa ga Adil dayakusa kamosa shima yana rumgume dashi yana Fadin i miss u Daddy yace miss u too my son....Zaratan matan nasa kowacce taci gayun kece Raina Safeena tana Sanye da wani

ubansu Fefe laces dinkin riga da sikat kayan sun amsheta ko"ina ya cika das da ita itakuma sakina sanye take dawani material fari da baki mai duwatsu dinkin doguwar riga ne dama tuni shi yasan zabin matan nasa safeena ita tafi son riga da sikat ayayinda Sakina tafi sanya dogayen riguna kowacce tacika tayi dam da ita lokaci daya yaji sha"awar kasancewa da matansa yakamasa dama kodayake chan sakamakon aikin dayayimasa yawa sai dare yake samun hutawa shima daya kwanta sai barci gari na wayewa kuma ba zama shiyasa sai lokaci bayan lokaci kewar nasu ke bijiromai...Atare sukayi dinner dukkansu kafin Tahir ya kwashi su Hajiya ya maidasu da yaran sukayi barci Sakina ta kwashesu takai Dakinta itakuma Safina tadau danta ita takaisa dakinsa dake gefen nata da'aka barmasa shima tashi yayi ya shiga nasa dakin ya fada wanka abun mamaki har ya kammallah wankan nasa yayi sallah ba wacce talekosa shiyasa yana gamawa yayi kwanciyarsa aransa yana so yaga mesuke nufi.

sukuwa matan nasa kowacce ta kullacesa ita safeena tazata dakin Sakina yaje shiyasa tajisa shuru tunda sun saba koda yaushe inkinada girki shi zai biyoki har dakinki sai dai kuma in yan mulkin ne suka motsa duk yadda taso kar abun yamata ciwo sai da yayi mata rabonta da mijinta tunda ta haihu duk da tasan in yaje gun sakina ba laifi bane ammh ko sallama ai yayi mata dataga abun na neman hanata sukuni alwala ta dauro tazo ta hau sallah..Sai wajen uku dawani abu ta kwanta.

Abangararen Sakina na ma haka take domin itama tayi tunanin yana gun Safeenarsa tunda ita yanzu bata dawani amfani abun yamata ciwo wanda sai da tayi kuka saboda bakinciki itama din dai haka takwana cikin jin takaichin Abun da Dr Safwan yayimata.

Yana dawowar sallahr asuba yadau mota yatafi gidansu Hajiya bai dawoba sai wurin takwas na safe koda yadawo ya tarar da Safeena zata kai Adil mkranta ta dawo don yau bazata shiga sch ba,suma koda suka fito suka hadu basu nuna ma juna wani abu ba sungaisa yadda suka saba sakina tahada musu breafast itakuma safeena ta shirya yaran dama haka sukanyi basu ma san baya gidanba sai da yadawo domin kowacce bata kalli ko kofar dakin nasa ba kowacce kishi nacinta shima koda ya shigo Safeena tawani dauke kai Sakina ma datake bama Little hajiya tea tahade rai tayi tagefen ido yake kallonsu aransa yace"Topha...To su wa'innan fa mena musu naga kowacce bata son ganina😂😂

Dakinsa ya wuce aransa yana fadin"lallema yaran nan ni zasuyima iskanci ko"uhmm yakada kai wanka yayo yakoma gado ya kwanta abinshi yayi banza dasu,koda safeena tadawo kai Adil

gidan Hajiya tabiya wai tabar musu gidan suci kansu to itama din sakinar daki ta shige da yaranta tana fadi aranta"Kada ta takuramusu.

Sai after 12 yatashi yasake wanka ya shirya cikin riga da wando na kamfanin armani wandon blue ne haka zalika rigar farace ammh anyi rubutu da blue an sa HANDSOME.
.Kafarsa sanye cikin buddaden takalmi ya fto hannunsa rike da wayarsa da key din motarsa babu kowa afalon shiyasa shima yasa kai yafice ko kallon abunda suka jeramai baiyiba daman ya karya agidan Hajiya asibitinsu ya nufa achan yayi wuninsa zugunr suna tattauna bikin Tahir din wanda za'ayi nan da two weeks.

Koda Safeena tadawo daga ko taba abinci safwan baiyi ba tayi mamaki harsaida ta tambayi Sakina,sakina ta kalleta cikin mamaki tace"ba tare na barku ba ai inaga zaki fini sani aie"Cikin wani yanayi Saferna tace"Bangane tare kika barmu ba Anty ni rabona da Unku tunjiya daya shiga dakinsa"Kai tsaye Sakina tace"Nima hakan take"Suka kalli juna har suna hada baki"ba"a dakinki ya kwana ba"...?

Atare kowacce ta girgiza kai ai sai suka dora hannu akai suna sallallami Sakina tace"Haba no wonder naga yana wani cika ashe ashe"Safeena tace "Mun bani Anty to yanzu yazamuyi"Sakina tayi shuru kan tace"mu rabu dashi yadawo yanzu ko munkirasa bazai dauka ba tashi zakiyi mu hadamai soecial delicious kafin yadawo aikuwa haka sukayi suka zage suka mai sakwara da miyar kan agushi sai ferfesun kan rago suka hadamai kunun aya domin yana so sosai kana kowacce taje daki ta chakare sunhada baki yau shigar wasu riga da sikat sukayi yan kanti cikin tsarabar da ya kawomusu ne kowacce tadaure gashinta da band ko dankwali basu saba yau din kara'i zasu sha.

aikuwa kamar yasani yaki dawowa agidansu Tahir yai zamansa yana hira sai wurin goma ya shigo gidan yara harsungaji da jira sunyi barci abun mamaki sakina da Safeena suna falon zaune sunyi tagumi sunzubama kofa ido yana ganinsu yawani hade rai ko kallonsu baiyi ba yashige daki harda bango kofa jikake bam"kallo juna sukayi kafin sumike gabadaya suka nufa dakin.

Suna sallama aciki ya amsa yana daura tawol zai shiga wanka dukkansu suka nufesa Sakina ta rike tawul din tana daidaita zamansa a kugunsa ita kuma Sakina tajawo hannunsa kiiii"suka nufi tiolet dashi shidai binsu kawai yake aransa yana fadin"waya gaya muku barno gabas take cikin bath suka wuntsilasa kafin sukalli juna sukayi sigina Sakina ta saki shower itakuma Safeena ta warwaremasa tawel din suka fara mai wanka atare suna wani ligwigwitasa kallonsu yayi yace"Ku...Lafiyarku kuwa fyade zakumin ne..?

"Dariya suka sheke dashi harda tafawa sukace atare"Srry...Srrry...Atare daure fuska yayi kan yace"kada wacce tasake tabani ku ficemin daga nan...Yanzu ku kasan dani"Kafin yakara wata mgana suka shige bath din suka turmusheshi suna mai Dariya binsu yake da ido wani nishadi na bin ransa shima turmumusa su yayi sai da yajikasu da ruwan kana ahaka dai suka gama mai wanka agantale bayan angama yace sai an daukesa kallon juna sukayi kan suyi hanyar fita suna fadin"Tab...Wazai iya daukan ka kazama lukuti'yace"ku...mekuka ce"suka fice suna tsintsiramai dariya.

Koda yafto su suka shafamai  mai suka shiryasa suka jasa har dinner abincin ma susuka dinga basa abaki suna tarairayansa shikuwa sai wani basarwa yake ammh aransa fes suna kamallawa ya mike  Ko magana bai musu ba ya nufu hanyar dakinsa suma mikewa sukayi kowacce ta nufi hanyar dakinta basu mai mgana ba sai da Safeena tashiga sai ta leko tace"Unku mu kwana lpy"tana dariya tamaida kofa ta rufe shuru yayi yana ganin shi zasuyi ma wayau kawai sai yanufi kan kujera zai kwanta sai ji yayi sakina tafigesa ta tura dakinta tana mai Dariya kan gado ta turasa kafin ta hayesa tana dukan kirjinsa tana cewa"Sai kadinga wahalar damu ko,"Rike hannunta yayi kafin yace"Ramawa nayi yara..Ni zaku nuna boko"cizansa tayi ahannu shikuma yace sai ya rama daganan kuma wasan yachanza salo...Nidai na fice araina ina Fadin Happy family.

haka rayuwarta  take  tafiya kwana biyu yayi gun sakina yakoma gun Safeena yanzu Safwan dan gatane domin wankama inyaji tsiya sai yace sai sun mai sukuwa su zage su sullesa tas bikin Tahir fa yazo tun ana saura kwana uku Safeena tatafi zurmi zuwanta na farko tun bayan aurenta sakina kuwa sai ana gobe biki ta isa hajiya kuwa da momma suna gidansu Tahir hakika sunsha biki sun gwangwaje sun dauko amarya sunkawota kaduna cikin aminci da soyayyah,...Bayan bikin safwan yayi shirin komawa a adalci da Sakina yayi shirin komawa domin itace uwargida.

Bayan bikin Da sati daya Suka daga zuwa Portugal shida Sakina itakuma Safeena anbarta da yara saboda sch dinsu da nata ita shida kanshi yatsara duk bayan 6,months zai dinga dawowa suna chanji ita da Sakinar.

Commet
And
Share
Vote

*Anitha...*
[10/14, 20:02] Sis Janafty: *NA TAFKA KUSKURE..*!

*Wattpad:Janafnancy13*
_Mallakar:Janafty💞_

*DEDICATED TO:My mommah Hajja Hadiza muhammed Ba"are*

_*Godiya gareku Masoyana wanda na sani da wanda bansani ba...Bahoot Bahoot Shukuriyyah*_

*END*

Bayan Tafiyarsu da wata biyu Safeena tayi rashin Ipy Tahir yace yadubamasa ita illai ana dubata sai ga ciki har na tsawon two month murna gun Dr baida iyaka...To ahaka dai Rayuwar taita gungurawa cikin kwanciyar Hankali Safeena cikinta nakai wata biyar ta ciresu anono tacigaba da kula da kanta ga sch suna shekarar karshene.

Watansu Shida kuwa kana suka nufi gida koda suka zo sun tarar da Safeena da tulelen cikinta agaba yan biyu sun kara girma da wayau Abunsu sati biyu kawai Dr yayi yakoma yaso Tafiya da Safeena ammh Hajiya mama tace"Kaniyarka da cikin zata bika wata uwa duniya tama uban mene nifa bansa zalama in bazaka iya zama kai daya ba to kakoma da Sakinar"Ransa yabaci domin shi da Safeenar yaso komawa tunda kuma akace haka shine yayi komawarsa shikadai.

Sai Da Safeena tahaihu kana yadawo tasamu dan ta Namiji Ranar suna na zagayowa yasa ma yaron sunan kwamishina wato kabir...Hakika kwamishina yaji dadi matuka domin har hakan yakasa boyuwa aransa sai dayazo ya furta da baki da kuma aljihu to baisamu komawa sai da Safeena tayi arba"in dama kuma gashi sun sami hutu kawai sai ya tattarata suka Tafi akabar Sakina da yara.

Safwan da Safeena a Portugal sabuwar rayuwa suka bude ita dashi domin sun dade rabonsu da juna azahirin gaskiya yafi samun Natsuwa in yana tareda safeena sakina kawai arakane ammh shi Namiji ne dayakeson kwatantan Adalci shiyasa ko afuska ba wacce yataba Nunama sai dai a aikace in yana Tareda Safeena kullum cikin desire yake sakamakon Sakina wacce shi ko Sha'awar kasancewa da ita bayayi kawai yana daurewane don kar ta gane ammh sai da tagane to yazatayi tarigaya tasani yanzu qualityta da sauran mata ba daya kawai dai ana rakawa da ita ne.

Suna da wata biyar da tafiya suna ma shirin dawowane aka yomasu waya suzo hajiya mama ba lpy...Cikin tashin hankali yanemanmusu visa ammh bata samu ba sai a washegari da yammh suka taso cikin ikon Allah koda suka iso sun tadda gida cike tun a airport yake tama Tahir tambayan ya jikin hajiyar ammh amsa dayane"Hajiya ciwo yakare"Dagashi har Safeenar jikinsu yayi sanyi.

Da kwamushina yafara cin karo wanda yaxo da tawagarsa ga kuma yan safana yagani dasu kawu bala ana alwala ai jakar hannunsa ya saki yanajin wani jiri na kwasarsa Tahir neya rikesa kwamishina yadafasa yana Fadin"Sai hakuri wanda yafi sonta ya dauketa...Sai muyi fatan Allah yasa tana kyakyawan matsayi"Wasu hawayene masu zafi suka zubomasa safeena kuwa da gudu ta shiga gidan da Sakina tafara cin karo wacce ke gefe sanye da hijabi tana rumgume dasu little hajiya tana zubar kwallah sai momma dake kurya kanta aduke tana digan hawaye Adil ne yazo ya rumguneta yana Fadin"Mami...Hajiya ta tafi naga ansata awani abu"Sulalewa safeena tayi tana kuka iyami dake gefe takalleta itama kukan take tace"Yanzu kuke Tafi ina megidanki Hajiya ta rasu ammh abakinta har ta mutu tana sanya muku albarka"Tana fadar haka kawai dakin aka kara kecewa da kuka domin kan kowa yasan Hajiya ta mutane ce macece mai dattako da sanin yakamata macece wacce indai kazauna da ita wlh sai ka karu.....ALLAHU AKBAR KULLI NAFSIN ZA'IKATUL MAUT.

Dama koda suka iso an hadata badadewa aka isa da hajiya makwancinta na dindin wanda safwan ya durkushe gaban kabarin yana fitar da kwallah Tahir yakamasa suka shiga mota suka koma gida ko mgana bai iya ko gaisuwa aka mai saidai ya jinjina kai cikin gida suka yana yin sallama afalon da suke kuka yakara kecewa kai tsaye momma ya nufa yana zuwa gabanta ya durkusa yace cikin shakakiyar murya"Momma ya mukaji da hakuri..?

"Momma tadago idanunta jawur tace cikin kuka"Hakuri namune gabadaya Safwan Hajiya tatafi ta barmu tabarmu da kewa"Tafada tana fashewa da kuka Safwan ya runtse ido hawaye suka xubomai yace cikin muryan tsausayi"Momma mun sake yin rashi akaro na biyu...Mun rasa jigonmu hakika kekika haifeni ammh dukkan wahalata Hajiya tayisa ta kasance jigoce agareni wacce tazame min makwafin mahaifi wlh tallahi hajiya ce komai na itace ginshikina momma rawar data taka arayuwarmu mai yawa sai dai Muyi mata Fatan ubangiji ya amshi bakuntarta"Yafada yana zama dirshan ya tusa kansa atsakanin kafafunshi yana kuka gabadaya dakin jikin kowa yei sanyi kuka kawai akeyi Tahir dake tsaye shima sharar kwallah yake iyami ne tataso tazo tadagosa tana fadin'Kadaina kuka Safwan yanzu hajiya tafi bukatar addu'an mu akan kukanmu...Ta tafi ga ubangijinta ammh wlh tatafi dakai abakinta tana sa maka albarka da fatan gamawa da duniya lpy sannan ta horeka da kakwatanta adalci atsakanin matanka"Safwan ye wuf ya mike yana tangadi yafice kuka keneman kwacemasa safeena da Sakina suka bi mijinsu da kallon tsausayi domin wannan mutuwar shi aka mawa.

Baki tako ina sun zo hatta da Ummi da mallam Aliyu sunzo gaisuwa tako ina Sai da akayi addu"an bakwai kana aka watse aka bar masu gida da kewa momma sai dai kaga tazauna shuru domin tunda aka aurota bata taba rabuwa da hajiya kona kwana daya ba sai gashi yau mai rabawa ta raba yan"uwa na adamawa sunso tafiya da ita Safwan ya hana ammh yace tabisu tayi kwana biyu ko tasamu saukin damuwa.

Safwan shi kadai yakema kansa shiri domin Nageria tafuta aransa kwata kwata babu hajiya mama babu mahaifinsa momma kadai tarage masa to shikuwa zaman mai zaiyi chukun chukun kai Adil garin manchester ne ya kammallah dama primary 4,yake ammh saboda hazakar sa yasa yazana common...Makrantar aikin sojane suma matan basu sani ba sai da Tafiyar ya rage sati daya kana yake fada musu to yazasuyi tunda mai afkuwa ta afku..Adil dayaji yayi ta murna ammh dayaga Tafiyar ce tabbas sai ya hau kuka Safwan dashi da Tahir suka isa dashi har kasar suka kuma barsa suka dawo ammh safwan yafadamasa ko awani hali yake kar ya manta da KASARSA NAGERIA.

Yagama musu kowani shirye shirye dama yajirane Safeena ta kamallah jarabawansu na

karshene to Alhamdulillah ta kammallah bai fada musu komai ba sai da komai yazama Normal yaje yadauko momma daga gun yan"uwanta anan yake cemata ta musu sallama don  jibi zasu koma Portugal da zama na dindin...Momma ta kallesa zatayi mgana yace"Momma yazanyi banda zabi...Babu hajiya to mai zaki zauna kiyi gani ni danki ina wata uwa duniya...Tafiya zanyi dake momma ayanzu ke kadai nake dashi yanzu"momma tashare hawayenta tana shafa kansa tace"Allah yamaka albarka da zuru"arka gabadaya...hakanan ta musu sallama sunso suyi gaddama ammh kuma duba ga shi dantane bata da wanda yafishi ahaka suka rabu cikin kewa.

Dama tuni yaje Safana yayi musu sallama suka musu Fatan alheri washegari kuwa gabadayansu yasasu amota sai zurmi basu wani jima ba yace suzo su wuce anan yake fadama su Ummi zencen tafiyar Sakina da Safeena suka kalli juna cikin alhini domin tunda akayi rasuwar nan suka kasa gane kan safwan komai nashi ya chanza...Fatan alheri suka musu daganan suka nufa kt suma chan din fatan alheri sukama kwamishina fatan Allah sa yazama alheri domin anyi canji gwannati gwannatinsu takare yanzu kasuwanci yakeyi..Suma din fatan alheri suka musu kawai domin babu tacewa.

Sakina da Safeena kowacce kayan sawanta kawai yace su dauka...awhegari karfe goma ta musu abuja ta chan zasu tashi Tahir ne da mami mahaifiyarsa da Matarsa Aisha wacce keda tsohon ciki suka musu Rakiya harsai da jirginsu ya tashi zuwa sama safeena da Sakina sai da hawaye ya xuraro musu domin kasa kasace....Yabar amanar asibitinsa da komai ahannu Tahir yace zasu dunga zuwa lokaci bayan lokaci shikanshi tahir yaji kewa sosai na rabuwa da Amininsa to yazaiyi Kwatakwata safwan yaji Nageria ta fitar mai aka.

*****

*Bayan shekaru biyar..*

Wani saurayi ne dan kimanin shekara sha biyu ya fito daga wani daki da gudu yana bin wata yarinya yar shekara shida da gudu Safeena ce zaune afalo tana sanye da wani gilas jaridace ahannunta tana karantawa kallo daya zakamata kagane girma tareda natsuwa sunkara shigarta ayanzu haka babbar Nurse ce a asibitin da Safwan yake aiki. Fadawa jikinta tayi tana Fadin"Mami..Kinga ya Adil ko"Tsaki taja ta tureta tana Fadin"Ke dagani Sa"anki ne"Tafara tura baki tafashe da kuka Sakina ta fito daga kichen tana cewa"To sarkin cin zali mai kuma tamaka"Yace"Ammi cewa fa tayi badani za'a Nageria ba"Harara ta zabgamai kan tayi mgana Dr Safwan yayi sallma ya shigo hannunsa sabe da wata karamar yarinya ga wasu biyu suna binsa

abaya duka matane dauke da lodoji justice dake kan kujera zaune ya mike yana tsallen murna ankawo ice cream Dr Safwan dayazama babban mutum wanda hutu da naira tagama ratsasa ya zauna yana fadin"Waya tabanin Hajiyata"Sakina tace"Babban banza...Safwan ya kalli Adil dake cika yana batsewa yace"Kai...Meke damunkane baka da wayau ko bakasan kannenka bako...?

Safeena tace"Haba Daddy yazaka hau mai Fada ai sune suke jansa ko"Safwan yace"Ke kuma uwarsa baki son laifin danki...To kidinga mai fada nan fa bariki bane ato"Gabadaya suka kece da dariya tashi tayi ta kama hannunsa tana Fadin"Mutafi daki my son...Duk munsan zaman dazamuyi dasu tunda ba"a sonmu"kansa ya aza kan kafadarta yana cewa,"I love u mamina..." tace tana shafa kansa"me too my son...Suka wuce daki Safwan yabisu da kallo yanzu wazaice ba Safeena ta i ta haifesa ba sai wanda yasani...Shikanshi yasani ammh kuma ko afusaka baya nuna ma Sakina ce uwarsa.,suna zuwa nageria lokaci bayan lokaci don Safwan bai manta da Gida ba.

Sakina ta matso ta amshi little keena wacce Safeena ta haifamata takwara tana dagata sai ga Tahir shima ya Matso ta hadasu ta daukesu ai sai kowa ya taso Ammi nima Ammi nima Haka ta hada ta daukesu dukkansu Hajiya justice,kabir,tahir,da keena masha Allahu da zarar safeena ta yaye zata mikama Sakina itace maman yara momma ce tafito daga wani daki takara manyanta ammh jin dadi yasa ba"a ganewa tana fadin"Don kaniyarku kashe ta zakuyi rai biyar "Tashi sukayi da gudu suna fadin"ehhhh...Momma nine first suna fadi suka fada mata suna shirin kadata Safwan yace"Kai karfa ku karyamin uwa"momma tayi dariya hakoran makkanta suka bayyana tace"kyalesu safwan Rai ne yakai barsu suyi" Sakina tayi dariya tace"Hakane mommanmu Allah dai yakara miki lpy safwan ya amsa da Amin yana kallonta tabbas sakina bata kara haihuwa ba ammh ya"yan Safeena kadai sun koremata kishirruwan ya"ya tana kara godema Allah akoda yaushe daya bata ikon gane TA TAFKA KUSKURE....Safwan dake binsu da kallo ya furta A hankali"ALHAMDULILLAH!

Toni ma Anan zance ALHAMDULILLAH....

*Nan nakawo karshen Ibrin NA TAFKA KUSKURE Abunda nafada dai dai Allah yabani ladansa kuskuren dake ciki Allah ka yafemin,Godiya ta mussamman ga  grouops din dasuka bini tundaga farkon Ibrin har zuwa karshe,Ina godiya ga Duka Masoyana na Wsop da Wattpad masu Sharhin da Voting ina godiya Sosai Allah bar zumunci Ameen*

Domin samar damar kasancewa Daya daga cikin wadanda zasu karu da Littafinmu na Silar Hallaci wanda muke kan Rubutashi Nida Sister Aisha Alto zaki iya biyan kudin karatu akan ₦300 kachal,Domin karin bayani zaku iya nemata ta wannan Layin 09069067488

*Akwai sabbin Littafaina da zasu Fito ammh sai mun Shiga Sabuwar Shekarar 2021 in Allah yasa muna da Rabon gani Daya zai kasance Free daya kuma na Biyan kudin karatu ne bana mallaka ba Zasu zo da Sabon salo wanda zai Nishadantar da masu karatu ina Fatan Bazaku bani kunya ba zaku nuna min cewa Ana tare*

Comments
Share
Vote
Share

*Shakira..*
*Anitha..*
*Paro..*
*Janafty*